□ MIKIYA □

{Mai hangen nesa □}

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

HAJIYA idan har kinsan ba karatun littafin MIKIYA ne ya kawo kiba pls kada kiyi joining ma, kinga basai kinba kanki wahala Nima kin bani ba, so be careful, domin bazan lamunci zama da shara ba□□

Ɗan ɗano□□ daga alƙalamin AMMEY LAYLERH □

Page 1&2

BY*

AMMEY LAYLERH ✍♥

✯ *~□ OFFICIAL MIRRAH □~*

THE WRITER'S OF

* KAREN BANA*

JALAAL AREEF

KƬAUNA BIYU

And Now MIKIYA

KIDNAPPER'S

Informants

DEEP

BEST LOVE

BlackMoney

By terrorism

Treason

Strong love

Right

Women's travel

The Secret Society

Oppression

Corruption

SADAUKARWA

Rayuwa da ƙaddara a tare suke tafiya tamkar yan uwan juna sukee, rayuwa take tafe take da tarin ƙalubale a cikin ta,ko wanne mai numfashi yana tsoron MUTUWA.

Wannan ba labarin ƙarfafa gwiwa bane,kuma ba labarine na al' ajabi ba, wannan kawai labarine na wata iriyar ƙaddara. Na Tsara wannan labarin ne da tunanin zan kawo gyara wa al' umm. Saboda zan bada labari na # KARFAFA GWIWA, JARUMTA, HAƊARI da kuma AL' AJABI EHHH tabbas Al'AJABI.

Kunsan akan waye?

AK, EAGLE. Wanda akema laƙabi da

*THE MAN WHO CANNOT DIE😱 {Mutumin da baya mutuwa}

Shin UBAN DABANE SHI? Ko kuma ƊAN DABA,? Ko kuma BABAN MASHEƘA!?.

Tabbas duk wanda ka gani yau to yabiyo ta jiya. Haka zalika duk wanda ka gani a matakin nasara, to kuwa tabbas acikin nasarar nashi akwai tarin ƙalubalen daya fuskanta kafin haka, SADAUKARWA

Labarine daya shafi ko wanne ɓangare na zalumci cin amana hassada baƙin ciki munafurci ƙunci duk wani nau'in saɓon Allah da abubuwan da suke faruwa da rayuwar mu a zahiri suna tattare acikin Wannan littafin na mikiya, wanda yake ƙunshe da manyan sakwannin da nake son isar wa ga al'umma harma da kasarmu nigeria

□□□

_____

LAGOS

Victoria island

A tsare a kuma jere ƙerarrun motocin suka gama daidaita parking na car's nasu Cikin wani haɗaɗɗen mention me girman gaske, wanda kallo ɗaya zaka ɗauka a ƙasar turai kake,, domin baƙi ɗaya komi dake cikin gidan na glass da glass ne.

Cikin zafin nama jibga jibgan guards ɗin suka shiga dirowa daga cikin manyan motocin hannuwansu riƙe da manyan bindigu da bakaken kaya zaka dauka basamudaye ne. Cikin tafiyar sassarfa suka soma kutsa kansu cikin ainihin haɗaɗɗen mention ɗin. A natse suka ƙarasa shiga cikin rantsatstsen parlourn daya amsa sunan parlour, wanda yake kewaye da wasu fitunannun ƙayatattun Cautions masu azabar ƙyau da tsari farare tass dasu, ga shi an ƙawata parlourn da wasu irin roll designer's masu azabar haɗuwa, Sai wasu manyan zanen emojis da aka manna a bangon gabas da kuma yamma, komi na parlourn dai so need.

Wani irin ƙamewa naga wannan samudawan sunyi tare da rusunar da kansu kasa, hakan yasa nayi saurin duban inda suke tsayen.

Da wani Wani bazaraten matashin saurayi naci karo wanda kai tsaye na gaza fuskantar ainihin waye, iyaka kwantaccen gashin dake kwance saman qeyarsa kawai nake iya hanga, wanda yayi parking na lallausan sumar ƙasan ƙeyarsa, in banda walwali da ɗaukar idanu babu abinda sumar take aikin yi, ga wani irin fitinannen qamshin da take fitarwa.

Yana sanye cikin wasu haɗaɗɗaun buttoned shoulder strip wool sweater na Paco Rabanne, Coffee and white color sai sweater daya ɗaura saman kayan, kansa sanye cikin p-carp blue black sai facemask dake saman kyakkyawarn fuskarshin, da ya mai wani irin kyau banabwasaba, a takaice dai babu ta inda na iya Gano wannan bawan Allahn

wani irin azababben ƙamshi yakeyi tamkar Companyn tularen duka ne a jikinsa. Ƙafafuwansa sanye cikin designer sneakers ruwan toka ƙirar Dior, daga yanayin yadda yake zaune zama irin na sarauta na fashimci Dogo ne da tsayinsa zai kai kamu ɗaya da ɗigo tara ma'unin meter (1.9m) kusan a ido za ka ƙiyasta tsayinsa da wannan shahararren ɗan film ɗin ƙasar Indian wato PRABHAS.

Tamkar ma bai san anyi ruwansu a wurin ba wanda ni anawa tunanin nama ɗauka bai gansu bane, domin kuwa typing nashi yake a system ɗin dake gabansa mai ƙirar apple da sauri da sauri yatsunshi kaman wani machine, Idanunshi nakan system ɗin har loƙacin kuma bai ɗago yakalli waɗan nan masu kama da samudawan ba.

"Sit"

Ya furta a dakile iyaka saman laɓɓansa.

A nutse suka zazzauna fuskar nan haɗe tamkar tayi aman wuta tsabar haɗen da dake, daga haka bai ƙara ko kallar inda suke ba yaci gaba da sarrafa system nashi.

saidai aka kusan kwashe sama da ten minutes kafin ɗaya daga cikin guards ɗin ya furta

”BOSS wannan ba abun ɗaga hankali ba ne. Har yanzu akwai sauran loƙaci dan haka zamu cigaba da saka musu ido kafin loƙacin ya cika!”

Cikin rashin son ya magantu saida yaja wasu sakonni kafin cikin deep sound nashi ya furta

" They are all going to taste my wrath Arielle!” cike kuma da fusata ya karasa faɗar maganar,

wani kalan gajeren tsaki yaja har loƙacin bai buɗe idanunshi dake lumshe ba, kaman wanda magana kema wahala

Kafin ya zuba baki ɗaya guards ɗin blue eyes nashi tare da folding hannunsa saman ƙirji kamar mai nazarin wani abu.

Luuuuuu yaja kyawawan idanunsa ta cikin sun glasses in daya toshe nake iya hango su, fuskarn system ɗin dake gabansa ya juya musu, sosae razani ya bayyana saman fuskokinsu, amma kuma dake cikakkun maza ne yasa sammm basu girgiza ba, cikin wata kalan murya dake nan ada ƙile irin muryan nan na no nonsense person ba wasa kokuma fara'a yace.

"I want to see him in front of me in 24 hours"

Fuskansa har wani bala'i kake iya hangowa domin ƙirjinsa har wani dagawa yake.

"Yes Sir."

Suka haɗe baki tare da sara masa suna barin parlourn baki ɗaya sai mutum ɗaya daya saura, "Sir there is something you need"

*NO!"

Ya furta a ɗakile tare da janyo plask na Black tea nashi zuwa gabansa a ɗan madaidaicin bowl ɗin dake gabansa ya tsiyanya wanda yake ta fidda turirin zafi ga kuma wani daddaɗan ƙamshin dake tashi na kayan haɗin shayi, duk uban turirin da yake amma shi ko a jikinsa haka ya shiga sipping abunsa hankali ƙawance.

1:40am ya tashi yana nufar upstairs nashi tsararre haɗaɗɗen benen ya shiga takawa bibbiyu, zuwa loƙacin gidan ya ɗauka wani irin shiru, babu motsin komai sai ƙamshin flower's ɗin dake ratsa ko ina na gidan, kasancewar mention ɗin kewaye yake da tarin shukoki na flower's color daban daban, kuma ginin gidan na saman ruwa ne sai wata iriyar sassanyarn iskar dake ratsa ko ina irin ta farkon damunar Nan. Siiiiiiii siiiiiiii siiiiiiii haka sautin iska ke fita.

Few minutes sai gashi ya fito cikin wasu blue black suit inda ya toshe ko ina jikinsa babu abinda kake iya kallo dade da hannuwansa suna rufe cikin sos na hannu, sawayensa na cikin covershoe dake kyalli na tomford hannunshi daure da wani rantsatstsen wristwatch,

Cikin takun isa se kace wani sarki yake taku, ko wanne lungo da sako na gidan na sanƙame da manyan escort wanda suka fi kama da samudawa, duk inda ya gitta sai sun Sara masa, amma ko kezau ba yayi kai tsaye ya nufi ƙaton parking space na gidan, wanda suke ɗauke da rantsatstsun narkakkun manyan motoci,wanda a ƙalla zasu iya kaiwa ki manin guda ashirin zuwa da biyar haka, gefe guda kuma ɓangaren

mashi nane babu colourn da babu, gaban wani lifan ya tsaya wanda yafi kama da haɗa shi akayi taka nass don baiyi color da sauran lifan ɗin da nasa ba gani ba. Cikin wani irin salo ya haye saman lipon ɗin yana bashi wuta, dake already dama bodyguards ɗin sun san ya saba fitan dare irin haka yasa sammm basuyi mamaki ba.

Kuma idan zaiyi fitan dare sammm baya fita da kowa shi kaɗan sa yake fita abunsa, haka ya shiga tsala gudu a saman titin wanda hasken sololi suka haske titin tamkar rana, Gaban wani babban club ya Park na lipon nashi kallo ɗaya zaka ma club ɗin tun daga waje kasan cewa Yes na wanda suka isane, idan kashigo cikin club ɗin kuwa kai karan kanka kasan bana wasan yara bane ko daga yadda aka zuba uban security.

Kai tsaye diro daga saman lipon ɗin tare da kutsa kansa cikin club ɗin, matane gasu nan reras wasu na rawa nashan love wasu kuwa ko motsin su ba'a iya ji, sai dai kaji sautin growing nasu na tashi wa'iya zubilla ya Allah 😭 kaci gaba da tsarkake zukan mu ya Allah.

Vibrating ring doorbell sound ɗin da wayan shi ya soma ne ya sanya shi dakatawa daga shirin shiga ɗaki me NO 0023 da zai yi, a tsayen da yake ya fiddo da tsadaddiyar wayarsa Samsung Galaxy S2000 rear end yana duba wayan da yaji faɗiwar saƙo yashigo masa yana dubawa, yana tafiya zuwa entrance din shiga ɗakin, wani lafiyayyen security door ne awajen da kana gani kasan wannan ba anyhow ur common club bane domin komai na club ɗin abin a kallane, yana ganin saƙon ya meda wayar cikin aljihun wandon, kai tsaye kuma ya tura ɗakin. babu zata babu tsammani ƙaton mutumin dake up&dwn kan wata koɗaɗɗaɗiyar badurya ya zabura, domin dama a tsoran yake. Laluben wandon sa ya shiga don suturce jikinsa, cikin zafin zuciyar daya motsa masa ya rumtse idonsa tare da harbin gaban mutu min, wanda tsabar rikiɗar da yayi ne ya sanya sam bai san zuwan mutumin gaban sa. Wata razananniyar ƙarar azaba ya saki yana rufa duka hannuwansa biyu a gabansa, cikin azabar kururuwaya ya shiga faɗin.

” I got out of the case, will my strength come back to me, or I will die! AK what happens What is wrong with me in life that you want to see my back, Woooooo wiiiiiiii huhhhhhhh ahhhhhh Pain, pain, pain”

Haka ya shiga hargitsa kalamansa wanda Ni ban fashimci ko manganun waye ba. Wanda naji an ƙira da AK kuwa ba tare daya tsaya sauraran kururuwan wannan dattijon fa ya juya yana barin ɗakin rai bace. ɗaki mai 117 ya kuma nufa. Shiru alamun babu wata rai mai Numfashi a wurin duk inda ya gitta sai kaga manyan security na sara masa, haka ya ratsa har petal na dakin. Wani irin gurnani na ringa

jiyowa irin na ceton ran, kafin naji an sheƙe da wata uwar mahaukaciyar dariya, cikin sautu me amo kunnuwana suka fara jiwo min wasu kalamai

"Ke a tunaninki har kin wani alhakin da kika isa tona min asiri Kina ƙarƙashin ikona REEYAH, akwai dubin ki kafin ke amma sun buga dani sun barni, domin ni AUDU BASHASHA ban fito ba Saida na shirya, ayau zaki sheƙe reeyah bayan na wulaƙanta rayuwarki na yagalgala ta" da ƙarfin masifa ya shiga fincikar kayan dake jikinta, da iyaka ƙarfin da ya saura a jikin ta, tayo kaki ta tofa samar baƙar fuskarsa, cikin muryarn da taci kuka harta gode Allah ta ce.

"Wawa! Jaki, dabba, daƙiƙi, wai kai a tunaninka kama ni! Kayi? to ka sani wannan karon ma shine ya kama ka, shine ya ɗana maka tarko kuma dole yayi wining wasan"

A ɗan razane ya dube ta kafin fusata ya ce, "reeyah sau nawa wai ake haifo shi?! shi wanene menene abinda yake taƙama dashi. Dariya mai tafe da hawaye ta saki loƙaci guda, sai kuma ta shiga nuna shi da yatsarta manuniya tana faɗin.

"Wai ka tsorata ne, ka sani sau dubu billions dollers ake haifo irin sa, kuma shi ne wanda baya mutuwa, EAGLE"

Ratsatsa haka sautin kararn fashewar glasses in daya ma dakin ƙawanya ya bada loƙacin da wannan mutumin me ɓoye fuskarsa ya faso ɗakin, a razane a kuma kiɗeme mutumin daya ƙira kansa da AUDU BASHASHA yaja baya yana zare jajayen idonsa irin na mugyaye. P-carp ɗin dake samarn kansa ya zare a take wata kyakkyawanr fuska ta bayyana wacce kallo ɗaya zaka masa ka san wannan ba daga ƙasarmu ya fito ba, kunnen ɗaya na gefen hagu na manne da wani gold ring bari ma daya huja. gun ɗin dake maƙyale a bayan wandon jikinsa ya ciro yana fasa kan wannan mutumin a take ko shurawa bai yiba, ko inda budurwarn nan take bai kalla ba ya sanya kansa yana ficewa a ɗakin, bayan ya ɗebe duka wayoyin mutumin duka biyun, yana bi ta wani door na daban ba wanda ya shigo ba.

A hankali yake saƙƙowa daga saman benen hannuwansa zube cikin aljihun wandon sa, yana tafiyar nan nasahi tamkar wani King

Yana sanye da wasu haɗaɗɗun riga da wando na trouser, yayinda fuskar nan ke sakaye cikin sun glasses ya sanya hular jacket ɗin dake saman kayan jikinsa, sannan ya sanya face mask. gentle yaci gaba da saƙƙowa zuwa downstairs, jikin sa na fidda wani irin fitinannen ƙamshin perfumes nasa mai kwantar da hankalin mai shaƙa

A ƙasaitance ya kai zaune zama irin na sarauta saman Royal caution ɗin dake jere a parlourn, binsa da ido wannan samudawan suka ci gaba dayi har sanda ya fara sarrafa system nashi.

Cikin kwanciyar hankali yake danna laptop nasa ga sanyin A/cn na ratsa ko ina na parlourn, duk yadda suke faɗin "Boss good morning, Boss good morning!" Amma ko saurararsu bai yi ba.

Ba tun yau suke anya kuwa AK cikakken mutum ne kamar kowa, daba da murɗaɗɗen mutun ne shi wanda baka taɓa gane gaban sa bare bayan sa, kullun cikin gindayar da mutane yake, sai ka rasa ina ya dosa kwata kwata, shin wacce iriyar zuciyace gare shi Sammm baya tsoron mutuwa, A yayin da sojoji suke tsaka da musayar wuta zaka yadda kowanne soja ne sanye da bulletproof, domin kare harsashi daga shiga jikin su. Amma banda AK, yayin da kowa ke gudun mutuwa to shi tunkararta yake shi yasa ake masa laƙabi da mutumin da baya mutuwa.

_____★★★

Nigerian army headquarters Lagos

Tun daga farkon shiga headquarters ɗin zaka fashimci ba lafiya, domin ta ko ina ta ko wanne saƙo da longo kewaye suke da manyan sojoji masu jini a jiki.

A babban ɗakin taron dake cikin headquarters ɗin, duk wani army dake da babban matsayi ne kewaye a cikin ƙaton ɗakin, suna Zazzaune saman kujerun da kowanne ke pacing dan uwansa, a matuƙar fusace mr. President ya doka saman table ɗin dake gabansa, cike da ƙonar da zuciyarsa ke masa da kuma takaicin wannan abu ya dago jajayen rinannun idanunsa yana zuba su saman duka soldier's ɗin dake zaune cikin Office ɗin.

"What are you doing and you are giving your feet to this militant boy, he is taking use dahar ya samu zarrar da zai riƙa mana dauki ɗai ɗai, ya zama dole a wannan karon mu kawo ƙarshensa"

Yayi maganar ne tare da duban duka soldier's ɗin dake fuskantar sa, cikin dakakkiyar sautin sa ya kalli ɗaya daga cikin soldier's ɗin yana furta.

”Ajmaal har yanzu kana kan bakar ka na kama EAGLE?”

"Yes sir."

Wanda aka ƙira da Ajmaal ɗin ya faɗa tare da sara ma mr. President ɗin.

Ɗaya daga cikin soldier's ɗin ne ya kuma miƙewa Saida yayi solid na mr. President ɗin kana cikin bauɗaɗɗar murya ya shiga magana kamar haka.

”Har yanxu ina mamaki sir.mutumin daya bamu horo sannan kuma ya kashe ɣan ta'addar da babu adadi!, me Ze sa ya zama ɗan ta'addar?”

Wani kafirin murmushi mr president ɗin ya saki tare da tsare wannan soldier's ɗin da firgitattun idanunsa, cikin dakakken sauti ya furta.

”Har yanxu kana son eagle kenàn?"

"Kwarai sir amma ba kamar yadda nake son ƙasata”

Cikin tsare shi da ido mr. President ya furta ”Idan har kai ka samo shi zaka iya harbinsa?”

Saida ya kuma solid na president ɗin kana cikin Amon murya furta

"Kwarai sir zan iya!, amma idan na tabbatar bashi da laifi, nayi ma wannan alƙawarin sir.”

Cike da jin zafin Ajmaal ya mike cikin fusata ya fuskanci wannan soldier's ɗin.

"Jaheed kodai kana tare da AK ne, in banda haka ta ya kake tununin cewa Eagle bashi da laifi?”

Shima wanda aka kira da jaheed ɗin ya juwo yana sake fuskantar Ajmaal ɗin, kafin cikin yaƙi ni yace.

”Idan baka son mutum zai iya siyar da borkono kuce ba zafi, haka zalika zai zai wuce ta cikin ruwa kuce ya tada kura, mutum kan gwada zafin wuta ne sau ɗaya a rayuwa, wannan sojan shi da kansa yake ta famar fafutukar shiga wutar, taya kuke tunanin mutum mai tsananin gaskiya da kuma sadaukar da rayuwarsa domin ƙasar da kuma aiki da zuciya kamar ABDULMALEEK KUWAIT AK zai iya zama ɗan

ta'addar? kamar yadda kuke ƙiransa da shi, dole Akwai dalili ko nace dalilan da suka sa ya zare kansa daga cikinmu”

Ba shi Ajmaal ɗin daya qA@@ maganar ba shi kansa mr. President ɗin yasha jinin jikinsa, wani irin shiru ƙatoton office ɗin ya ɗauka, kowa da abinda yake sakawa acikin zuciyarsa, wani irin shiru ƙaton office ɗin ya ɗauka na kusan second 40.kafin Ajmaal ya magantu "ko tantatama bayana yi kana ɗaya daga cikin ƙashin bayansa"

Ya buɗe baki da shirin sake yin magana keñan mr president ya Wani irin doka table a take komai da yake kai ya tarwatse komai yayi nashi wuri fuuuuu ya fice a office ɗin a fusace, ganin haka ya sa duka soldier's ɗin suma suka mimmiƙe suna barin office ɗin, wani irin kill smile Ajmaal ya saki loƙacin da yake dab da fita.

ISAH MANU EMPIRE

Wani katafaren ƙerarre haɗaɗɗen luzary ne iyaka ganinka gini ne Irin na manyan ƙusoshin kasar,wanda suka ci suka sha kai harma suka tada kai, baki ɗaya ginin gidan ya kasance na glass da glasses ne. Duk kuwa irin girman da gidan yake da, amma kewaye yake da uban wasu jibga jigban soldier's.

Kai tsaye katafaren parlourn gidan na kutsa kaina,da wani farin dattijo na fara cin karo wanda keta faman safa da marwa. Hannuwansa goye a gadon bayansa wanda a ƙalla zai iya kaiwa shekaru 80 ko irin da biyar ɗin wani irin sintiri yake famar yi, wanda kallo ɗaya zaka mashi ka kai tsaye ka gane cewar tabbas baya a cikin hayyacin sane, da ƙarfin masifa ya dunkule hannunsa tare da kaima iska naushi.

"Why is everyone afraid of him? Wanene shi yaushe ma aka haife shi dahar zai sanya ni gudun tseran tsira"

Yayi maganar Cikin zallar ɓacin rai da kuma jin ƙona daga cikin tsaƙiyar ƙirginsa.

Da sauri ɗaya daga cikin samudawan mutanen dake zagaye a ɗakin suka haɗa baki wajen furta.

"Ko wa ye izini kawai zaka bamu!, mu kawo maka kansa BOSS"

Idanuwansa da suke rine sosea ya ɗago tare da zuba musu jajayen idanunsa da suka ƙanƙance. Numfashi ya fesar me zafi kamar bazai magana ba, sai kuma ya magantu, Cikin wani irin dakakken sauti ya furta.

"EAGLE, MIKIYA Shi nake da buƙata!"

A razane A ƙiɗime hankali tashe suka ja baya namomin jikinsa na rawa, suka shiga bin boss in nasu da kallon You are smart 😁😱

Hhhhhhhhhh to ai shikenan 😂 A gimtse 🙃♥

*BY AMMEY LAYLERH ✍ *

*MIKIYA *

{Mai hangen nesa }

~We want an end to oppression~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

NA MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

⭐ *~ OFFICIAL MIRRAH ~*

□□□

★★★Sosai yasha barci mai lafiya a safiyar ta yau kasancewar a daren jiya ya jima bai kwanta ba. domin bayan ya dawo daga fitar daren da yayi sosea yayi aiki a cikin laptop nashi,wanda ya raba dare yana yi. Sallar asuba ma daƙyar ya fita masjid dake cikin anguwar yayo Ahankali ya soma buɗe lumsassun Idanunsa da har yanxu suke cike da barci, santala santalan fararen sawayensa ya fara zubowa kan tattausan carpet ɗin dake gabansa. A nutse kuma ya miƙe yana nufar haɗaɗɗen bathroom nashi, shower ya sakamar kansa sosai ruwan ya dake shi, kana ya tara ruwa masu ɗumi da daɗin ƙamshi a cikin bathtub,Wanda gefe da bathtub ɗin akwai drawers masu yawa da wata full sized jaccuzi da kuma site din wata striated rectangular glass shower tana wani fidda wani irin ƙyalli, kamar ba'a taɓa amfani da shi ba shima gefen sa da akwai fixtures masu ɗaukar hankali sosai. Yaja tsahon loƙaci a bayin kafin ya fito sanye da bathrobe chocolate Colo mai azabar taushin tsiya

dan har wani wani maski-maski take yi tsabar taushi da kuma laushinta,da mini towel ɗin dake a hannunsa ya shiga tsane jiƙaƙƙiyar tulin sumar dake kansa mai tsaho, Fuskar nan a tsuƙe Samm babu alamun rahama a cikinta.

Gaban ƙaton mirror'nsa ya nufa cikin tafiyar jin kai da kuma isa.

Hand dryer dake saman mirror ɗin sabuwa fil ya ɗauka ya jona a socket, ya shiga busar da himilin sumarsa da tafi kama data yan India, lotion ɗin dake jere saman mirror'n ya shiga shafa wa jikinsa sama sama. Saida ya mulke jikinsa da spray's nashi masu azabar ƙamshi da tsada, kafin ya nufi gaban wardrobe nashi data kusan cinye bango guda.

Tsabbb yayi shirinsa cikin wasu haɗaɗɗaun track suit baƙaƙe, sai glass ɗin daya sakaye idanunsa a ciki tare da facemask yar gadon, phone's nashi kaɗai ya diba yana nufar main Parlour, cikin takun cikakkun mazan dake ji da kansu. Kafin ya fito tuni su milse sun gama shirya komai daya dace, jin takun tafiyarsa da baya taɓa ɓuyane ya sanya su risinar da kansu ƙasa, cikin girmamawa suka haɗe baki wajen furta

"Good morning Boss!"

Saida yaja wasu luƙuta kafin ya amsa "kuna lafiya" iyaka saman laɓbansa.

"So boring Boss"

Wannan karon kammm da ka kawai ya amsa su, yana zama kan ɗaya daga cikin ƙayatattun kujerun dake kewaye da dinin Area ɗin,

A ƙasaitance yaja wata haɗaɗɗiyar kwalba wine Wanda naga ansa with alcohol, zubawa yayi a glass cup ya farasha, bai wani shada yawa ba, yaja plantain chips ya fara cakuta kaɗan yaɗan taɓa ya tashi tare da wine ɗin ya koma kan caution ɗin parlourn ya kafa bakinsa ya fara sha inda saida Ya shanye Kafin ya ajiye bottle ɗin. Laptop ya janyo tare da buɗe mukullan sirrin ya shiga sarrafa abarsa cikin kwarewa.

A rikice a kuma ɗimauce Rooney ya faɗo ɗakin cikin tashin hankali ya nufi ogan nasu kai tsaye, system ɗin dake hannunsa ya dire gaban uban gidan nasu.

A tare miles axton lani da kuma Vincent suka ja baya suna toshe bakunansu, hankali tashe suka juyo baki ɗaya da nufin Boss ya kalla laptop ɗin, amma ga mamakinsu abinda suka kalla ɗin ya tada musu hankali shine Boss ɗin nasu yake kalla hankali kwance tamkar babu abinda ke damunsa ko kuma ya girgiza shi. A baɗini kuwa wata iriyar tsuma namomin jikinsa suka ɗauka.bai motsa da ga zaman da yay a lallausar kujerar ba ƙafa ɗaya kan ɗaya. Yayinda bayansa ke kishin kiɗe jikin kujerar kansa a sama kaɗan, Yanda yay biris ɗin sai ka ɗauka baima fahimtci kamai dangane da hakan ba, Yaja kusan 10 mint kafin yaja wani irin huci ya furzar yana mai buɗe rinannun idanunsa da suka sake wani irin garai-garai ai nahin suffarsu ta idanun mage na sake bayyana a fili.

Zaune ya tashi da ƙyau sai dai a nutsensa yake Samm babu alamun firgicewa a tare dashi,Sudai baki ɗaya sun gaza samun Nutsuwa sai kai da koma suke famar yi a cikin parlourn, suna a cikin wannan alhinin ne kuma get man na gidan ya faɗo parlourn against.

"Boss da akwai matsala"

Wani irin rumtse idanunsa yayi a duniya kalma mafi muni daya tsani ji itace kalmar yaji an ambaci matsala, ya tsani jin kalmar andaɗe da fice wannan babin, don haka ya kalli get man ɗin tare da ɗunkule hannunsa tamkar wanda zai kai naushi, sai kuma ya kaima iska naushin, yana fesar da wani zazzafan Numfashi, loƙaci kaɗan kamanninsa suka sanja jikinsa ya shiga rawa kana ganinsa zaka san he is not on his mood,musamman yadda yanayin jikinsa ya sanja tare da wani irin tsuma.

Cigarettes ɗin dake jere gabansa ya ɗauka a zuciye da sauri Vincent yazo gaban sa tare da kunna masa lighter ya fara zuƙarta a haukace, cikin ƙankanin loƙaci ya har gitsa parlourn da hayaƙin cigarette.

Saida zuƙe wajen kara biyar kafin yaji zuciyarsa ta ɗan risina, cikin hosky voice nashi ya furta

"A tura saƙon kai tsaye!, Vincent maza a nemo mana biza daga nan zuwa yamma"

"An gama Boss"

Suma suka haɗe baki wajen faɗar hakan suna fita daga parlourn baki ɗaynsu, Shima da ƙyar ya iya miƙewa da ga parlourn ya nufi bedroom ɗinsa.

Zaune yakai saman lafiyayyan gadonsa

Yanda ya zauna shiru ya dafe kansa zaka ɗauka ciwo yake masa ne. Amma sam ba haka bane Abubuwane kawai suke masa kai-komo a rai da suka wayi gari dasu.

Ba yau ne ya fara cin karo da matsaloli da ƙalubalen rayuwa ba, domin zai iya cewa kusan a haka ya rayu, Amma na yau ɗin sai yafi ƙona zuciyar sa fiye da koda yaushe,dan duk sunzo masa a bazata ne. Hakan na nufin ya sakankance da yawa kenan Sannan dole ne ya sake shiri in har yana buƙatar abubuwa su tafi masa a yanda yake buƙata anan batare da tangarɗa ba.

Goran ruwan dake a Centre table ɗin ya ɗauka. Batare da yabi takan kofin dake kusa da ita ba ya ɓalle murfin kawai yakai bakinsa ya fara kwankwaɗa, Sai da ya shanyesa tas sannan yayi cilli da bottle ɗin. Sake furzar da huci mai zafi yayi a karo na ba adadi yana sake nutsar da kansa. Sosai abubuwa masu yawan gaske suka shiga ƙoƙarin zeroying Brain nashi.

Tamkar kuma wanda aka zabura ya miƙe aɗan zafafe yana yin gaban ƙofan Glass ɗin dake a shafe da Pics manya na emeji me hoton lion, babbar yatsar hannunsa ya sanya a take wurin dake a shafe yayi On tamprint na yatsunsa, zuuuuuuu wata haɗaɗɗiyar ultra door ta baiyana. Wasu manyan Computers ne A ɗakin dasu jojjone ta ko wacce kusurwa dake ɓangaren, akan wani ƙayatacce dogon table saikuma macbook akan wani dogon lumtsatsen kujera, Zama cikin hanzari tare da ɗaukar MacBook ɗin dake kan kujerar, buɗewa yayi yafara aiki cikin ƙwarewarsa da kuma baiwar iya sarrafa ko wanne abu, yakai kusan 40min yana danne danne, wata iriyar ajiyar zuciya ya sauƙe kafin ya tashi yana barin ɗakin da yafi kama dana bincike.

Yana fitowa daga wannan ɗakin ya ciro iphone XR ɗin sa, NO na Vincent yayi dialing NO In, cikin ƙanƙanin loƙaci daga ɗaya ɓangaren ya cira wayar yana faɗin

"Boss"

"Get ready to go out operations!"

Da wannan ƙasaitar nashi yayi maganar yana zare farar Morocco ta mazan dake jikinsa, cikin sauri sauri ya shirya kansa cikin straight leg trim trouser sai black Versace greco hoodie, ƙafafunsa sanye cikin wasu haɗaɗɗaun black hermes cover

shoe, sai hannunshi sanye cikin wasu haɗaɗɗun safan hannu, ga kuma facemask ɗin dake saman fuskarsa dake saye cikin sun glasses ɓaki wuliƙ dashi.

Yana fitowa coumpaund ɗin tuni wannan samudawan sukayi shiri na musamman sun ɗane cikin rantsatstun baƙaƙen motocin su. Suna ganinsa suka hau fito da shewa suna faɗin "BOSS! BOSS!! BOSS!!!" Cikin wani irin salo da ƙwarewa Miles ya yayi tsalle ya diro yana shirin buɗewa Boss In nasu car, hannunsa dake a rufe ruff ya ɗaga masa yana mashi nuni da power bike ride ɗin da zai hau, sara masa yayi yana komawa cikin motar, shi kuma cikin wani irin taku ya nufi power bike ɗin tare da daura hannunsa akan key na machine ɗin, wani irin tsalle yayi cikin salon daya zam ɗabi'arsa ya haye saman machine ɗin, tare da masa key wani irin kuka yayi machine ɗin ya ɗauka. Kasancewar shine a gaba ya sake daidaita machine ɗin Cikin sallon ƙasaitarsa ya ɗaga hannunsa sama ƙaramin yatsansa ya fara musu wata alamar dasu kaɗai suka san ma'anar kayansu. Suna gama fashimtar haka

yaja machine ɗin da wani irin azababben gudu ya fita a gidan baki ɗaya, suuuuuu motocin suma suka rufa masa baya Sosai motocin ke sheƙ uban gudu a titi tamkar suna a jerin gasar tsere, bakajin komai sai ƙara ƙainarsu,

Da yawan sauran motocin dake a kan titin sauƙa suke gefen hanya domin basu fili, ganin yadda suke zuga uban gudu na tashin hankali, dan duk mai hankalin da yaga wannan gudun yasan bana lafiya bane ba. Kai tsaye Lekki suka nufa daidai wani mahaukacin ƙaton luzary suka kutsa kansu, tuni jami'an tsaron gidan suka soma sakar musu wata.

Wani irin sakin kan machine ɗin yayi tare da Ciro wasu bindigogi guda biyu kirar berreta M9, tsalle ɗaya yayi ya diro akan power bike ɗin ya fara tafiya kamar irin fusataccen zakin nan,

Saida yayi pulling trigger Kafin cikin wani ƙayatacce salo ya soma harba bindigar.

A gigice Governor Ibrahim Khaleel Nasara dake zaune irishe irishe acikin mahaukacin parlourn sa yayi wani tsalle kamar mage ya haye saman lumtsememiyar kujerar jikinsa na kerma, minister Zubairu tanbuwal kuwa rasa ma yadda zai yi yayi sai kawai yayi knell down a tsakar parlourn.

Acen coumpaund na gidan kuwa Sosae jami'an tsaron suke neman gagararsu su, tuni AK ya fusata kafin kace mene saiga wannan kattin jami'an a ƙasa shi kaɗai ya kutsa kansa cikin ƙaton parlourn, duk wani lungu da saƙo dazai shige saiya haɗu da jami'ai haka yake harbesu. Harse daya danganta kansa da rantsatstsen parlourn minister'n. Fuskarnan yawa kunu haka ya tisa ƙewarsu su duka biyun. Bayan na jakin da suka sha.

Tuni suka bama wurin iska suna barin cikin anguwar, suna barin unguwar manyan sojoji da jami'an tsaro harsun ƙaraso, hakan yasa suma jami'an tsaron a fusace suka mara musu baya, nan fa aka shiga fafatawa tsakanin yan ta'addar da kuma jami'an

tsaro, suna dab dacim musu suka suka saki hayaƙi tuni wurin ya gauraye dama titin baki ɗaya suka harba motocin su tamkar walƙiya haka suka ɓacema jami'an Nan.

Cikin wani mugun jin haushi Ajmaal ya taka birki tare da jan wani mugun tsaƙi tare da cije saman laɓbansa.

Rai ɓace suma sauran jami'an tsaron ke yarfar da hannaye, kowa yanajin takaici da ƙunar rai cikin zuciyarsa.

"AK!"

Wani zazzafan numfashi ajmaal yaja tare da komawa cikin motarsa yana yin reverse, a 370 yaja motar tamkar wanda zai tashi sama.

ZAMANI TV

"MEERAH! MEERAH!! MEERAH!!!"

Sunan da suke ta famar ƙira kenan tare da juyi da matashiyar budurwar a tsaƙiyarsu. Ita kuwa wannan matashiyar da suke ƙira da MEERAH, murmushi kawai take saki baƙar doguwar riga ce a jikinta wadda ta yane kanta da baƙin mayafin doguwar rigar sosae tayi wani irin fitinannen ƙyau cikin shigar.

"MEERAH ABDULLAHI GWANI!, ana son ganin ki a sashen MD"

Aka faɗa daga cenñnn ɗan nesa dasu.

Ahanzarce wannan matashiyar budurwar da zatayi irin shekaru sha taran nan, ta juyo tare da nufar office ɗin MD ɗin harda yar sassarfarta.

Da sallama ta shiga cikin fuska kaɗan kadaran kada han, bakinsa ya baje ba ki ɗaya yana amsa sallamar nata,

"Stay here"

Ya faɗi cikin ɗan saurin bakin da yake da, zama tayi bayan ta gaida shi, amsata yayi sauri sauri kafin kai tsaye ya shiga rattaɓo mata bayanai. "Amm MEERAH aduk faɗin wannan tasha tamu kusan zan iya bugar kirgi wajen faɗin kece haskenmu, kana Nasarar mu, ɗaukakarmu, yanxu nake samun labarai daga majiya me ƙarbi kan cewa yanzu yanxu wannan babban criminal ɗin ya ƙwamishe gwamna da kuma

ministan gida!, SO shine nake son ki haskaka ki faɗaɗa ki ninki maganganun ta yacce wannan tasha tamu zata ƙarayin popular fiye da da, duba da cewa duk wani abu daya danganci wannan babban me laifin son shi mutane suke kamar hauka. Tuntuni nake son samun ɗan firit news akansa ko yayane, saidai sammm babu wata hanya to yanxu ga dama ta samu mezai hana a yanxu kafin wasu gidan jaridun labarain suje musu ke ki fara fitarwa daga wannan tasha tamu ta ZAMANI TV!"

(Ɗan azabar son kuɗi dason suna)

Ta faɗa a cikin ranta

Jin tayi shiru ne yasan MD dan takar teburin dake gabanta cikin marairaice murya yace.

"Wannan labari zai jawo hankalin Mutane zuwa wannan tashar tamu uwa uba yanda kowa ke ƙage dason jin sabon News daga AK EAGLE babban ɗan ta'addar da duk duniya sunansa ya kewa ye ko ina"

"Pls MD naji!, naji!! Naji!!!"

Suna kawai kalaman data furta cikin ƙosawa dajin harmutsatsan zancen MD ɗin.

A take aka tattaro duk wasu ƙananun ma'aikata dama manya, cikin 5 mints kowa ya gama halarta a inda ake gudanar da shirin a ɗaki na musamman. Dama tuni Md ya bata doguwar takardar da duk wasu maganganun suka ƙunsa.

Murya ta gyara bayan ta maƙala headphone tare da sanya ɣar ƙaramar loudspeaker a bakin ta, Cikin zaƙin Muryarta sautin maganarta ya fara fita kamar haka cikin amsa kuwwa.

"_Assalamu alaikum masoya barkanmu da kasancewa damu ayau safiyar juma'a, wacce akema laƙabi da juma'atu babbar rana , karku manta kuna tare da tauraruwar tasharku mai farin Jini wato ZAMANI TV!, Wanda muke tafe muku da zazzafan labari akan wannan babban criminal ɗin nan wato EAGLE, wannan Ni! MEERAH ABDULLAHI GWANI Ni ce jagoranci shirin.

A yau safiyar juma'a mun tashi ne da alhinin labarin ƙwamishe governor da kuma ministan gida, da wannan tantirin ɗan ƙunar ƃakar waker ɗan. Ta'adda wato AK EAGLE yayi wanda ahar kullum tazara kaɗan ce tsakanin sa da jami'an tsaro.

Bayan karkashe masu tsaron gidan gwamnatin, shin ku a tunaninku miye wannan criminal ɗin yake nufi ne?, yana nufin yafi ƙarfin jami'ainmu kenan, domin dai kunsa tatsuniyar gizo bata wuce ƙoƙi YA FECE kamar yadda ya saba dai, kamar kwanaki da labaransa suka game media kan ta'adda cin ɗaya shiga cikin babban hotel ɗin yayi fashin sa ya fice salin alin. Masha yi, maci amanar ƙasa ɗan ta'adda, We want an end to oppression. Musaso a kawo ƙarshen zalunci, cin amana, ya

kamata jami'anmu su farka daga nannauyar barcin daya ɗaukesu kodan sharen fa gen da wannan babban criminal ɗin ya soma ɗauki ɗai ɗai a cikin al'umma, donjin ra'ayoyin ku zaku iya na ƙara faɗa We want an end to oppression

tuntuɓarmu akan wannan number 081---------- ko kuma shafin mu na Instagram, Facebook, dadai sauran tasho shinmu a gimtse "

Tana kammala shirin ta miƙe jiki a mace tare da barin ɗakin baki ɗaya, Tafi su su majeedah dasu Sairah ɗauka da shewa shi kuwa me girma MD sai faman washe baƙinsa yake domin dai yasan wannan karon zasu shahara,

Daga cikin garin Lagos kuwa harda ma ƙetare a take mutane daban daban suka shiga turo saƙonnin jinjina da ƙara buɗaɗama jami'ai hanya, na suna tare da su 100 percent.

Kamar yadda al'umma suka saurari wannan labaran na yau haka ma babbar headquarters ta Lagos ta saurara, Cikin ƙanƙan da da ido mr.presiden ya ɗago kansa tare da duban Ajmaal, ƙasss masa da ido, nan suka suka shiga tattauanawa akan wannan batu me girma, cikin ƙankanin loƙaci kuwa duk inda ka gaza labarin KIDNAPPING ɗin ake, saiga ZAMANI TV a sama tana shawagi.

A gimtse

To ai shikenan kooooo !?

Sai na ce sai mun haɗe a next page kanan. Laaaaaa na manta shegun sunyi bannet numbern WhatsApp nawa nefa

Shi yasa kuka jini ɗiffffff taku ce *AMMEY LAYLERH ✍*

* MIKIYA *

{Mai hangen nesa }

~We want an end to oppression~

https://chat.whatsapp.com/DGIo9iiSjlgJPPqFHNtddH

_____

NA MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

☆ *~ OFFICIAL MIRRAH ~*

Page 5&6

□□□

" Ita yarinyar da tai labaran lallai ina son sanin wacece ita"

Ya faɗa cikin dakakken sauti tare da ɗaukar kwalbar Win yana kafata a baki, bai dire kwalbar ba Saida ya shanye tasss.

"Sunanta MARYAM ABDULLAHI GWANI wacce akafi saninta da MEERAH, haifaffiyar garin nan ce suna zaune a unguwar GATAN KOWA. Mahaifinta malami ne sananne wanda daƙyar ya bar yabar yarinyar ta fara aiki da gidan jaridar, acewar aure shine kaɗai rufin asirin dukk wata mace ta gari, Md ɗin ne yaje har gida ya roƙi alfarmar malam Abdullahi don ganin loƙacin da suka je pratical cikin tashar, bayan sun gabatar da pratical ɗinne yarinyar ta ringa samun viaw na jama'a, hakan ya haukata Md, shine dalilin da yasa yaje har wurin mahaifinta neman alfarma ta fara aiki da tashar, nashi kona ɗan loƙaci ne.yana da mata uku tayi karatun ta tun daga kan primary nata har zuwa high school ɗinta ji duka anan cikin garin Lagos, ta fara aiki da gidan jaridar zamani tv watanni shida da suka wuce, tana da tsayayyen saurayin ta wanda za'a yi bikin su nan ba da jimawa, tun ranar da rahotannin ya fita na bibiyi ita kanta yarinyar, don nasan dole zaka buƙaci sanin wacece ita, yanxu haka md ɗin yana ƙoƙarin buga jaridu akan hakan, umarnin ka kaɗai muke jira wajen daƙile faruwar hakan, A yadda nayi kyakkyawarn bincike game da Md ɗin

yana da masifar son kuɗin masifa, shi ba ruwansa da inganci abu burinsa kawai kuɗi ɗaukaka sune kaɗai yaren daya fi fashimta"

Axton ne duka me wannan maganar kuma tun a ranar da rahotannin suka fita yabibiyeta, harya samu cikakken tarihin ta.

Saida ya kuma zuƙar cigarettes ɗin dake hannunsa, kafin ya ɗago rikitattun idonsa ya zuba su akan axton, shi yasa ahar kullum yake kuma alfahari dashi acikin yaran nasa, duk abinda ya kamata kafin yace shi kuma ya aikata.

Miles ne ya kuma daidai ta nutsuwar sa cikin gurɓatacciyar hausar sa da baya fita ya furta.

"Boss ni kuma bayan na bibiyi rahotannin ta na shiga duka kafofin sadarwarta, kamar yadda ta umarta tabbas tauraronta na haskawa a wannan tashar dama duniya baki ɗaya, duba da yadda take da tarin masoya tako ta ina hakan yasa cikin ƙanƙanin loƙaci wannan ruhotannin ya baza garin Lagos harma da ƙetare, a yadda ma na samu cikakken bayani daga cikin headquarters na A F S, aka bama shi MD ɗin bayanin dukkan abinda ya faru a safiyar juma'ar, kana Saida suka yi duba da yanda tauraron yarinyar yake haskawa kana sukayi amfani da hakan don son cika burinsu, zasuna amfani da ita ne kawai don.....

Ɗaga masa hannun da Boss In nasu yayi ne ya sanya shi dakatawa, wani irin killet murmushin gefen baki ya saki tare da faɗin.

"A barta taci gaba da buga wasan da dukkan alama zai yi armashi, zai kuma kawo nishaɗi, Nazari muke da ƙwaƙwalwa karku manta!, Sadaukai ne mu tamkar mafarauta!, ba'a taɓa nasarar yaƙi sai in da mayaƙa, don haka ina son a buga wannan game ɗin tare dani"

Wani mugun waro idanu sukayi suna bin boss in nasu da kallo

Lallai Boss rigimarka yawa gare ta da ɗaukar abu me muhimmanci da rashin muhimmanci.

Kai komai da zuciyarka ta raya maka sai kace ayi baka tuna abinda zai iya zuwa ya dawo,in banda taryan Aradu da ka taya ma zakace a bari a buga jaridu akan ka, kana kace a barsu kana son buga wasa akan mutanen dake farautar rayuwarka. Sune kalaman da da axton ya shiga nanatasu cikin zuciyar.

Tsammm ya miƙe cikin tafiyar nan na ƙasaita da kuma izzar da yake da yabar main Parlourn tare da nufar upstairs nashi, yana barin su da wasuwasai falll zuciyarsu.

Shi kuma Boss In saman sa ya nufa zaune yakai gefen bed nashi tare, da janyo system nashi me ƙirar campanyn apple, engine machine ɗin sa ya jona tare da jan glass cup yana siyanyar coffee tare da fara dan sipping nashi a Ahankali, kana ya shiga wasu yan sarrafe sarrafe kafin ya janye ta tare da ɗaukar wani ɗan kit box,, buɗeta yayi a take wata ƙaramar waya ta bayyana irin nokia ɗin nan ta da.

A take ya shiga loda Numbern daya gama haddace abarsa ya lodata tare da shiga ɓangaren messages, ya koma yana ajje wasu short mess tare da switch na wayar yana jefata cikin wannan kid box ɗin.

Zamani tv

Jikin MD har mazari yake wajen amsa saƙonnin dake ta famar shigo musu, tun a daren shekaranjiya da da suka bayyana rahotannin babban criminal ɗin, kamar daga sama kuma yaga wani ɗan short mess ya faɗa masa, cikin rawar takashi ya shiga cikin message ɗin,

_ Amatsayina na babban masoyin wannan tasha ina so ayi fira dani da misalin 11:15Am na safiyar gobe tare da

MEERAH ABDULLAHI GWANI_

"Yesss!"

MD ya faɗa da masifar ƙarfin daya sanya sauran ma'aikatan dake dab da Ofishin sa fitowa, dama abinda yake fata da kuma buri kenan ayi ta jan maganar wannan AK ɗin, gashi Alkhairuka suna ta samunsa a sanadiyar iyaka yaɗa labaran sa kawai. Loƙaci ɗaya tashar sa ta kara zama shahararriya kuma yasan duk ata sanadiyyar MEERAH ne.

"Kai wannan ya kin zama Alkhairi na iyayenki sun iya farar haihuwar yar baiwa!"

Haka dai Md yaci gaba da zabga surutunsa kafin yasa a ƙira masa mera ɗin.

Zaune take gaban me girma Md wanda ya shiga koɗa ta da mata kirari kala daban daban, kafin ya shiga sanar mata da buƙatarsa na wannan bawan Allahn da yake son yin fira da ita.

nooding kanta kawai ta yi tare da zuba masa ido tana binshi da wani irin kallo wanda kai tsaye zamu iya ƙiransa da najin haushi. Ganin ba haƙura zai yi bane ya sanya ta miƙewa dare da barin office ɗin, kai tsaye coumpaund na gidan jaridar ta nufa tare da barin gidan baki ɗaya. tana fita kuwa taci Sa'a ta haɗu da me napen,

shigewa kawai tayi shi kuma yaja kanta ta kife saman cinyarta, tsananin ciwon kan da take ji na ƙara tsananta, "Hajiya ina muka nufa?" Ɗan adedeta sahun ya tambaye ta.

"Daɗin kowa" ta bashi amsa ba tare da ta ɗago kanta ba, babu wata tafiya me zurfi sai gasu har sun ƙaraso, handbag ɗinta ta buɗe bayan ta fita tare da zaro dari biyar ta bashi, canjin ɗari da hamsin ya bata tace ya barshi tana faɗawa cikin gidan nasu.

_____★★★_____

Cikin wasu haɗaɗɗun riga da wando na campanyn Dior saddle Brook yafito brown se ɗaukar ido yake baƙaramun amsar jikinsa kayan suka yi ba, abinka da cikakken namiji me jini a jika da ɗan sassarfa yake saƙƙowa daga stair ɗin, Zazzaune ya samu su axton suna yar firan su , ganin sakkowa Boss In nasu ne ya sanya suka miƙe zumbur tare da rusunar da kansu.

Kai tsaye motocinsu suka nufa suna mata key dake dama already sun riga da sun san da fitar.

katafaren unguwar Banana Island suka nufa wadda take nan da manya manyan ƙerarrun gine gine na zamani

duk inda ka kalla zaka so kara kallar wurin, tamkar ba'a nigeriyarmu ba, ko ina ka ɗaga idanu ka kallah sai ka ji baka son kawar da kanka daga wannan wajen, tsaruwa iya tsurwa, haɗuwa iya haɗuwa kammm anguwar ta gama haɗuwa.

Tun da motocin suka hau saman titin babu abinda kakeji sai suuuuuu suuuuuu suuuuuu shine kaɗai sautin dake tashi, har suka nufi wani ƙayatacce fitaccen gini na alfarma, da remote suka yi amfani wurin buɗe ƙaton jibgegen get ɗin. Kai tsaye suka danna hancin motocin nasu zuwa cikin gidan a jere, nan suka ci gaba da tafiya a jere a saman kwaltar, a ƙalla dai Saida suka wuce wajen get huɗu kamin su isa gaban wani ƙaton parking space ɗin da ya gaji da haɗuwa, wasu shegun tsadaddun motoci ne maƙare a parking space ɗin, tamkar companyn kera motoci , kowani mota ka ɗaga idanu ka kallah sai ka sake kallah saboda tsabar tsananin kyau da tsadar motar, kallo ɗaya zaka ma dogon ginin da yafi kama da masarrafin kera motoci.

A jere waje guda motocin nasu suka yi parking, ɗaya daga cikin manyan samudawan sane ya fito tare da buɗe masa ƙofar motar, cikin zallar izza ya fito yana ƙara gyara zaman p-carp ɗin dake saman kansa, wanda lallausar sumar

kansa ta fito ta ƙasar ƙeyarsa. Ya Ilahi wannan gida kacokam ɗinsa saidai mu ƙirashi da aljannar duniya, ga wasu haɗaɗɗun beneye wajen hawa ashirin da wani abu.

Su dukka daga nan suka dakata shi kuma ya soma tafiya cikin tsananin zallar iya sarrafa tafiya, wata rantsatstsiyar ƙofa ya dosa tare da seta ƙofar da ƙwayar tsaƙiyar idanunsa, wanda suke nan exctly irin na mage a take kofar ta buɗe sai gashi cikin wani irin azababben narkakkun parlour, wanda ya linka na gidansa dake Victoria island sau goma a haɗuwa da tsaruwa.

Baki ɗaya parlourn ɗauke yake da wasu uban lumtsuma lumtsuman kujeru wajen set huɗu, ga ta ko ina na parlourn kewaye da na'u'rorin sarrafa abubuwa, gaban wata kerarriyar ƙofar glass ya nufa, bayan ya shiga cikin lifter ɗin ya danna Black B Parlour 3 zuuuuuuu lifter ɗin tayi ƙasa dashi idanunsa Lumshe a haka har ta kawo shi parlourn, still wasu kofofin da suka kusa kwance min kai na kuma cin karo dasu, nan ya ringa ratsa parlouna yana wucewa har ya isa gaban wani ɗaki da yafi kama dana masu bada horo.

Nan ma Saida yayi amfani da ƙwayar idonsa kafin kofar ta buɗe ya sanya ƙansa cikin ɗakin, tare da ɗan yin baya da blue jacket ɗin dake saman shigar sa, mutane biyun dake a galabaice ne suka yi saurin dago kansu domin tun da aka kawo su wurin ko sau ɗaya babu wani mahalukin da suka kuma gani.

Gashi yau wajen kwanaki shidda ake magana, komai na amfan da aka tana jar musu ga ɗan madaidaicin stoor nan a cikin dakin wanda abubuwan da suka shafi rayuwa aka tanajar a cikin sa irin su kayan girki ne, maƙulashe ne kayan tea ne, chocolate cake recipe with milk duka dai abubuwa ne da akayi tanajinsu dama, farar kujera yaja irin da yan ɗaurin auren nan yana zama akai tare da fuskantar su.

A take suka sha jinin jikinsu sai suka ji duk wani hope na ƙwarin gwiwar dake garesu ya gudu nashi wuri,

Cikin haɗiye miyan wahalta governor Aminu Bello ya dubi AK tare da faɗin.

"Mine hurumin ka na sacemu?,

Wani irin ɗan jujjuya kyawawan ƙwayar idonsa yayi tare da furta.

"Kar kayi magana a loƙacin da babu abin faɗa, koda da abin fadanma kasani shuru bai taba zama illaba, rayuwar duniya kamar series film take, episode episode take zuwa amma duk yawan film ɗin dole ne ya ƙare wata rana"

Ministan gida ne ya ɗan zunguri Aminu Bello, tare da fara kifkifta masa ido ga jikinsa dake tsuma

Shi kuwa cikin aro wata jarumtar ya kuma furta. "Yaro A wasu loƙutan kana ganin kayi nasara shine faɗuwa, haka ma wasu loƙutan ka yadda ka faɗi shine nasara"

"Ka sani sawa a rai ne yasa falke baya jin wahalar tafiya,wanda idonsa basa gani sunanshi makaho, Ammah cikakken makaho shine wanda zuciyarsa bata gani kamar dai ku ɗin nan"

"Ita fa Duniya kamar jirgin ruwa take,

Zata iya kaika inda kake so, kuma zata iya kaika inda take so. don haka be careful respect your mouse ba lallai a wannan karon ta kaika inda kake so ɗin ba"

"Bani da loƙacin ɓatawa loƙaci loƙacinsa,don ba zamane ya kawo niba, a cikin mutanen ku duk mutumin da ya kuskure ya kuma yarda ya haɗa hanyar sa da nawa, saidai uwarsa ta haifi wani badai shiba rayuwata rayuwa tace, haka za rayuwarku rayuwar kuce, kowa ya rufe idanuwansa akan mahaukacin zakin daya fito domin yin farauta, ya kuma toshe kunnuwansa daga hargaginsa"

Sosae suka sake rikicewa ba kuma su sake rikicewar ba Saida ya danna wani ɗan abu mai kama da elevator kyawawan kwalaben wine suka bayyana tare da dasu cocaine cigarettes. Wannan cocaine ɗin ya ɗauka tare da walwale ledar yana matso da ita dab da hancinsa, wani irin kyawawan shaƙa ya mata tare da Ciro kwalin cigarette yana zarar guɗa daya lighter ya ɗauka a cikin abun kana ya karsta ya mata zuƙa ɗaya tare da faso musu hayaƙi Sigarin, zuƙa biyu ya mata ya gama da ita kai da ganin yadda yake zuƙar cigarettes kasan ehhhhhhhhh lalle wannan ubanta ne.

A take yanayin idanunsa suka jirkice zuwa wasu colourn daban, wannan blue In tuni ya kau yana dawo wa jaaaa sosae ga kuma ƙwayar idon ta tayi wani irin fari tasssss tamkar wanda aka ɗura madara a cikin su. Haka ya tashi yana tafiya irin ta wanda ya bugu har yaje bakin kofar sai kuma ya waiwayosu cikin muryarn maye ya furta.

"Duk lalacewan kura a dawa to tabbas tafi ƙarfin kare, haka duk lalacewan mafaraucin zaki yafi karfin alade"

Zuuuuuuu kofar ta koma bayan ya gama fita , directly ya hau lifter ta komar dashi har zuwa asalin wannan narkakken parlourn.

Cikin mayen daya fara ɗibarsa ya nufi kofar yana fita bayan ya loda mata security. Suna ganin yanayin her boss ln nasu suka tabbatar ba'a cikin hayyacin sa yake ba, axton ne yayi saurin buɗe masa murfin motar, shiga yayi suka ja motocin nasu a guje tare barin anguwar baki ɗaya.

Wayar sane ya hau vibrating ring a fusge ya shi ƙoƙarin zaro wayar, *first love* sunan daya bayyana kenan saman screen In wayar, manna wayar yayi a kunnensa bayan yayi picking call ɗin,

"My Boy!"

Shine sautin daya fita cikin wata irin kamalalliyar murya me sanyi, a take yaji jikinsa yaji ya yi wani irin sanyi rauninsa na ƙoƙarin bayyana.

Shirun da taji yamata ne yasanyata ta furta *"William"*

gaban sa ne yaji yayi mummunr faɗuwa jin sunan data ƙira shi dashi. yanzun ma shirun yamata dama tasan abunda zai faru kenan ɗin, dama tasan hakan ce zata kasance duk loƙacin da zata ƙira shi da wannan sunan na William bakin sa yana masa nauyin ne wajen amsata.

Da dai taga alamun bazai amsa tan ba ya sanya ta furta "ABDOUL-MALEEK KUWAIT! har yanzu kana nan kan bakarnka na ƙim amincewa na dawowarka gida?, rayuwar da ka zaɓarma kankayanxun William.

takai ƙarshen maganar cikin yanayin

Sanyin murya da kuma raunin da muryar ta samu, domin maganar harya fara fita da sautin rawa rawa na rarrabe wa.

A hankali yaji jikin sa na ƙara yin sanyi sanyi, ita kuma cikin muryarn dake dab da fara zubar hawaye taci gaba da faɗin. "Kasan irin mikin dake cikin zuciyarmu kuwa William?, kasan irin tsananin ciwon dake galabaitar damu aduk loƙacin da duniya zata haskaka a matsayin criminal kuwa?, do on hey ta yes'ka'rev'nvu ka dawo ƙasarka me yanci, Onoyin na nan na maraba da dawowarka tare da sauran yan uwanka, harda ma jesra, twin yafi kowa missing naka. MOH tana buƙatar ganin ka William.....

Sammmm bazai juri waɗannan maganganun ba hakan yasa hannunsa har rawa yake wajen datse qiran, wayar ya tsura ma lumsasaun Idanunsa tamkar mahaifiyar tasa ce agaban sa,Ajiyar zuciya ya sauƙe mai nauyi,yana ƙara lumshe birkitattun idanunsa.

yana jin yadda namomin jikinsa suka ɗauka rawa, daga cenñnn ƙasar zuciyarsa kuwa wani irin mugun zugun masifa yake ji. Kife kansa yayi da tafin hannunsa yana cusa kansa tsaƙiyar cibiyoyin sa.

Daga nan bai kuma koda ɗagowa bane har Saida yaji an buɗe masa ƙofar motar, alamun sun iso keñan.

Kai tsaye yana fita wajen sink ya nufa alwula ya ɗaura domin anata ƙiraye ƙirayen sallar magrib ne, hakan yasa suma sauran yaran nufar gaban tarin sink ɗin dake

jere reras suka shiga ɗaura alwular suna take masa baya wurin bautama mahaliccinsu.

Sune ne basu dawo gidan ba sai wajajen ƙarfe taran dare, a parlourn suka dakata suka fara shirya dining ɗin domin suna buƙatar suyi ɗinner.

A nutsen sa ya shiga saƙƙowa zuwa loƙacin 9:35 ne, ahankali ya doshi kan dinning ɗin nasu yana baza wannan mayataccen ƙamshin nasa cikin shigar short trouser fari da kuma vest blue wadda takara haska farar fatarsa,yau kammm ko yˑar p-carp ɗin babu saman kan nasa, hakan shi ya bama lallausar baƙar sumarsa bayyanu wacce aka yima wani irin kwalliyar dada, gefe da gefen kuma an kitse shi sai tayi shilim a tsakiyar kan sa tare da sakkowa har ƙeyarsa, wani irin shining take yi na tsabar kyau da makudan kuɗaɗen da ake narka mata.

zama yayi yana ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya, tare da buɗe wani kyakkyawan food plask lafiyayyan tuwon semo ne da jar miyan dage dage domin shine abu mafi sauƙi daga cikin jerin abinciccikan boss ln nasu, kuma dama best favorite food nasa kenàn, idan kana son ka birgisa to ka masa tuwon semo.

Duk da baya a yanayi me daɗi hakan bai hana fuskarsa nuna jin daɗin saba.

Barka da dare suka masa kafin axton ya matso ya fara saving nashi, tuwon semon ya zuba mishi , ya ɗora masa A gabansa tare da sanya masa spoon a ciki,

karamin cup na glass yaja yana tsiyan ya masa win with alcoholic a ciki, A hankali ya fara feeding kansa, ya danci da dama kafin ya ture plate ɗin, wannan glass cup ɗin ya ɗauka tare da fara sipping nashi tamkar wani King. Tsammm ya miƙe yana komawa saman sopa tare da jan shisha ya shiga zuƙar ta yana fesar da hayaki.

Suma Abincinsu suke ci hankali kwance, suna kammala cin farar shinkafa da jar miyar suka miƙe tare da zagaye boss ln nasu. tamkar wanda zasu hana zarar ransa idan loƙacinsa yayi.

Wayar sa ya ɗauka kawai yawuce warsa bedroom, cikin tafiyar ƙasaita wadda sarauta tagama ratsa jinin jikinsa. Yau kam babu aikin babu aikin daya tsaya yi kai tsaye kwanciyar sa yayi bayan yayi adda'oin barcinsa kamar kullum.

♥□□

MEERAH

Kamar kullum gidan na nan kamar kasuwa, duk uban sallamar data rinka yi amma babu wanda yayi ƙoƙarin amsata, itafa har mamakin gidan su take yadda abubuwa suke tafiyar musu tamkar irin gidan jahilan nan, kanta kawai ta sanye xuwa barandar da mahaifiyarta take zaune tana aikin zuzzuba humra cikin kwalabe.

Zaune takai dab da mahaifiyar nata tana faɗin "AMMANMU sannu da aiki!, ina raiha tayi ne naga ban ganta ba?"

Dago kanta wacce ya kira da amman tayi tana cewa "yawwa meerah raiha na ɗan aike ta ne bayan layi, gidan jajiya kareemah zata kai mata humra"

Nooding kanta kawai tare da cewa "Ina Affan naga ban ganshi ba..... Kafin ma ta rufe bakin saiga wani ɗan bakin yaro nan a guje irin ɗan shekara shida ɗin nan zuwa bakwai, a guje ya faɗa jikinta tare da faɗin "oyoyo aunty meerah na!"

Rungume shi tayi tana sakin dariyar farin cikin nan ta buɗe bakinta kenan da niyar yin magana, gaji an wani janye shi a jikin ta.

Cikin haki da masifar dake cin gabjejiyar matar dake tsaye ta rike hannun yaronta ƙammm, "meerah ki fita a harkan Affan fa, ko sai kin iskan tamin da?, duk yaran gidan nan da suke nan ga sunan kamar jamfa a Jos, amma duk babu wanda kika liƙema sai ɗana dalilin ki iskanta min ɗa ko?, to wllh bari malam ɗin ya dawo bazai yiwu ba dole ne yau na datse alaƙar dake tsakanin ki da Affan"

Kanta dake mata ciwo ta riƙe domin dama komai take yi dauriya ne kawai sharrrrr wasu hawayen takaicin familynta ya saukar mata,

_Wai sai yaushe kan family's nasu zai haɗu wuri guda?, sai yaushe zasu gane Allah da girma yake?, yaushe ne zasu san daɗin zumunci da ɣan uwan taka, gidan mu ya kasance wani irin gida ne me cike da son kai da son zuciya, kowannensu yana tafiya ne ya kife kansa kaɗai ya sani da rayuwar yaran sa.

Gidan mu yafi karfin a ƙira shi da ko wanne irin suna, domin kafff iyaka bincike na na gaza samun sunan da yayi daidai da rayuwar gidan mu, kawai zan baku abin a dunƙule ne kowa yaje ya nemi fassara!.

Mahaifin mu malam Abdullahi gwani yana da mata huɗu, duk wani haƙki na uba ɗa yana bamu saidai sammmm iyayenmu basa taɓa fashimtar hakan, kullum babban burinsu shine meda gidanmu filin yaƙin sunƙuru dana fili.

Ga yawan tarin iyalan da Allah ya bashi, gamu da masifar dangin kamar tsaƙi amma sai ka kasance jajirtacce ɗan zamani zaka zauna da kowa lafiya a sannu a sannu muna tafiya, zaku fashimci halin kowa da kuma manufa na_

Wannan keñan

Amma dake zaune tana ci gaba da zuzzuba humrarta cikin kwalabe idan ƙasa tana magana to kuwa tayi ita ma, haka Maman Saude ta karaci bala'inta tayi gaba ita da Affan dake ta kuka, yana miƙo min hannu, sai tallar ƙeyarsa take.

Na yunƙura zan tashi keñan yar ƙaramar wayata irin tecno common ɗin nan tahau ruri cikin waƙar hamisu breaker me taken _Kada ki bari zuciya ta zuga ki_ saurin kallona Amma tayi tare da tsare Ni da manyan Idonta wanda duka muka gada daga gare ta, Cikin in ina nashi ga faɗin.

"M.... MD ne, Ammah wai yana son za'a fira dani, kuma kinji wai dole sai dani za'a yi firarn, bayan duk ga su mardiyya nan su hayatu amman dole sai dani za'a yi wai"

Kanta ta mayar taci ga

□ MIKIYA □

{Mai hangen nesa □}

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/DGIo9iiSjlgJPPqFHNtddH

_____

NA MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

□□□

Aikin ta ba tare da tace komai ba, haka yaci gaba da ƙiran Ni ban ɗaga ba kuma ban tafi ba.

"Ki amsa shi, Idan kuma baki so ki bashi amsa ki dena ja masa rai har haka!"

Ganin abinda nake son ta fashimta ɗin bata fashimta bane, ya sani faɗin.

"Fuskata za'a haska a yayin firan Ammah!"

Saurin ɗagowa tayi tare da dubana sai kuma tamin nuni dana shige ɗakin kawai, alamun bata son maganar. Handbag ɗina na ajje a kan doguwar kujerar dake parlourn mu, dake ciki da parlourn ne dakin namu, kayan jikina na rage ina faɗawa kan kujerar tare da kwanciya bayan nasha maganin ciwon kan.

A take nannuyan barci yayi awon gaba dani, ban farka ba sai bayan sallar magrib, daƙyar nake Iya buɗe ido na sabo da nauyin da suka min, Adda'ar tashi daga barci nayi tare da tashi ina fita alwula na ɗauro na data salla ina zaune na haɗe kaina da gwuiwa na abin duniya duk sun gama sanyoni gaba raiha ta shiga ɗakin, zama tayi kusa dani tare da daura kanta saman ƙafafuna tace, "Yaaya kije Inji baffa yana ɗakin zaure"

Dammmm gabana ya bada sautin bugu baffa kuma yake ƙirana a irin wannan loƙacin kuma. Jiki babu ƙarfi na miƙe ina fita tare da nufar ɗakin zauren.

Da sallama na shiga ya amsani tare da nuna min wurin zama, zaman nayi tare da gaisa shi ya amsani a nutse, "ko miye dalilin daya sanya Maryam ƙin amincewa Md firar da ake son yi da ita?"

Kaina sunkuyar ina wasa da yatsun hannuwana cike da ladabi na furta, "Videon kai tsaye ne za'a haskaka ma duniya!, shi yasa sammm naƙi aminta da hakan, domin acikin sharruɗanka babu ɗaukar video!"

Wani gwauron Numfashi ya kawo ya sauƙe tare da dubana, "A gaskiya banyi tunanin haka abin yake ba amma kije babu komai kije ayi firar kariyar Ubangijii yaci gaba da tabbata a gareki, Allah Miki albarka tashi kije"

Da saurin umman mariya ta ɓoye bayan bishiyar dake kofar fita a dakin, domin dama badai iya laɓe ba, Ni kuwa banma san tanayi ba tunda cikin yanayin dana kasa gane masa na baro dakin.

AK

Ahankali cikin nutsuwar sa yake saƙkowa daga upstairs nashi zuwa wangamemen parlourn gidan, loƙacin sha ɗaya da minti sha biyu, kunga kenan minti uku ya rage masa.

Zamani tv

Duk da kasancewar yau kwata kwata bata niyar zuwa wurin aiki, amma haka ta danni zuciyarta ta fito tun sha daya saura, gudun kada tayi lettt, sai gashi kuma har yanxun wajen sha ɗaya da minti goma shiru shiru babu labarin zuwan nashi.

Ɗan madaidaicin Agogon Rolex ɗin dake hannunta ta shiga dubawa ganin har sha ɗaya da mintinan ashirin da biyar tayi bai iso ba, hakan yasa ta jan ɗan ƙaramin tsoƙi, domin jira na ɗaya daga cikin abinda tafi tsana a cikin rayuwarta. Na miƙe kenan ina fita daga cikin department namu wasu irin fitattun narkakkun motoci guda uku suka sanyo kansu cikin coumpaund na gidan jaridar namu, hakan ya sanya ni ja baya ina komawa cikin dakinmu inda mardiyya ta shiga tsokana wai kwana biyun nan kamar wacce akama turen rashin son magana, nidai ci kanki ban ce mata har zuwa loƙacin da Md ya ƙara so cikin department namu, cikin wani irin rawar jiki sai faman zazzare idanuwa yake ya tsohon maye.

A kaina ya fara sauƙe Idanu, cikin rawar murya ya furta, "MEERAH da dukkan alamu wannan baƙon namu wani ƙusar ne ke kinga wasu irin rantsantstsun motocin da yazo dasu?, tare da wasu samudawan escort, baki ɗayan sa tun daga ƙafarsa kamo fuskarsa a rufe suke cikin wasu haɗaɗɗun suit baƙaƙe ke hatta takalmin ƙafarsa abin kallo ne, maza yi sauri ki fito, kana ki tabbatar kin cire wannan liƙabin da kika kwama a fuska"

Ko amsata bai ji ya fice harda haɗawa da ɗan gudu gudunsa, yake zai shiga kenan ya kusa cin karo da hancin bindigar dake hannun miles, wani irin zaro Idanu Md yayi, domin shifa sai yanxun ma ya kula da uban manyan bindugun dake hannuwansu, kuuuuuuu cikin sa ya bada sauti, gumi na keto masa, miles dake zuƙar cigarettes Samm bai kula da yanda ya tare hanyar da bakin bindigar saba,

hakan ya sanya shi saurin janye wa yana tsare Md da firgitattun idanunsa da suka kada sukayi zajurr. A gujeeeeeeee MD ya zura har yana neman hantsilawa "innalillahi wa'inna ilair raji'un, me yake shirin faruwa damu kodai kidnapped namu aka zo yi "

Ya faɗa a bayyane amma sai ya daure yana ƙaraso cikin Office ɗin nasa.

A ƙalla Saida na ƙara wajen 10 mint da fitar Md ɗin, kafin na fito, Nima dai ganin wannan samudawan hannuwansu riƙe da manyan bindugun Saida ya razanani, amma na dake don nasan matsoraci baya taɓa zama gwani.

Haka na ratsa tsaƙiyarsu na fice cikin takun daya fi kama da a ƙira shi dana yanga, saidai sammm ba haka bane haka Allah ya halicceni, zuwa wannan loqacin tuni wanda yake zaune harya fara fusata da zaman jiran yarinyar da murya ta kaɗai yaji, don ko photon ta bata yarda ta taɓa ɗaurawa a media.

Wani irin mahaukacin ƙamshim turare ne ya fara welcome nawa, tun daga bakin ƙofar, a nutse na sanya zara zaran yatsuna ina tura ƙofar Office ɗin, ya ɗago kansa da Nijar yama Md magana yaci karo da zanen jan lallein yatsun hannunta, kafin na bayyana kaina cikin qaton hijjabina da kuma niƙab ɗina.

Cikin yar siririyar muryata nayi sallama wanda Md ne kaɗai ya amsa ni banda mutumin dake haƙimce saman kyakkyawar kujerarn da nayi tunanin daga ina Md ya samo ta, don dai nasan Bama da irinta cikin kaffff gidan jaridar namu.

Banko damu da yadda duk mutanen dake cikin Office zubo min Ido ba, domin duk da ko ina na jikinsa a ɓoye yake amma sai suka gaza samun sukuni. kujerar dake pacing dashi naja na zauna,kasancer nasan shine nawa mazaunin. sai table ɗin dake gabanmu wanda ya raba tsakanin mu, an ɗaura glass cup guda biyu masu ɗauke da ruwa, sai dai an rufe su da ɗan ƙananun fai-fai.

Ta ƙasan ido na ɗan saci kallon sa dan koda na zauna ban tanka musu ba, ban kuma zare niƙa ɗin fuska na ba. Haka naci gaba da ƙare masa kallo duk kuwa da cewar bana iya ganin komi nashi, har yatsun hannuwansa kuwa abinda zan iya faɗi kawai shine da ganinsa ba karamin mutum bane, ko daga yanayin zaman da yayi irin na shahararrun sarakunan nan ba muna sarki ba, sai hujin dake kunnensa ta ɓangaren hagu ya sanya wani diamon ring barima color'n gold.

Ɗan taɓe baki na nayi tare da janye idanuna dake kansa, Cike da ladabi Md ya ƙaraso tare da maƙala masa abin magana a jikin jacket suit ɗinsa. Nima ya miƙomin na maƙala a jikin hijjab ɗina, Sai da aka tabbatar mun gama kimtsawa sannan aka ɗora camara a kanmu. A nutse na sanya fararen hannuwana ina janye niƙab nawa zuwa saman fuskana, cikin aro jarumta da bada attention Kamar bani

ba, sai da na kalla cemara naima masu kallo sallama tare da gaisuwar barka da wannan loƙaci tare da fatarn sake kasancewa damu a shirin mu na kai tsaye, dangane da wannan bawan Allah dake son bamu ƙarin haske game da AK. (Wama ya sani ko AK ɗin ne) Na faɗa aceñnn ƙasar zuciyar, sai kuma nayi saurin faɗin (kai hakan ba bazai taɓa iyuwa ba, bayan ance shi kamar aljani yake kuma tunda yake babu wata cemara data taɓa haska shi aduk tsawon rayuwarsa, saidai kawai sunan daya karaɗe ko ina sabo da mumman aikinsa)

Saurin dawowa cikin hayyacina nayi dan gyaran muryan da aka min a take na dawo da ainihin nutsuwa na zuga ga dubban jama'ar da ke son kallon mu. Cikin tsare sa da Idanuwana duk da cewar bana iya ganin ƙwayar idon sane, na furta.

“Assalamu alaika ranka ya daɗe”.

A hankali ya motsa lips ɗinsa ya amsa min da “Wa'alaikissalam”

cikin muryar dake tamkar wanda akama dole. Kai tsaye zaka taɓa fahimtar kallona yake ko akasin haka ba saboda akwai eyeglasses mai duhu a idonsa. Bayan irin hular nan ta sojojin da suke sanya wa.

Yinai kamar ban damu da abinda yay ɗin ba nima, na cigaba da faɗin, “Wannan shiri na maka barka da zuwa, tare da nuna farin ciki matuƙa wajen zaɓarsu da kayi duk da bamu san dalilin ka nayin hakan ba, duk da bamu san waye shi ba"

“Barkanmu tare fatan Alkhairi ma duka jama'ar dake sauraraen wannan shirin!"

"To masu kallo zan iya cewa duk sai ku sake matsowa gaban akwatinan talabijin naku, masu rediyo su ƙara sauti domin ji daga bakin babban baƙon namu da musan waye shi ba!”

Sai kuma na sake juyowa garesa tare da faɗin, “Ko zamu iya sanin cikakken sunan ɓoyayyen baƙon namu?”

Wani irin kafirin murmushi ya saki irin na gefen bakin nan, Cike da wani salo ya sake harɗe ƙafafunsa da yay crossing cikin motsa lips ɗinsa kaɗan ya furta. “ABDOUL-MALEEK KUWAIT"

“to Saidai kanmu ya daure da sunan baƙon namu, gashi kuma bama iya kallonka kai tsaye, duba da cewar kazo mana da batu ne akan wannan babban CRIMINAL ɗin Wato EAGLE, wanda ya kasance cikin aikata tarin ɓarnuka marasa ƙyau, wannan shi

yaja hankulan masu bibiyar wannan tasha ta zamani tv jin batu ne akan CRIMINAL ɗin da ake nema ruwa a jallo!"

Wata zazzafar iska ya fesar daga cikin bakinsa na wasu sakanni sannan yay wani ɗan murmushin gefen baki, a taƙaice ya furta, "Kai tsaye ki ɗauka kina tare ne dashi wannan babban CRIMINAL ɗin da kowa ke nema ruwa a jallo"

Manyan Idanunta da suke kama da na mashayiya, uwa uba tsarin halitarsu da girman da suke ta ware baki ɗaya, tare da wani irin zaro su Wanda har saman fattar idon Saida ta ɗan kara faɗi kadan. Tana tsare shi dasu tamkar irin me tuhumar nan nasa, A nutse ya zare baƙin sun glasses in daya manne fuskar sa dashi, tare da kafe ta da nashi manyan Idon wanda kana kallon su zaka so fara kawar da dubanka, dan ba irin idannuwan da ake tsatsarewa da kallo bane, ga wani ruwa ruwa mai nuni da cewar Saida aka shawu kafin a fito,wanda ba dan ta kasance mai tsaurin ido ko mai taurin kai bane da taurin zuciya babu abinda zai hana ta kutsawa a gujeeeeeeee.

hasalima ana ƙiran da farar kurane amma Halittarta mai bayar da tsoron ce ita ma

Farar fuskarta dake ɗauke da kwantaccen gashi a gaban goshinta, wanda lafcecen hijabinta bai hanna su bayyanuwa, A hankali ta sanya hannunta mai ɗauke da awarwaraye na roba irin masu kyallin nan kwaya biyu pitch color ta shiga mirza saman goshinta irin tana cike dashi ɗinnan.

A hankali ya sake zuba mata ido tun daga yanayin yadda ta zazzaro ido har zuwa sanda ta shiga mirza saman goshinta yadda Idannuwanta suka rinqa sama da ƙasa. Haƙorinsa ya ɗan datse yana ci gaba da mata kallon ƙasar Ido.

"Duk da ance shi ɗin ba kamar sauran mutane bane, amma a yadda nake ji ɗinnan idan har nayi gaba da gaba dashi zan iya kashe shi a matsayina na me kishin ƙasa"

Haka ya riski muryan ta me kama da waƙa take rerawa ba masifa take sirfawa ba, harda irin mutsitstsike hannuwan su bada sautin ɓasss.

Dade beyi niyar jimawa a zaman tattaunawar ba domin akwai manufar shi na yin hakan, akwai saƙon da yake son masu shi su ɗauka. Don haka cikin wani irin jannn hankali da salo me kyau ya ɗaga hannunsa sama tare da mirza shi irin gintsewar nan yace.

"Mutuwa dai kika ce idan kuma ya kasance shi ɗin baya tsoron mutuwar ba fa?"

Zuciyarta ce ta ji ta buga da mugun ƙarfi amma cikin ƙarfafama kanta gwiwa ta mayar masa da amsar daya bata daidai dashi.

"Idan harya kasance baya tsoron mutuwar, ya bayyana kansa mana ga jami'an tsaron da suke fafutukar nemansa ruwa a jallo, nasani dai baifi ƙarfin hukuma ba saidai idan ya kasance shi ɗin matsoraci ne, domin jarumi ba'a san shi da yakin suƙuru ba ya fito ayi na sarari gaba da gaba shida matakan tsaro a gabza yaƙi"

Wani irin ɗan waro mata Idanu yayi, tare da mata alamar jinjina da hannuwansa, kafin cikin hosky voice nashi ya furta.

"Idan kuma ya kasance su jami'an ne da kansu suke tsoron tun karar safa? Mutumin daya Kasan ce baka gane gabansa balle bayansa balle ka gane inda ya dosa, yanzu duk rikicin da tarzomar da ya haɗa a garin nan amma ace yasha, kinga kenan ƙarfinsu yafi ya musu zarrar da basu taɓa iya ja dashi ba, idan kuma sun shirya to Bismillah,

hakan bai hana shi ya shiryawa kansa zuwa mataki na gaba ba kamar yanda ya tsara ma kansa , yana da karfin hali sosai, komai zai aikata yana aikatawa ne cike da kwarin gwiwa ɗari bisa ɗari, tare da yaƙini da kuma sanyawa a ransa tabbas zai yi nasara, Ki sani sawa a rai ne yasa falke baya jin wahalar tafiya,wanda idonsa basa gani sunanshi makaho, Ammah cikakken makaho shine wanda zuciyarsa bata gani kamar dai jami'an tsaron ku.

Haka za Kafin ya sanya kansa cikin harkar sai da ya shiryawa kansa komai da komai, tare da tsara ko wanne mataki!, don haka idan ma da wata manufar suka tsoma zancen zuwa gidan jarida, wannan shine yaƙin sunƙurun da suƙe ikirarin AK EAGLE yana yi, wannan yaƙin iya na filin daga ne bawai na media ba, don haka sojoji, yan sanda, wannan yaƙin ba na nan bane, yaƙi ne na iyaka jami'an tsaron da suke ikirarin suna son kare ƙasar su, kana Idan suna jin sunkai sun kuma isa su nuna jajirwarsu, wajen dawo mana da governor da kuma minister ta hanyar nuna jajircewar su a aiki".

Zuciyar tace taji ta matse da tunanin irin fassarar da yayi ma Maganganun sa

Atake taji tana jin wani abu na narkewa a cikin jikinta kamar ƙarfen da ake ƙonawa a cikin wuta, tabbas yayi maganar gaskiya, wannan yaƙi ne na jami'ai, bawai su kawo media ba, kafin ta ɗago wayammmm taga babu shi babu alamunsa, a wurin da yake zaune, jikinta ne ya shiga wani irin mazari da tsoron masifa, tuni ta gaza

sarrafa kanta wajen dawo da nutsuwar ta, tana shirin tashi ne kuma tayi gamo da Katar ɗin ganin yar ƙaramar fara tasssss ɗin takarda, wanda take ƙaya ce cikin kyakkyawarn ado, tare da tsarin rubutun daya fi kama da a inji aka zana, cikin manyan harrufa aka yi rubutun kamar haka.

" FLOWER BERRY PIE, THANKS DA KASANCEWA DA AK EAGLE "

A razane ta tayi cilli da takar dar tana juwo gasu MD, bata tashi aune ba sai ganin Md tayi ƙarƙashin dujuwar office ɗin.

To ai shikenan kooooo saimu gimtse

By AMMEY LAYLERH ✍

 MIKIYA *

{Mai hangen nesa }

~We want an end to oppression~

https://chat.whatsapp.com/DGIo9iiSjlgJPPqFHNtddH

#HOT LOVE

#ROMANCE

#AK FOV

#DEEP ASSUMING FOV

_____

#*NA MARYAM NASEER*

#~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ OFFICIAL MIRRAH ~*

Page 9&10

□□□

_____

★★★★

Ba md kaɗai ba duk wani ma dake ƙarƙashin zamani hankalin sa idan yayi billions dollars to a tashe yake. Cikin tsananin tashin hankali itama ta shiga zara idonta, bawai don tsoron abinda ka iya zuwa yaje ba. Sai don kawai hangen irin tashin hankalin da Annenta da zata shiga harma da baffan ta.

Hankalin ta bai sake tashi ba saida jiniyar yan sanda ta karaɗe gidan jaridar baki ɗaya cikin fitar hankamotar yan sanda,wasu zafafan hawayen ta kuma sharewa wanda take jin zafinsa tun daga tsaƙiyar ƙirjinta, me cike da tsantsar tsabar AK me zafin gaske wanda a duniya taji bata taɓa tsabar wani abu ba kai tsaye kamar AK ɗin. Gangan zunzurutun matasan da suka yi zanga-zanga bakin gidan jaridar ne suka yunƙuro da niyar kai hari ga MEERAH tare da Md, wanda zuwa loƙacin yake neman fita a hayyacinsa.

Banda zazzara ba ido babu abinda yake ga uwar zufar data riga ta gama kwaranye masa jiki, na tsabar tashin hankalin da yake ciki, kamar bashi bane mintoci kaɗan yake cikin mafi ƙololuwa a farin ciki, amma gashi komai ya zama shuɗaɗɗe cikin abinda bai wuce 30 mint ba. Zufar dake tsatstsafo masa ya share a karo na ba adadi tare da sauƙe numfashi kaɗan, sai kuma ya ɗan kiwo da dubansa zuwa ga meerah amma ga mamakin sa sam babu wani alamun tashin hankali tattare da ita. Hakan ya jefa zuciyarsa cikin kokwanton ko dai ta samu attack ne koma shock zai ce shidai baima sani ba, bai dawo daga duniyar tunanin daya afka ba yaji tsaiwar motar su a police station GTA ɗin dake babban birnin Lagos ɗin.

Babu ɓata loƙaci akayi ciki dasu wanda suka kuma tadda cincirindon al'ummar dake cike da bakin police ɗin, suna fadin a sudai adalci suke so,mebi ba ai harda haɗin Md ɗin dá yayi fira dashi. Shidai Md ido ne kawai nashi sai kunnuwan sauraren domin tuni gaɓoɓin jikinsa suke tsaya cak da aikin su, wajen iya sarrafuwa, A gaban babban d.p.o aka sune su kai tsaye

Su kuma sauran jami'an sukaji da matasan da suka yi zanga-zangan, kai tsaye dake akan babban criminal ne ake magana yasa sam babu wani jan batu akan jinkirta maganar.

Army Headquarters

Suna ganin komi dake wakana amma sukayi biris babu abinda suka furta akan maganar dake ƙara yaɗuwa game da kamen da aka yi. Amma ta ƙasa sune sane da komi ɗin dake wakana a police ɗin, amma a zahiri kam shiru kake ji.

A police station kuwa dake Md shine namiji shi suka fi tsananta bincikensu a kansa, amma amsar ɗaya ce sam baya da masaniya akan Ak ɗin. Hakan yasa jami'an ganin kamar raina musu hankali yake son yi, shi kuwa Md tsoro ne me tsanani tattare da zuciyarsa na irin uban gargaɗin da yasha wurin wanda suka bashi batun kai tsaye, don haka baya da yacce ya iya dole ne yayi gum da bakinsa, tunda yasan idan allurar sojoji ta tashi sunfi Mahaukacin kare iya hauka, bare ma wanda ya bashi bayanan kai da ganinsa kasan ba ɗan ƙaramin mugu akayi ba.

*********Gidan su meerah kuwa idan hankalin Annenta yayi dubu to a tashe yake, Raiha kam zuwa wannan lokacin duk da ƙananun shekarun tayi kukan rashin kwanan meerah ba'a gida ba, amma haka anne ta danni zuciyarta ta hana nata tashin hankalin bayyanuwa, ko washe gari kuwa mutan gidan tamkar sabuwar kasuwa haka suka tashi da hada hadarsu, tamkar basu san abinda yake faruwa da meerah ba. Baffa kuwa tun bayan da akayi sallar isha'i babu wanda ya sake jin motsin sa daga mutanen gidan, domin kuwa kai tsaye meerah itace raunin sa, haka za itace sanyin idaniyarsa. A loƙacin da wannan mummunan labarin ya riskeshi, saida yaji numfashinsa ya tsaya cak da aiki, duk wata hanya saida yabi a sirrance don ganin al'amarin bai girma har haka ba, amma akace idan wani sammako yayi to wani kwanan tsaye yayi inji masu iya magana.

Shi ɗin babban malami ne na addinin musulunci amma sai gashi ya rasa duk wata ta ganin meerah ɗin ma kawai, wannan shine dalilin hana bayyana kansa da yayi, domin sam bazai iya kallar tsakiyar idon Anne ya faɗa mata an hana shi ganin meerah ɗin ba.

Sosai bakar Ralls Rayce ɗin ke shahara uban gudun fitar hayyaci a shimfiɗeɗen kwaltan, babban burin Isha Manu bai wuce ace ya ganshi cikin police station ɗin ba, domin tun jiya daya sami zancen hankalin sa yaƙi kwanciya, bacci ma ɓarawo gwanin iya sata kasa sace sa yayi, haka ya kwana cingirgir a zaune domin gani yake ai kamar ma Ak ɗin ne aka kama, don gani yake shine mutum na farko da ak ɗin ya fara illatawa mafi muni a cikin rayuwa.

AK

Tunda ya riga da yabar baya da ƙura bai sake bi ta kan kowa ba, duk kuwa irin fifigen da jama'a harma da jami'an tsaron suke famar yi a kans, amma yayi shiru yayi biris da dasu yaƙi magantuwa akan komi. Badan baya da yacce zai yi ba a'a sai don kawai yana son ganin gudun ruwansu ne, ya dai manna musu bajon haukane kawai ya fisge abin sa, burin sa dama saƙon nashi ya Isa duk wuraren da yake son isar kuma sun isa, don haka yaci gaba da shimfiɗa life ɗin sa yadda yake so.

Zaune yake akan yar ƙaramar couch ɗin dake dining room, cikin hadaddiyar shigarsa da mafi yawanci yafi amfani dasu, fararen Dior sweet shirt ne sanye a jikinsa, sai kuma dogon wandon trouser kansa sanye cikin luxury fcap ɗin daya sanya cikin natsuwa yake breakfast nashi da ƙayatattun dinner ɗin da Vincent ya musu odar daga wani tsadadde kuma Hadadden eatary luxury

Chips pepper soup na zallar tsoka sam babu ƙashi ko kaɗan a jiki, sai kuma ketchup

Hankali kwance yaci gaba da yin ɗinner gefe guda kuma yana sarrafa laptop ɗin dake gabansa. Kamar koda yaushe yauma zagaye samudawamsa suke dashi tamkar wasu masu gadin gidan wuta, a kasaitance yaci gaba da dakilar laptop ɗin bayan ya kammala breakfast in da kamar 20 minute ya kunna cigarettes yana busa hayaƙin. Almost 30 minutes ya miƙe cikin yana nufar upstairs cikin takun mazan taka.

A police station kuwa duk yadda kuke tunanin wannan abu da sauki toya zarta haka, domin kuwa ta ko ta ina ƙara rura wannan wannan maganar ake. Abin kamar wata alamara saiga labarin kama su meerah ya zama lates a yanzu musamman media da gidajen rediyo a cikin kwana guda kawai. Kusan dai ko ina ba'a rasa yan adawa tuni labaran ya gama karaɗe media dama kusan duka duniyar zance baki ɗaya.

Md kuwa cikin kwana ɗaya takk ya fita a hayyacinsa sa, gogar tamu kuwa da ido ne kawai take bin kowa take kuma kallon duk wani abu dake wakana a tsakan kanin su, zuciyarta ta bushe ta ƙekashe taƙi kuma ta magantu duk kuwa uban jaddagadeden da d.p.o yake a kanta zuwa sauran jami'ai tun a yammacin har zuwa wayewar garin ranar.tana zaune ta kafe wuri guda da idonta daya yayi jaaaaa, a hankali wata police ta Turi ɗakin tsananin hasken daya haske mata idone ya sanyata ɗago da kanta, plate ɗin robar dake hannun ta dake shirin ajje mata a gaba, amma kuma ga mamakin ta sai taga meerah ɗin ta ɗaga mata hannu alamar bata da buƙata. ”ma'am Ina buƙatar text book da pen idan ba dmw pls”

Tayi maganar ba tare data motsa daga yadda take ba, ɗan jim police ɗin tayi alamar tunani kome ta tuna kuma sai tayi saurin juyawa tana barin ɗan suƙurƙurin ɗakin ajje masu laifin baya ta rufe. 10 minute sai gata ta dawo ɗauke da text book ɗin da kuma pen tsaye tayi akanta, ba tare data damu da tsaiwar data mata a kai ba ya ta fara aiwatar da abin da zuciyarta ta gama tsara mata, kyawawan idaniyarsa masu kama dana mage ta shiga zanawa a pepper ɗin, exactly tayi zanen full face nashi sai dai iyaka eye nashi ne a bayyana ne. Ita kuwa wannan police ɗin har wani sake karkatar da kai take wajen hango zanen.

Tana kammala zanen ta miƙa ma police ɗin text book in, jiki na mazara ta fice ta text book in a hannun ta kai tsaye babban office ɗin d.p.o RT Atya ta nufa. A lokacin d.p.o na tare da Isa Manu Atya ta ajje text book in gabansa.

”What are you doing to say?"

"Sir. Meryam yebdullahi goni meerah!"

"What?"

D.p.o ya faɗa a zabure tare da miƙewa yana nufar hanyar woje, har da yar sassarfa yake haɗawa ganin ya cimma ɗakin da take. Hasken daya sake haske idonta a karo na biyu ne ya sanya ta sakin wani lalataccen kill smile dama tasan za'a rina, samm ta rasa mine ma ya hanata aiwatar da hakan tun a juya.

Zanen fuskar da tayi aka d.p.o ya tura gabanta, "muna buƙatar ƙarin haske akan zanen da kika bamu!"

(Anzo wajen) ta faɗa a cennn ƙasar zuciyarta.

A zahiri kam ɗan duban wanda ake da d.p.o tayi a kai kaice ba tare da shakkar komi ba ta furta.

"AK kenan! Inda har da gaske kuna kan aikin ku, ga Ak nan ku baza yaranku su fara farauta iyaka idonsa ne kawai nima na sama gani"

jikin d.p.o har tsuma yake ya furta "da gaske kina da tabbacin wannan face ɗin na Ak ne?" Noding kanta tayi alamar tabbatar wa.

A 380 suka bar ɗakin tsabar sauri hular d.p.o har faduwa take. Cikin ƙanƙanin loƙaci aka baza fuskar Ak da ake nema ruwa a jallo. Kanka ce me matasa sunyi caaaa a media game da fuskar Ak da aka ɗora.

★★★

Wani irin kafirin murmushi Ajmaal ya saki a lokacin daya kalla zanen fuskar Ak ɗin shishar daya ke zuka ya feso da hayaƙin matashiyar budurwr ko nace ƙaruwar da yake tare da ita ya sake mannata da jikinsa, a bayyane ya furta. "AK muje zuwa da dukkan alamu wannan wasan me zafi ne!, Lallai na yarda da tauraron ki yana haske yar jarida meerah, kece tsanin Ni! Kuma nine mahayin" sai kuma ya sheƙe da wata iriyar dariya ta marasa hankali. Tare da hade bakinsa dana wannan budurwar, ita kuma cikin kwarewa a fannin ta wani shiga sarrafa gangar jikinsa tana karasa fitar dashi daga ɗan hankalin daya saura a gareshi.

★★★

Safa da marwa kawai yake famanyi a karo na ba adadi ke nan sai yana dab da cimma burin sa. Sai wannan ɗan gaba da fatihar yazo ya rugaza masa aiki. Baki ɗaya ya gama jigata kansa gumi sai kwaranye masa jiki yake. Idan bai manta ba governor da kuma minister suna hannunsa,kenan target ɗin Ak na gama dole shine.

"Inaaaaaaa hakan ma bazai taba yiyuwa sammmm" ya faɗa da ƙarfin masifa haɗi da kaima bango iska nashi, sai huci yake saukewa. (Kai wannan yaro uwarka ta haifo mana masifa da bala'i wllh) ya faɗa a cikin zuciyarsa. "Dole na dakile duk wata hanyar da nasan wannan ɗan shegiyar yaron da nasan zai ganni, kafin na gama samun mafita"

★★★

A bazata murmushin ya subce daga fuskar Ajmaal (dole na fara nuna maka ba kai kaɗai ne teterors ba Ak) ya ayyana hakan a cikin zuciyarsa tare da ciro wayar sa yana dialing wata number.

"AK! AK!! AK!!!, Da kyau tsohon abokina sheɗanin sheɗanu, kuma tsuntsu me wayo"

"Kwarai kuwa haka ne sabo da mun saba sheƙe sheɗanu tare da kai ba Ajmaal"

"Uyummmm naji daɗi dake fashimce haka Ak baban shadanu a yanzu haka dai nasan ka girgiza ba?"

Jin Sautin lalataccen murmushin Ak ɗin da yafi natsa a kaff cikin duniyar ne ak ya sakar masa. Ɗan zame wayar yayi tare da kallon screen ɗin sai kuma ya sake manna wayar da kunnunsa, still Sautin fitar murmushin ya kuma ji daga Ak ɗin. dip dip dip yaji sautin katse ƙiran da akayi ba tare da an sake furta masa komi ba. Shima murmushin ya saki domin wannan loƙacin yaci alwashi akan Ak ɗin sosai, shi kaɗai yasan shirin daya danajama hakan ciki kuwa harda ziro meerah acikin tafiyar.

To ai shikenan kooooo saimu gimtse

By AMMEY LAYLERH ✍

* MIKIYA *

{Mai hangen nesa }

~We want an end to oppression~

https://chat.whatsapp.com/DGIo9iiSjlgJPPqFHNtddH

NA MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ OFFICIAL MIRRAH ~*

Page 11&12

#KIDNAPPING

*DRUG TRAFFICKING

#AGGRAVATED ROBBERY

□□□

_____

★★★

Police station

Zaune farin dattijon yake gaban d.c.o bayan gama koro masa jawaban sa akan meerah ɗin,duba da uban kuɗaɗen daya zube masa wanda dama already yau za'a sallames, ganin tsuntsu daga sama gashashshe ne yasa jikin d.p.o har mazari yake wajen bada umarnin a kawo meerah ɗin. Cikin ƙankanin loƙaci sai gasu da meerah ɗin, shi kuma ya miƙata ga wannan dattijon. A kamilance ya musu sallama yana ma Meerah nuni da suke, saida ta ɗan yi dammm na alamar mi hakan ke nufi.kana dai tayi gaban, bata sani ba ko duk cikin aikin ne hakan.

Gaban wata arniyar bakar mota suka tsaya shi da kansa ya buɗema meerah ɗin ta shiga domin kuma zuwa yanzu ta fuskanci kamar gida ne za'a maida ta.

Uban gudu yake tsalawa a cikin motar wanda gudun har ma ya kusa tsorata meerah amma dake zuciyarta a dake dake sai taƙi barin tsoron nata baiyanuwa. Sunzo daidai round about wata kafurar Mota ƙirar Mercedez Benz tazo tasha gabansa, sai kuma yaji tsaiwar wata ma da bayansa hakan ya sanya zuciyarsa tsinkewa, amma sauya dake yana kawar da hasashen da zuciyarsa keson bijiro masa. be gama tunanin me ke faruwa ba ya ji ana ƙwankwasa window'n Motarshi da Bindiga daidai saitin kanshi kululu cikinsa ya kaɗa hanjinsa ya ɗuri ruwa nuni suka mishi da ya fito. hannu na rawa ya fito ganin wasu uban samudawan da yasan kuskure kaɗan zai musu su aika shi inda in aka tafi ba'a dawowa, yayi ɓeshi dukkaninsu suka yi suna sanye da facial Mask.

Umurnin da suka sake bashi ne a karo na biyu ne ya sa shi tunanin wannan wasu irin yɾan fashi ne? Inda ɗaya daga cikin wannan samudawan ke ce mai "Take off your clothes" da sauri yace "What?" sauƙar wani abu me ƙarfi yaji a gefen fuskarshi, da sauri yayi ƙara tare da dafe gefen kanshi yaji danshi danshi Alamun jini, cikin ɗaga murya yace "take off your clothes,i wont ask again" da sauri dan farin dattijon yayi yanda sukace, ya rage daga shi sai gajeren wando da guntun singileti, hatta takalmanshi zobe da Agogo, sai da ya cire, bai dawo daga duniyar daya tafi ba na wuccin gadi yaji sauƙar

Bindiga a kanshi.

Ɗaya daga cikin samudawan ne yama na kusa dashi alamu da ido.

Gaban motar ya nufa kai tsaye Sleeping powder'n dake hannun sa ya shaƙama Meerah, Kafin ta samu damar cewa komai ne taji abu a fuskanta. Yuuuu taji kanta ya fara mata, Cikin zabura tai yunƙurin dira daga cikin motar ɗin, sai dai ta kasa hakan dan cikin ƙanƙanin loƙaci jikinta yay wani irin masifar nauyi nan ta silale jikin kujera idanunta na lumshewa. Daga haka bata sake sanin mike faruwa ba kuma.

Baifi 10 minute da fitar motar ba baffan meerah ya shigo station ɗin, sosae hankalin sa yayi wani kalan masifar tashi, jin wai mahaifin meerah ɗin yazo yayi belin meerah ɗin. To waye mahaifin meerah kuma wanda ya wuce shi?, Kodai hankali ne kawai suke neman rena masa. Amma saiya danni zuciyarsa cikin tsanako da dattako irin nasa yabar station ɗin ya barma zuwa an jima kaɗan, wai a ganin sa kawai yau ɗin ma basa da ra'ayin barin sa ya ganta ne kawai shi yasa suka ɓullo masa da wannan zancen.

★★★

Wani kalar furzar da iska yayi yana maida kansa jikin saman sopa ya kwanta tare da lumshe idanunsa a hankali. Shi kaɗai yasan abinda yake ji game da taurin kan yarinyar data zaba buga game dashi. Ya fahimci lallai bata fahimci a ramin da take neman jefa ƙafarta bane. Amma zai bata loƙaci ta gama nata kalar ɗan ƙaramin wasan kafin ya fara buga babban game da sai tayi dana sanin sanin AK a rayuwarta da tayi. Idan ita ƙaramar yɾar iskar layi ce, zai tabbatar mata shi na duniya ne baki ɗaya, dan ba zubar da jini kawai ya iya ba harda cin uban duk wanda ya shiga sabgarsa. Lallai ta ɗaukarma kanta Dala ba gammo tunda tayi kuskuren zana fuskar sa, ya fahimci ita ɗin yɾar zafin kaice tun daga yanayin yadda ta mu'amulance shi a gidan jaridar su, amma ba komi tayi nata zafin kan ta gama duk zai sauƙe mata su kuwa nan bada jimawa ba.

Ya jima a wajen zaune har su Axton suka dawo ɗauke da abincin da Vincent ya sasu suka yo order. Amma shi boss ɗin sai yace bazai ci ba. Ya haɗa coffee kawai da biscuits mai daɗi. yana shan coffee ɗinsa da biscuit tare da nazartar yarinyar.

Koda ya kammala shan coffee ɗin bedroom ya wuce kai tsaye Maimakon kwanciya bathroom ya faɗa, ya haɗa ruwa mai ɗumi cikin baththtub tare da haɗa kayan ƙamshi kala-kala a ruwan sannan ya shiga ciki. Sai da ya kashi mituna a cikin ruwan na ratsashi da miƙar masa da kowace gaɓa sannan ya fito ya shiga wajen wanka ya ɗauraye jikinsa. Bayan ya fito salla ya fara gabatarwa tare da shafa'i da wutiri sannan ya shiga shiri. Yayi ƙyau sosai cikin shigar tasa tamkar ka sacesa ka gudu. Ga wani uban ƙamshi na tashi tamkar duka Company'n haɗa turaren ne a jikin sa. Sumar nan tasha gyara daka gansa kasan ya haɗa jini da masu jajayen kunnuwa. Hakama kwantaccen gashin sajensa sai walƙiya yake gashi kwance luf-luf ya sake fidda taswurar doguwar fuskarsa. Sai da ya tabbatar komai ya masa yanda yake buƙata sannan ya fito cikin nutsuwarsa da takunsa na tsayayyen namiji.

National Hospital atarubus

3:45pm

Accidents and Emergency aka shiga da wannan farin dattijon dake sananne ne shi babu wanda bai san waye Isa Manu ba, A kaff cikin Lagos harma da zagaye ta cikin ƙanƙanin loƙaci aka shiga bashi taimakon gaggawa.

Ba ƙaramin tashin hankali su anne suka shiga ba ganin har bayan sallar isha'i babu baffa babu dalilin sa Raiha sai kuka take, baffa kuwa da kansa ya gama kullewa ne yasa jininsa naiman hawa nan take, bai sake tsorata da lamarin ba sai loƙacin yɞan sanda suka zo da batun mutumin da ya yi belin meerah yɞan fashi sun sun tare sa a hanyar sa ta mika Meerah ga iyayen ta a round about ɗin sa na shan kwanar anguwar su malam Abdullahi gwani.

Cikin abinda bai wuce kiftar ido ba labaran suke zake hargitsa media, ƙura takai ƙura kam a wannan loƙacin, a kuma daidai loƙacin ne aka shiga musu da malam Abdullahi gida a yanayi mafi munin gani. Nan da nan matan baffa biyu suka shiga yaɓama Anne maganganu baƙaƙe. Wai akan yarinyar data gama gantalewarta a titi suke neman rasa malam, wllh baza su yarda ba. Anne kammm zuwa lokacin ma ita kam babu abinda take iya fuskanta daga cikin maganganun nasu, a fisge taji kalmar ƙarshe daga cikin ɗaya daga cikin matan.

"Dama ai barewa ba zata yi gudu kuma ɗan ta ya rarrafa ba, wllh malam ka auro mana masifa da bala'i, gashi kuma masifar daka ɗaya yɞanta sune suke ƙoƙarin ajalinka, kaje garin kwashe kwashenka ka auro mace mara asali wanda ba'a san inda asalin ta take ba, wanda ya wuce yɞar gaba da fatiha me bakin duniya"

Dipppp ji da ganinta suka ɗauke daga nan bata sake sanin ainihin abinda ke faruwa ba.

★★★

Sannu a hankali na shiga motsa idanuna da suka min matuƙar nauyi da ɗaurewa. Sai kuma na shiga buɗesu sannu-sannu harna gama buɗesu. hasken daya cika idanunane ya sanya na ɗan tashi a zabure da sauri. komi daya faru ya ringa dawo min daki daki har zuwa sleeping pawdern da suka shaƙa min. Ƙirjina ne yay wata irin masifar bugawa da sauri na ambaci sunan Allah.

Cikin sauri na mike na nufi ƙofar bathroom ɗin da nayi amfani dashi wajen uzurina. Alwala na ɗauro sauri² gudu² na fito praymad ɗin da nayi sallah akai jiya yauma na nufa, a nutse na fara sallar cike da nutsuwa.bayan na idar na sulale a wajen ina saki wani irin kuka mai tsuma rai da da zuciya. Na jima kwance a wajen ina kuka kamar numfashina zai rabu da gangar jikina. Nama rasa ina zan kai tunanin na. Handle ɗin dakin naji an taɓa tare da shigowa mutumin jiya da dare ne duk da cewar fuskarsa a rufe take amma tsab na gama gane shi, kasancewata mutum bai kaifin basira, plate ɗin dake ɗauke da soyayyar wainar kwai ya ajje min tare da ledar bread recipe ya juya abinsa da niyar tafiya.

"Lallai hakan da kuka yi shi ne ya sake tabbatar min da cewar ku dukkanin ku lusaraine, kolaye ne tunda har kuka rasa abinda za kuyi sai kidnapping mace" nayi maganar tare da jan wani mugun tsaki.

Duk da ya tsaya cak tun fara maganata bai juyo ba. Harna kammala maganar kuma bai tanka min ba ya buɗe ƙofar ya fice tare da sauri tare da kulleni ta baya. Ido kawai na zubama ƙofar wasu kalar hawayen bakin ciki na sake gangaro min da gudun tsiya.

A yanzu ba wai kaina kawai nake tausayi ba su Annena baffana Raiha ɗina nake tausayi da halin da zasu shiga sune suke matuƙar tada min da hankali fiye da komai.

Bai cika 20 minute da fita ba sai gashi ya sake dawowa farin handkerchief ɗin dake hannun sa ya jefa saman fuskana hakan yasa na fara ganin bibbiyu kafin kuma na tafi luuuuuu.

Ban ƙara sanin inda kaina yake ba sai bayan sallar zuhr, a wani bedroom ɗin na daban na sake tsintar kaina ba wanda aka fara kaini ba. Da kyar cikin mutuwar jiki na miƙa na nufi hanyar da tsammanina ya gama bani bathroom ne, ilai kuwa bathroom ɗin ne toothpaste da brush na farke su a ledartarsu, saida na fara wanke bakina kafin alwala sallar zuhr tayi tare da fara duk wasu addaoin da suka zo bakina. Ledar takawey ɗin dake gaban gadon naja bisa dole zuwa gabana. Domin kuwa in banda kukan yunwa babu abinda cikina yake. Kaɗan na ɗan chakala na ture gefe domin ma samm sai naji bana jin cin abincin ma.

Mahaukacin ƙamshim da hancina ya shaƙar min ne ya sanya ni saurin ɗago kaina zuwa Said ɗin da naji ƙamshim na fitowa. Da wannan idanuwan dana zana na fara cin karo, wanda har ƙarshen numfashina baran taɓa mancewa dasu ba.

Sanye yake cikin wasu tsadaddun luzary Ride vizzon sky blue colour daga ƙasar rigar kuma fari kaɗan irin hadarin Dubai ɗin nan ce dai.sai lallausan farin wando trouser kansa sanye cikin hular luxary supereme irin ta sanyin nan sai facemask irin Turkish ɗin nan shima, yau kam babu glasess ɗin da yake toshe idonsa dashi. Fuskarnan a matukar haɗe. Chair lind ɗin dake gefe da gadon ya janyo zuwa gabansa, zaune yakai zama irin na wanda suka isa zama ne irin na zaratan sarakunan da suka kai sarakai ba muna sarki ba. Wanda hakan da yayi ne ya shagaltar da Meerah a kallonsa.

"What wrong with you flower pie?" Ya faɗa cikin daƙilallalliyar muryansa, a rikice ta dawo nutsuwarta tana dedeta kanta, tare da hararar inda yake zaune. A fusace ta furta

"miye Amfanin kidnapping na da kuka yi?"

Wani malalacin kill smile ne ya subce mishi a bazata. Domin samm baiyi zaton bakinta zai iya murta wata magana ba, amma kuma idan yayi duba da tsaurin idonta da tsaya samm hakan ba abin mamaki bane.

"Wannan bakin naki zai kaiki ya baro ki silly girl! Idan kika ce zaki buga game da Ak to kuwa tabbas zubar hawaye bata shirya barin idaniyarki ba ke nan"

Cike da tsiwa da son hana ganin lagona na sake maida fuskana gare shi tare da furta "Never for ever ka rubuta ka ajje Ni Meerah Abdullahi gwani saina sanya ka gudun ceton rai a tsakiyar karnuka"

A bazata yaji sauƙar kalaman nata don haka ya zuba mata cat eye's nashi tare da folding hannun wansa saman ƙirjinsa. Don shi maganar nata dariya ne yaso bashi amma dake tantirin kansa ne hakan ko ajikin shi. Saima gira ɗaya daya ɗage mata tare da furta "weldone pie" tare da juyowa da kallonsa a kanta ya sakar mata wani lalataccen murmushi.

"Tabbas kuwa karen zai mutu da haushin kurar"

ya faɗa idonsa cikin tsakiyar nata idanun still murmushin gefen bakin nan bai bar fuskarsa ba.

"Bad boy da dukkan alamu kana wasa da wannan Meerah ɗin amma dai muje zuwa musu iya magana sukance ba'a san maci tuwo ba sai miya ta kare"

Cikin majestical takunsa ya nufo inda nake tare da matsowa daf dani. "Did I look like a comedian to you?"

Yana faɗar maganar ya nufi hanyar barin bedroom ɗin baki ɗaya cikin nutsatstsen takunsa mai cike da ƙasaita. Bayan ya mata wata halamar data gaza fashimtar kota miye.

_____

Shigar Isa Manu a zancen ya saka yan sanda sake ɗaukar zafi, Dan a yanzu D.c.o ɗin ne ma da kansa yake gudanar da binciken kidnapping ɗin Meerah ɗin tare da Inspector atya murail.

Al'amari kamar wasa akan ɓatan Meerah ƙaramar magana na neman zama babba. Dan yan sanda sun matuƙar zafafan bincike akan maganar duk inda ka wulla magana ɗaya ce, duk da kuwa shi kansa Isa Manun kidnapping yarinyar yaso yi.

□ MIKIYA □

{Mai hangen nesa □}

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/DGIo9iiSjlgJPPqFHNtddH

NA MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~□ OFFICIAL MIRRAH □~*

Page 13&14

#ROMANCE##

#BLACKMONEY

#KIDNAPPING

*DRUG TRAFFICKING

#AGGRAVATED ROBBERY##

#AMAZING W*w(☞ □_□)☞

https://www.aihausanovels.com.ng********** Ai Hausa Novels **********

**********⬆ **********

DOWNLOAD More complete Hausa Novels, Education Books, Adventure, Drama, Mystery, Religion, Fiction, Non-Fiction, Romance, Meimor, True Life Stories & Others from our blog.

Visit > https://www.aihausanovels.com.ng

Ka tura mana sako ta adireshinmu na email, domin tuntubarmu ko turo mana hausa novel ko kuma post.

******* FOLLOW US ******

WhatsApp Number: 08104493215

Haka kuma domin shiga kowanne daga cikinsu za ku iya ziyartar shafin ku yi search na AI HAUSA NOVELS, hatta facebook group dinmu ma za ku samu.

********** ⬇ **********

********** Ai Hausa Novels **********

********** ⬆ **********

***Sosae police report ɗin da suke kan aikin nemo wanda sukai kidnapping yarinyar tare da case na Isa Manu suka sake ɗaukar zafi na gasken gaske.duk da shi kansa bai san inda kansa yake ba tunda yana very critical condition ne, wanda hakan keda matuƙar haɗari sosae.

Duk wasu wuraren da suka san zasu sami news ko yaya ne samm basa wasa da damar su, gashi babban yaron Isa Manu'n wanda baya a Nigeria'n ma yana daga ƙasar Poland ne yayi stating ƙarar . sannan yasa a tsananta binciken case ɗin duk faɗin Lagos dama kewayenta ya kuma yi musu albishir ɗin kyauta mai tsoka, muddin suka samo masu hannu acikin case ɗin. Abinka da manya nan da nan suka bazama don sosai ya mugun sakar musu kudi masu gwaɓi, tako ta ina jami'an tsaro sun ɗau zafi sosae kawunansu ya ɗauki ɗumi. Kan kace me maganar tayi spreading kamar gobara a bushashshen ciyayi.

Gidan su Meerah sosae hankalu suka sake tashi ganin malam Abdullahi yana a mugun yanayi,ga Amma dake hospital har yau bata san inda kanta yake ba. Sai wasu siraran hayawe da suke ɗan zubo mata time to time sosae likitoci suke iyaka bakin ƙoƙarin su akanta.

Sai dab da Asr Amma ta farfaɗo abu na farko data fara nema itane Meerah.

"WHO WHY su waye ? Su waye masu son rabani da hasken rayuwata! Su waye ku? ¿"

Dr nimra dake tsaye tun farkon farkawar Ammance ta shiga bama Ammn baki akan ta kwantar da hankalinta. Sadda kanta kawai ƙasa not saying anything saidai ita kaɗai tasan irin halin da zuciyarta take a ciki da irin ɗacin dake danƙare acen cikin tsakiyar ƙirjinta. A hankali ta maida idanunta ta lumshe tana haɗiye yawun daya tokare makoshinta, zafi mea mugun raɗaɗi take ji a zuciyarta ji take kamar ana gasa mata zuciyar a oven ne kuma a tarfa mata narkakkan Salman. Meerah ita kaɗai ce jininta daga ita Raiha sune suka maye mata gurbin yar uwa, ɗan uwa, UWA,UBA dangi baki ɗaya.

Su kaɗai ne hasken rayuwarta kuma sannan rana tsaka ace irin waɗannan muggan musifun sun faru da rayuwarta?. Ita da Meerah ɗin ta kuma har ake tunanin ma zata kwantar da hankalinta abin ma da bazai taɓa yi yuwa ba kenan. Ahankali ta maida idanunta ta lumshe tana jin yadda ƙirjinta yake mata wani mugun bugu tarkar ƙirjinta zai fashe zuciyarta ta fito fittt haka take ji.

Faɗowar mutum ajikin da kuka kukan da aka fashe mata dashi ne yasa ta san Raiha Raihan tace a jikin ta. Wani irin ƙanƙameta jikinta tayi domin gani take itama amana iya kidnapping nata kamar meerah'ɗinta. Ahankali ta shiga ɗan bugun gadon bayanta comfortably tana streaming abubuwan dasu faru da ita koma tace suke kan faruwar.

Malam Abdullahi da ya zuba mata idanunsa tun farkon shigowar su da Raiha ne ya ɗan shiga takawa zuwa gareta jiki a matuƙar sanyaya.

"Ita ƙaddara wajibatunce akan ko wane bawa kuma mumini mai iman domin Allah baya taba dorama bawansa kaddarar da bazai iya dauka ba. Kana ita kaddara da kike gani rubutacciya ce tun daga rabbis samawati! Me yasa kike ma taki ƙaddarar

kuka?. Idan muka sanya ma zuciyarsa mu nasibi da miƙa al'amurra ga Sarkin da shi kaɗai ne buwayi gagara misali sai kiga ya sauƙaƙa mana tarin ƙalubalen dake cikin makauniyar ƙaddarar mu. Ya kuma kawo mana mafita akan hakan cikin sauƙi!, Duk da zuwa yanxun nasan shuɗaɗɗan al'muran da suka faru ne shuke zeroying main naki. Ki daure ki daure ki daure kiyi haƙur AYSHATUL

MUBINA"

Ƙara ƙanƙame Raiha tayi a cikin jikinta tana jin inama inama inama ace, saidai tasan wannan inama ɗin ta barta har gaban gaban abada abadan. Ahankali ta shiga noding kanta tanayi tana ƙara ƙanƙame Raiha dake matse a cikin jikinta.

"Bawai ƙaddarata nake ma kuka ba Abbu maira tarin ƙalubalen dake tattare da ita nake ma kuka. Bawai kukan faruwar wani abu ba kukan ƙinnn.....

Sai kuma wani irin kuka yaci ƙarfinta irin mai sarke numfashin nan.

Hawaye taci gaba dayi tana sobbing ahankali tana jin raunin zuciyarta daya fara kamewa komai daya faru na dawo mata kamar yanxune komai ke faruwa.

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

NA MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page23&24

ROMANCE

BLACK MONEY

Treason

Strong love

Right

Women's travel

The Secret Society

Oppression

KIDNAPPER'S

Informants

DEEP

BEST LOVE

□□□

★★★★

Da Wani kallon ka shiga hankalinka Isa manu yabi salman dashi don ganin irin mayataccen kallon da yake bin meerah dashi, Kasan Keyarsa yadan shafo yana waskewa abinsa. Kallo daya tama mutanen dake tare da baffanta ta dauke kanta daga garesu tamkar bata gansu ba, duk da kuwa ta gane isa manu don ita ba mutum bace mai yawan mantuwaba.

A mutumce cikin salon girmamawa isa manu da salman suka shiga gaida Anne da tambayar me jiki.

"Jiki alhamdullih da sauki wllh"

Anne ta amsa itama a mutumcen kamar dai yadda suka gaida tan, ta dayan gefen da kanta yake salman ya koma don bai gama morewa kallonta ba.

"Baby ya saukin jikinki?"

Ta tsinkayi muryarsa me kama da anyi bari an kwashe, ba tare data ko kalli inda yake ba taja idanunta ta kulle abinta domin haka kawai taji ta tsani mutumin farat daya. Shima daga haka ya kama kansa domin be kamata ya fara bata aikinsu tun daga yanxun ba.

Sallama sukama su baffa bayan sun ajje katuwar ledar da suka shigo da ita, duk da baffa beso hakan ba amma be ya kyalesu kawai.

Kwananta daya da wuni daya amma daga gidansu meerah babu wanda ya leko da sunan dubiya bare taya Anne murnan bayyanar da tayi.

Hajiyar salman ma tazo dubiyar haka manyan yan siyasa suka dinga zarya a cikin hospital din domin nuna karamcinsu da girmamawa wa Isa manu.

Karfe biyun rana aka basu sallama lokacin baffa baya hospital din yaje gida, suna fitowa harabar hospital din wata rantsatstsiyar black Toyota Camry 2024 ta sha gabansu, duk tsaiwa sukayi a tare suna jiman moton ya wuce ya basu hanya su tari napep ya mikasu gida ga zafin rana da yake dakar ko wannensu. Kokarin kauce may suke ganin yaki basu hanya, sake shan gabansu yayi tare dayin qasa da glass din motar yana sakin murmushinsa me kama dana muna fukai tare da fitowa yana fadin.

"Mama barka da rana Ku shigo nine fa"

Yayi maganar yana kokarin bude musu Motan domin shiga, "0'oh ba ayi haka ba salman daga haduwa kuma sai dawainiya ai nauyin saiya ma yawa"

Amma ta fada cikin hakikanin gaskiyarta, Saida yadan saki wani shegen murmushi kafin ya furta. " Haba mama dawainiyar miye zaiyi yawan matar dazan aura CE fa Insha Allah "

Da sauri ta dago kanta tare da watsa mishi wani banzan kallo, domin ita sai yanxune ma ta tuna shi, tasha ganinsa a inda bai dace ba ta dalilin aikinta da irin aikinsu na jonalist (JARIDA) babu inda baya kai mutum. "Halan kai babu zuciya a kirjinka? Nifa a duniya na tsani mutum Mara fashimta OK"

Kin dauke nasa idon yayi akanta duk kuwa yadda take jifansa da muggan kalamanta hadu da mummunan kallon da take jifansa dashi, amma shi hakan bai dameshi ba saima sake watsa nashin da yayi cikin natan, hannun Anne ta sake damka tana yin gaba abinta, da sauri yasha gabanta cikin maraitacciyar murya ya furta.....Pls mana babe don Allah Ku shiga"

Tana kokarin sake Jan hannun Anne'nta ne taji annen taki biyo bayanta, ita kuwa annen ganin yadda hankulan mutanen dake compound din ne ya Sanyata tsaiwa chakkk. Da ido tama Merrah din alamar data kalli yadda hankula ya fara yowa garesu, kamar ance kalli side din dake damanki idanunta suka shige cikin nasa kyawawan idon, yana tsaye jikin wata mahaukaciyar baka wulik din Ralls rayce car yayi crossing kafafunsa yana buga games da tsadaddar waya abinsa hankali kwance cikin nutsuwa.

Wani irin matse hannun Anne tayi tare da dan mutstsikar idonta kadan waiko gizo ya mata, still dai shi din ne tsaye cikin shigar riga da wando na long sleeves sawayensa sanye cikin wasu hadaddun snickers shoe sai idonsa daya to she su da wani mahaukacin luxary shade. Amma hakan bai hanata gane shi din bane *AK* ta furta. (Me wannan abin yake anan?) Ta fada acen kasar zuciyarta.

"Didi wai kodai kin hadu da cutar kurumta ne?"

Anne data riga ta zauna a cikin motar ta jeho mata tambayar, da sauri ta dauke kanta a kanshi tare da kokarin sanya kanta cikin motar.

"Ashe kedin me arha CE haka ban sani ba tunda har zaki Iya shiga cikin ko wacce tarkacen shara right?"

Haka taji saukar wucewar kalamansa har cikin tsakar kanta dap da ya kawo kansa kamar zai wuce ne.

Ahankali ta saki murmushin daya kara kawata kyawun fuskarta a karo na farko tana tsayawa chark. Sai kuma ta dan tabe bakinta tare ta sakin wani murmushin takaici kafin cikin maganarta ta kai tsaye ba tare da jin shakku ko tsoron komai ba, Idonta cikin nashi ta shiga furta.

”Ai abu me tsadane yake birge kowa koda kuwa mutum yasan bazai same shiba yakan Iya tsayawa yayi tayi duk da yasan zaren ba kalan yadin bane, amma zeso ya dandali arziki yakuma bar arziki a inda arziki yake SBD farinjini halittane metarin baiwa wadda duk tsadar Abu seyanada farinjini yake birge kowanne halitta, just if u been a black stomach man ok tell me now but u are very amazing me for ur talked”

Tunda ta fara motsa lips nata ya zuba mata kyawawan idonsa, kafin ya saki wani shegen murmushin nan nashi da mutane kema lakabi da na mugunta.

A fusace ta shige cikin motar da Sam bata da ra'ayin Shiga 5 minutes da suka shude, harta shiga kuma ta juyo again. ”Remember kasani ayau zaka kara tabbatarwa mutum crismatic ako' Ina nadabanne kuma yanada wuyar samuwa” da karfin masifa ta buga murfin motor'n.

Wanda hakan ya sanya salman kwasarta a guje suna barin kurarsu.

★★★

Har bakin kofar gida salman ya kawo su Meerah,bakin baffa na zaune cikin barantar dake kofar gidanshi suna zaune da mutanen da suke karatu duk bayan sallar asuba da kuma isha'i, dake yau kuma ranar alhamis ce karshen sati duk alhamis din duniya sau uku suke daukar karatu. Da farko be kawo su annen bane saida yaga fitowar Annen kafin merrah ta biyo baya. Da dan hanzarinsa ya nufo su har wasu daga cikin mutanen na Mara mishi baya.

Shi da kansa ya dauki yan kayayyakinsu da basu da yawa bayan ya dada musu sannu, sallama sàlman ya musu yana cewa da baffa sent xuwa dare Insha Allah, sosae baffa ya dade masa godiya yana fadin. ”Allah ya kaimu min gode sosae”

Cikin gidan suka shige shi kuma bayan sun gaisa da jama'ar dake tare da Baffan, shi kuma salman ya dauki hanya yana barin cikin anguwar baki daya.

”Assalamu Alaikum!”

Anne da meerah suka hada baki wajen ma jama'ar dake zaune gaban bishiyar setline suna shan iska, amma tari babu Wanda yayi tsakanin matan gidan da kuma tarin yaransu. Saima hayaniyarsu da sukaci gaba dayi suda yaransu wanda ba'a raba gidanmu dashi.

Da gudu Affan daya fito daga toilet yayo wurinmu cikin murna sosae yana fadin. ”Oyoyo aunty meerah dinmu ta dawo bayan mamanmu tace bazata sake dawowa ba wai”

Wani irin fisgar hannun affan maman Saude tayi cikin fushi ta shiga sirfa masa masifa. "Ance ba zata dawo ba din dan ubanka, affan zanci ubanka a gidan nan wllh shege marar zuciya ban hanaka kula wannan yadin magen ba @ gidan nan”

Kuka yake yana ta kokarin kwatar kanshi daga mahaifiyarsa, wata uwar tsawa ta daka mishi tana jan hannunsa kiiiiiii suka shige daki.

Ahankali ta dauke kwallar da suka tarum mata, tana jin wani Abu da batasan ko miye shiba yana tokare kirjinta, tana bakin cikin irin wadan nan abubuwan da suke faruwa a rayuwar gidansu.

Daki suka shige duk kuwa yadda take jin kukan affan yana ta kuka yana fadin wllh saiya rataye kansa, tanajin sanda maman saude tana fadin ya rataye mana idan bashi da hankali. Da haka suka shige dakinsu kwanciya tayi ita kuma Anne zama tayi don ta huta.

***Bayan an shiga sallar la'asar affan dake labe yana ta faman sauke ajiyar zuciya, satab satab ya leko saida ya tabbar babu kowa a tsakar gidan kana ya fito tsakar gidan. Gyalen mamansa dake rataye a kan window ya dauka da gudu yabar dakin yana yin gaban bishiyar setline din tsakar gidan.

Gyalen ya cilla ya hada ya masa daurin azar gagi, turmi ya taka ya zira kansa cikin daurin azargagen da yayi tare da shure turmin da kafarsa. Ji kake zug kansa ya zuge.

Bacci tasha sosae Wanda har batasan iyakar shi ba, ihun maman saude shine ya farka da ita sama sama take jin ihun tana fadin.

”Jama'a Ku temake ni affan ya rataye kansa, Innalillahi wa'inna ilaihir raji'un! Wayyo affan, wayyo jama'a, yanxu dama Ashe da gaske kake rataye kan naka zakayi affan?”

Da wani mugun gudun bala'i na fito har inacin tun tube, kaff matan gidanmu suna tsaitsaye an rasa Wanda zai sinto affan. Hakan yasa na janwo drow din da muke tara ruwa na taka zan sinto shi.

Drow din da nake kai naji an ture da karfin masifa, ji kake *tummm*

na fado daga kan drow din.

”Shegiya mayya wllh kema saikin mutu tunda kece sanadiyyar kashe min da”

Sune kalamai na karshe da kunnawana suka jiyo min na tafi duniyar somewa.....kan kace meee gidan harya cika da mutane ko nace samarin gidan, jikin baffa kuwa rawa kawai yake don kowa a gidan ya shaida irin girman shakuwar dake tsakanin baffa da kuma affan din, Yaya Ibrahim ne ya sinto affan kan yay jale alamar a karye yake,wani irin kuka maman saude ta kece dashi ta fadi kasa tana mututuwa tana tunballo ta ratayo wuyan affan din tana kuka, Anne kuwa wani irin rumtse ido tayi tana jin wani irin dacin da bata San na miye ba na taso mata.

”Innalillah wa'inna ilaihir raji'un²”

Ta fada tana jin wani zafaffen hawaye na karyo mata.

Yaya Auwal ne shida Sapwan sukayi saurin Ciro affan daga jikin maman suna fita dashi don kaishi hospital.

”Ibrahim miye haka kuma zakuy? Kulli nafsin za'ikatul mauti! Dukkan mai rai mamacine saida muce ubangiji ya jikan Nasiru (Affan) ya kuma Sa mace tane”

Cewar baffa da baki daya jikinsa yayi sanyi, su kansu manyan hawaye zubar musu yake domin affan irin yaran nan ne masu azabar shiga rai, dadi da kari akwai shi da nutsuwa,hankali, biyayya Sam shi babu ruwansa da yadda tsarin gidan nasu yake duk da kasan cewar yaro me dan bazai zarce irin shekara biyar din nan ba xuwa shida.

Kan kace me makwafta sun cika gida harma da sauran yayan gidan aurarru duk sun iso, duk wannan fadi tashin da ake babu wanda ya sake bi takan meerah. Tana cen palon baffa da yasa Ibrahim ya maida ta cennnñ, bayan yayyafin ruwa da yasa aka mata ta farka amma alhamdulillah kuma ta sami bacci.

Cikin kankanin aka suturta gawar affan aka meka shi xuwa gidansa na gaskiya. Sisae ya sami jama'a kasan cewar Sa yaro na kowa, har a manyan masallatu da gidan radio aka sheda rasuwar.

Sai bayan sallar isha'i wajajen goman dare kana malan Abdullahi ya shigo, har xuwa lokacin kuwa meerah na palon Baffan, da kansa ya tada ta ruwan tea din da aka kawo masa ya hada mata da kansa, tare da bread saida ta wanko bakinta da fuskarta kana ta zauna tana tonkoshe kafafunta a gaban baffan.

Haka badan taso ba ta shiga tura ruwan zafin zuwa cikinta amma sammm taki cin bread din, xuwa lokacin idanunta sun fada sosae sunyi zuru² duk da cewar dama tana a halin jinya be. Maman Auwal CE ta shigo dakin da sallama kasan cewar itane da girki yau, wani mugun kallo ta wullawa meerah a fakaice tare da Jan kwafa.

Ita kuwa a tsanake ta mike tana ma maman Auwal sannu, ciki² ta amsa ta ita kuwa ta kwashi tarkacen tana yin woje bayan ta sake baffanta gaisuwa a karo na biyu.

★★★

Armstrong

Gurfane yake gaban manyan police din dake kewaye da dakin, jikinsa duk jini ya jigata iyaka jigatuwa.

Wata uwar tsawa dpo ya kwatsa mushi yana furta. "Tell me know zaka fada mana inda sauran suke ko sai yanke ma yatsun hannuwa?”

Dago kansa yayi Wanda yake sharkaf da zufa, kafin a galabaice ya dago ya dubesu tare da sakin murmushin daya kusan haukata zukatan police din.

“Wai kuna son na baku batu akan Boss ne¿”

Ya fada tare dabin su da jajayen idonsa, da badan boss yaki bashi dama ba da tuni ba wannan batun ake ba wani ake.

”who is ur boss master' who is he?”

Dcp ya fada cikin zafi yana cakumo wuyar rigar Armstrong.

”AK”

Ya furta cikin wani jahilin sautin daya sanya dcp sakinsa yana yin baya a mugun tsorace, jikinsa na wani irin mazari dpo kuwa wani irin yanka yaji zuciyarsa tayi. A kuma daidai lokacin manyan soldiers suka danno Kansu cikin babban dakin horaswas.

A zafafe Ajmaal ya wani irin cakumi wuyar rigar Armstrong hada shi yayi da jikin gini yana furta.

”INA YAKE?”

Hhhhhhhhhhhhh sautin dariyar Armstrong ya karade dakin kafin cikin wani sauti ya shiga furta.

”Ganinsa kawai kansa kafafu su dau mazari, zuciya ta fara bugawa tamkar kazar da tagaji ta kwanta a cikin mai sai gata a kafe. Kunsan waye AK kuwa?

_Shine mugun da yake lalata mugyayen kasa!!!, shine me tsince kazantar cikin al'umma! Kuma shedanin shedanun cikin al'umma, a shirye nake da in bada rayuwata ga *AK* wanda nake kallonsa a matsayin uwa uba Yar uwa Dan uwa”

Dogo kansa yayi tare da bin Ajmaal da wani dan iskan kallo hannunsa yakai gefen bakinsa dake disar jini ya goge, duk kuwa da cewar hannunsa na cikin handcuffs ne.

Cikin dangerous voice nashi ya furta.

”kodan sabo da mutuwa ta tai ma'ana shekeni!!!, zoka harbeni. Ko zaka rage radadin dake sukar zuciyarka domin shi kasan *BA YA MUTUWA*”

Wani irin damkar wuyar rigar Armstrong Ajmaal yayi tare da bashi wani mugun naushi a gefen fuskarsa, saida ya dan dakata kafin still ya sake damkar wuyar rigar nashi yana sake furta.

”Idan har baka fada min inda yake ba na rantse sena sheke ka kafin nabi ta kansa shima na karkkarya kasusuwansa a gaban idonka”

Wani shegen dariyar bazatane ya kwacema Armstrong.

”AK is too hard for me to break, diamond ne shi kafin a narka shi sai an yi amfani da ice da fire I have used the ice. Ta ya kake tunanin karamar kwakwalwarka ya gaya maka daidai? Ko dai ka manta *SARKI NE SHI A DAWA?*"

A matukar fusace Ajmaal ya daga bindigarsa ya dana akan Armstrong yana shirin d'ana kunamar binfigar nashi.

”Ajmaal stop!!!”

Mr president da shigowarsa kenan ya furta cikin rawar jiki, da dacin murya amma ina tuni Ajmaal yaaaaaaa.....

★★★

AK POV

Fitowarsa cikin takun nan nasa na isa da izza tamkar babu wani abinda ke damunsa ya saka uban guards din dake harabar gidan nutsuwa. Cikin Tsananin kwarjininsa da gizagon da kullum ke sanya zuciyar magauta nutsuwa, lullebe a akan kyakykyawar fuskar dake nan tamkar hadarin daya kunshi ruwa yaki ya fashe.

Sanye yake cikin ash wandon fendi da farar rigar rugby shirt sai blue Lorenzo snickers a sawayensa. Fuskar nan saye cikin Sun glasses sai nose mark daya sanya.

Da sauri daya daga cikin samudawansa ya bude masa wata shegiyar blue car 2024 Bugatti, Cikin tsantsan jin kai ya shige cikin motar rufewa yayi driver ya bata wuta, Sauran motacin na Mara musu baya.....

ISA MANU empire

Hannuwansa goye a bayansa baki daya kansa ya kulle yama rasa wanne tunani zaiyi, ”Dom ITT"

Ya fada cikin daga sauti. Wanda kuma yayi daidai da shigowar Salman a rike ce. Ganin yanayin daya tadda dad nashi ya sanya hankalinsa sake tashi over,Saida ya dan fesar da wani zazzafan numfashi kana ya furta.

"An dauke Assembly leader wayewar garin yau na Serevellar”

“What!?”

Isa manu ya fada da karfin masifa tare da kaiwa kasa yana fidda numfashin da yaso sarkeshi sama².

Komai bai Iya furtawa a lokacin saida ya debi wasu minutes kafin ya furta.

“Lallai yau duk yanda za'ai ina bukatar ayi zanga zangar nan, Kaiiiiiiii abin yayi yawa haka nan, nasan next target nine kuma ko kai”

Yayi maganar zuciyarsa na wani irin beating very fast.....

Cikin abinda bai gaza 50 minutes ba gangar samari yan ko ta kwana suka gama hallara kansa a babban gidan gonar Isa manu.

By AMMEY LAYLERH□□

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page 25&26

ROMANCE

BLACK MONEY

DEEP

BEST LOVE

★★★★

5:55am

Cincirindon matasan suka zagaye babbar police ɗin dake birnin Lagos da kuma headquarters na sojoji, Suna faɗin *ADALCI* suke so. Su a fito musu da gwamnansu tare da ministan su da assembly leader nasu.

Wannan zanga-zangar ta matasan ce ta kuma janyo hankulan jama'a kansu, dan danan cikin mitsitsin loƙaci jama'ar gari suma suka firfito ana zanga-zangar dasu, kafin kace meye Social media ma ta ɗauka.

Suna son soldier's da police's su jajirce wajen dawo musu da governor da minister'nsu tare da Assembly leader, Tuni wannan zanga-zangar ta yau lanar Laraba ta zama latest a kafafen yaɗà labarai. Irinsu magazine, Television, Radio.

Su Isa Manu da suke cikin gidajensu suna kallon duk abinda ke faruwa tuni suka cika da maɗaukakin farin ciki, lallai haƙarsu ta cimma ruwa dama abinda suke da buƙatar kenan. A tada hazo a cikin garin na Lagos dama kewayenta.

Acen kuwa cikin babbar police da kuma headquarters ɗin kuwa duk da barkonon tsohuwar da aka baɗesu dashi sunƙi ko gezau balle su gudu. Ga na cikin gari ma

hakan take dole yɑn sanda dama sojoji suka bazu ko ina don bada tsaro wa al'umma.

****

MEERAH

A Yau Lahadi akayi adda'ar sadakar ukun Affan wanda har zuwa wannan loƙacin meerah na'a cikin alhinin mutuwar.

Daren daya kasance dare mafi matuƙar muni a cikin tarihin rayuwar meerah, domin Sai yanxun mutuwar Affan ya dawo mata sabuwa fillI. Domin sai yanxu ta sake tabbatar da cewar ehhhhhh lallai ta yarda ta rasa Affan ɗin ta har gaban abada abadan abada kenan, A wannan dare na sadakar ukun ta kasa rumtsa kwayar idonta shi yasa ta ƙira daren da baƙin dare.

Dare ne mai ɗauke da tsananin duhu tare da cushewar yanayi kasancewar babu yalwar iska ko kaɗan dake kai komo acikin gari, yayinda sama tayi duhu dulum kasancewar babu hasken farin wata ko ɗigo, haka ma hasken taurari duk sun disashe wannan yana ɗaya daga cikin abunda yasa duniyar tayi mata tsananin duhu, yayinda ko ina ya zama shiru babu motsin kowa a cikin gidan sai ita kaɗai da take kowawa da numfashinta. kasancewar adaidai irin wannan loƙacin kaso 90 acikin 100 na mutanen duniya bacci sukeyi, saboda kowa yasan akance *DARE* mahutar bawa.

Saidai awani ɓangare tsawon awanni ashirin da bakwai kenan da MEERAH ke kokawa da numfashin dake shirin barin gangar jikinta.Luuuuuuu idanunta suka rufe kirib, yayinda bugun zuciyarta ya yi ƙasa sosai kasancewar ta jima da fita acikin hayyacinta, wannan yasa ta shafe tsawon awanni 30 batare da tasan

duniyar da take ba, ta manta wacece ita da kuma duk wani abu daya shafe ta, ta manta da Cewar an taɓa halittan wata jinsi irinta, komai ya tsaya mata ne cak kamar ba’a taɓa wanzar da ita adoron duniyar ba.

Ammma sai' gashi cikin hukunci na Ubangiji maji ƙan bayinsa cikin ƙarin wasu awanni, numfashi ya fara ziyartar wannan kirjin daya jima ba tare da ya shaƙi numfashin duniya ba, wanda hakan yasa ahankali ta soma motsa babbar yar yatsar ƙafarta wacce ta ƙame waje guda, A loƙacin da numfashinta ya gama daidai ta a kuma wannan loƙacin ne wani irin ɗaci da ciwo me gigita zuciya ya ya sake sarƙafe tsaƙiyar ƙirjinta.

“MEERAH?...”

Amma ta ƙira sunanta cikin sautin fitar amon daya sake gigita duniyar Meerah, wanda tarin ƙalubalen da take kan fuskanta ke haifar mata, wani irin rumtse idanunta tayi tare da matse hannuwanta dake rawa sosae. Wani irin mashahurin sanyi na ratsa cikin jikinta.

Da sauri Anne ta ƙarasa shigowa ganin kamar Didinta bata a mood me daɗi, domin yau ita ce da malam Abdullahi haka kawai jikinta ya bata Didinta ba lafiya ba. Zaune takai gefen gadon da take kwance. Wata guntuwar kwalla data tarummata ta share zuciyarta na mata suya.....

Shin sai xuwa yaushe zata dena zubar da hawaye akan ƙaddara?

Shin yaushe ne babin rayuwar su zai juye zuwa wani mataki na daban?

Shi sai xuwa yaushe rayuwarta ita da yayan ta zatayi haske? Yaushe zasuji daɗin rayuwa ita da yayanta kamar ko Rai me numfashi?, Yaushe haske zai ratsa cikin rayuwar kowannensu?

Shi dama laifi ne dan ƙaddararsu tazo musu a yadda ba suyi zato ko tsammani ba?, Ashe haka duk wata ɗiya ta kwarai take ji idan aka shegentaka? Wani irin ɗaci da raɗaɗi me zafin gaske take ji a duk loƙacin da kishiyoyinta suka jefeta da kalmar shegiya

_Bafa ita ta zaɓama kanta tasowa a inda babu kowa nata ba! Bafa zaɓen ƙaddararta tayi, ba itace ta zaɓi da rayuwa tayi ta watan gaririwa da itaba, ba kuma itace ta tsara ma kanta yanayin rayuwar da suke ba. Ta buɗe idontane kawai ta ganta inda bata san kowa nata ba, ba UWA ba Uba, ba yar uwa ba ɗan uwa.

Babu kowa nata data sani itama tsintar kanta kawai tayi a cikin rayuwar da take a yanzu tsumu-tsumu, Tana ƙara roƙon Allah har kwanan gobe Ubangiji karya ɗauki rayuwarta saiya bayyana mata wani nata a duniya....._

Tana son ta tambayi wanne irin laifi ta musu da suka zaɓi su jefar da ita? Tana son ta tambayi wanne irin mutane ne su masu son zuciya?

_Ita kaɗai tasan abubuwan da suke cunshe a cikin Rai da ruhinta, wanda suka kusa tarwatsa zuciyarta ta buga ta dena aiki, domin tasan tana dab da bugawar.

Badon Allah yayi ta mace me tsananin haƙuri da danne abu komi girman sa a cikin zuciyarta da tuni numfashinta ya jima da barin gangar jikinta.....

A bayyane ta sauƙe wata nannauyar ijiyar zuciya cikin muryan da yayi low sosae ya furta.

"Me yake damun DIDINA haka?"

Kanta ta ɗago tare da kallon mahaifiyar nata cikin raunatacciyar murya ta shiga faɗin.

”Nima bansan abinda ke damuna ba Anne! Kawai dai inajin yanayin cinkushewar zuciya ne, da rashin jin dadin yanayin rayuwar ma baki ɗaya”

”Ce ALHAMDULILLAH domin Allah shine abin godiya a koda yaushe!”

ALHAMDULILLAH ɗin kuwa ta furta tare da duk sauran adda'oin da suka zo mata.

Kiran sallar asuba da aka ƙirane ya fitar da Anne a ɗakin bayan taci kukanta harta gode Allah.

Ko Washegarin ranar Meerah kasa fita ko ina tayi, kayan karin tama har ɗaki Raiha ta kawo mata.....ita kuma ta wuce makaranta.

Tana zaune a ɗaki Sai wajajen sha biyun rana kana ta fito verander inda yan uwanta aurarru suke zaune. Gaisar dasu tayi wasu sama sama suka amsa wasu kuwa arziƙin kallo bata samu daga gare su ba.

Kwanciya tayi ba tare data nuna damuwarta akan rashin amsanta ba basu yi ba.

Babbar yayarsu da suke ƙira aunty Zaheedah ce tace.

”guys na manta ban baku wani latest story ba"

Shewa suka sanya a tare kusan su biyar kana aunty Sumayya ta furta.

”Bamu musha yer uwa”

Saida tayi yar dariya kaɗan irin ta rashin mutuncin nan kan furta.

“Kai Wllh na daɗe banga mara zuciyar mace irin zulaiha ba, Ata zaluntar mutum amma saiya nuna baimasan ana yimay ba. Kunsan a wayewar garinda Affan ya rasu sai dana sake banka musu ɗaki ita da Belle"

”Kai Wllh na daɗe ko'a littafin Hausa Novels banji me hali irin na matar nan, ayi yarinya sai kace me zuciyar takarda ko ma wacce bata da zuciyar a tsakiyar ƙirjinta”

Aunty labiba ta faɗi tana gyara zama

"Nake baku labari shegen kamar kullum ranar ma kasa tanka min yay saima rawar jikin daya fara min..... Ita kuwa shegiyar Wllh ko kallo na kasa yi tayi kamar dai ko yaushe”

Aunty Maryam da tunda suka fara maganganunsu ce dama kuma bata ce musu komi ta furta.

”Innalillahi! Yanxu dama har yanzu Zaheedah baki dena wannan banzan halin naki ba?, Na cutar yarinyar mutane ta shigar mata ɗaki kina gane mata sirrin aurenta.....Wllh kiji tsoron Allah domin ɗaurin talala ya miki duk randa Ubangiji ya tashi nuna miki ikonsa a kanta Wllh daga ranar zaki gane Allah ɗaya yake”

"Huyummmmmmm me zuciya irinta marasa kan gado, ke dai kici gaba da zama a cikin duhun kai da bar abada bazaki waye ba"

Cewar aunty labiba, shewa suka sanya mata nan fa suka koma kanta suna mata cin mutuncin da suka ga dama.

Ni kuwa dake kwance a wurin tsammmm na miƙe domin kunnuwa ba rasuji gaba da jin zunufi ba. A cikin zuciyata kuma ina musu fatan shiriya duniya da lahira.

★★★

ABUJA

Zaune take akan caution ɗin da yama ƙatataccen parloun ƙawanya, tayi zurfi sosae a duniyar tunanin halin da rayuwarta take ciki.

Tana zaune cikin ƙunci na rayuwa da azabtar War kishiya.

”Zulaiha! Zulaiha!!"

Shiru alamun tayi nisan kiwo a cikin kogin tunanin data faɗa.

”Zulaiha kodai kin sanya wata damuwar ne a cikin ranki?”

Matashin mutumin dake kanta tsaye ya tambaya wanda a shekaru zai iya kaiwa irin Talatin da bakwai ɗin nan ko da shida.

zamanta ta gyara tare da fuskantar sa sai kuma idonta suka ciko da kwalla.

”Yanxu Bello tambayana ma kake ko damuwar woni abu nasa a raina? Duk irin ƙalubalen da nake fuskanta a cikin gidan nan?

Haƙuri na yana dab da ƙarewa Wllh na gaji- na gaji *NA GAJI BELLO!* Duk irin abubuwan da ake min woni a gaban idonka woni a bayan idonka amma kanzil ba zaka iya furtawa akan anyi min ba daidai ba”

Ta furta cikin muryan kuka sosai da sosae.

Kafaɗunta ya dafa cikin kwantar da murya ya shiga furta.

”Har abada ba zan gaji da cewa kiyi haƙuri ba zulaiha, ita rayuwar duniya ɣar haƙuri ce kuma duk wanda yayi haƙuri baya taɓa faɗuwa ƙasa....Ƙarshen ko wanne haƙuri nasarace, ƙarshen tsanani darajace, ƙarshen wahala ɗaukakace, ƙarshen jarabawa kuma Alkhari ne ciki gaba da zaman haƙuri dakai kukanki wurin Allah domin shi maji ƙan bayinsa ne"

Daga haka ya saki kafaɗunta yay taku ɗaya ana biyu ta riƙo hannuwansa, Sai kuma kawai ta faɗa jikinsa tare da cusa kanta cikin ƙirjinsa rana fashewa da wani irin kuka me cin Rai.

Tsammmm ya rungumata ya fara lallashinta,Saman sa ya nufa da ita tana cikin jikinsa.

★★★

Ayau wayar garin litinin zazzafan martani ya fito daga bangaren *AK* Wanda indai mutum masoyin media me to da wannan zazzafan latest news din ya karya.

Ga abinda martanin ya kunsha na farko a cikin tiktok.

Yana zaune a wani kayataccen palo ne wanda Wanda ya wadatu da komi na mo re rayuwa, sanye yake cikin shigar bakaken Riga da wando yayi covering duka jikinsa ko kwayar idonsa babu me Iya gani.

Shi kanshi video'n don ka tabbatar dana musamman ne idan ka shiga kafin ka fara ganin komai said kamar 5 minute haka xuwa 7. Kafafun nan a harde kamar kullum cikin nutsatstsen sautin da yake fita cikin wani irin low voice nd sweet ya shi fara mayar da martaninsa kai tsaye.

Fusata ya kamata ace kunyi bawai nuna fushinku a kaina ba!. Kasancewar kun gane wannan shugaban da kuka zaba ha'intarku yake yi, akanshi ya kamata ace kun nuna fushinku sakamakon zabarshi da kayi

_A yayinda fitilun titi suka dauke hanya ta cika shara da kuma tarkace,

A yayinda ake wulakanta talakawa tamkar dabbobi a asibitin gwammanati!, cin hanci ya wanzu a kowanne ofishin ma'aikacin gwammanati anan zaku nuna fushinku.

Me yasa ba baku nuna fushinku fusatarku a ire-iren wadan nan abubuwan?, amma a yayin da gurbataccen shugaba ya shigo hannu shine kuka harda fitowa wata zanga zanga?

Kukayi kone-kone kuka har gitsa komai da komai a cikin ko wanne lunguna na wannan gari dama wajen garin?.

Idan har wani iftilati ya faru daku ya kasance kuma kuna bukatar taimakonsu to amfani Duke wannan hatta shi wannan taimakon Right?.

A wannan kasar shima talakan ba wani salihin bawa bane, shine ma hanya mafi gurbata a wannan fannin.

Rashawar dake tattare da kuri'a itace ke bama shugabanni wannan ikon.

A yayinda da suka zo suka raba muku wasu yan tsirarun abubuwan amfanin yauda kullum da bazasu wuce wuni daya ba.

Shine kawai kuke zabarsu ba tare da tunanin menene abinda gobenku zata haifar muku ba.

Sabo da rashin sanin yanci zarmammun cikinku suke dauraku akan ra'ayin da ba naku ba, domin kasa ta sanja dole sai talakan gari ya fara sanjawa domain kawar da rashawa da kuma son zuciya.

*DON HAKA MU FARA SANJAWA.....*_

Kafin kace mene tuni media ta dauki hayakin bala'i domin wannan zazzafan martani na ABDOUL-MALEEK AK tuni ya baza ko INA.

Har wasu na mai dashi rubutu ta hanyar copy suna dorawa irinsu Facebook, Twitter, Instagram, telegram dadai saurinsu haka gidajen radio suma suka ringa

maimaichin abun kamar ba gobe. Sai yanxu hankalin mutane ya fara dawowa jikinsu.

Tuni hankalin jami'ai kuma ya tashi da wannan ballo ruwa da AK yayi Wanda suka rasa ta inda zasu toshe hakan. Hankalin duk wani Dan siyasar dake Nigeria a tashe yake da ganin wannan video, tuni jamaar dake kiran AK da criminal suka dawo girmama koda jin sunan shine. Saidai amsa daya da ko wanne mutum ke dokon jira a jirace shine bayyanar ak a zahirance. Da kuma asalin kasar shi da inda yake zaune domin kuwa kallo daya mutum zai yi masa yasan cewar shiba mutumin NJ bane, ko daga yanayin zancenshi da baya idasa fita duka.

Wannan Abu shine yayi sanadiyar takawar shugaban kasa har xuwa Lagos. Inda suka tattauna da manyan Jami'ai da kuma wasu kuso shin gwommanatin dake mulkarmu ta karkashin kasa.....

Meeting din gaggawa suka shirya tsakanin masu ruwa da tsaki a cikin tafiyar.

After like 50 minutes haka suka shirya meeting ɗin gaggawa cikin wani haɗaɗɗan building mai haɗe da wani ƙaton hall acikinsa, coutions ne acikin sa na alfarma wanda hall ɗin yaji kayan mo re rayuwa, ko ina stainding A/C ne manner a wurin sai sanyayyar ƙamshi da kuma fitar numfarfashin jama'ar da wurin ya tara ne ke tashi.

meeting sukayi me sunan meeting Dan sai dab da magrib suka tashi suna ta faman kulli da warwara, ahaka har suka sami mafita kana kowa ya kama gabansa bayan zaida mafitar da suke ga itane kadai mafitarsu.

Kwanan Armstrong hudu AK yayi dirar miki a boyayyen wurin da suka boye shi ta hanyar footage din dake cikin karkashin harshensa.

Tsaro sosae akama wurin duk don kaicema samin kuskure,amma hakan bai hana ak bayyana a gabansu ba. A lokacin su Mr President, Ajmaal, Isa manu, dadai sauran manyan kawunan suna a cikin setrest din ne don sun fitar dashi a station din ma baki daya.

Suna kan azabtar da Armstrong Woyar dco ne yayi kara hakan ya sanya shi dakatawa da bugun Arms din.

”What AK kuma?”

Ya fada a zabure har yana kokarin hantsilawa saida Ajmaal yayi saurin taro shi tu kuna ya daidaita tsaiwarsa.

Wani matsiyacin kallo Ajmaal ya jefawa arms.

”Ta Yaya yasan kana a wannan boyayyen wajen?”

Ya fada yana shakar arms din.

Wata shegiyar dariya arms ya saki tare da furta.

”Ku a dakikin tunaninku da kunyi haka ne don boye ni daga BOSS?”

Ya fada cikin wannan dangerous voice din nashi.

”ANSWER MEE ARMS!”

Ajmaal ya sake maimaitama arms tambayarsa.

Dariya ya shiga yi kafin ya furta ”footage”

”Karya kake arms babu camera a jikinka nida kaina nayi check out naka!, don haka ka bani amsana a karo na karshe”

”Shi yasa na CE duk cikin Ku babu Wanda Zan kira da *JAN WUYA, duk kaninku ”KOLAYE NE”

Ya fada yana daga harshen Sa tare da sanya shi tsakanin seen da tongue nashi ya turo musu Yar karamar camerar.

Duk cikin su babu Wanda be razana da wannan basirar tasu ak ba. Ehhhh dole suce basira mana amma sai suka waske abinsu....

Few minutes

Zaune yake zama irin na harde kafar nan. Akan kujerar da Isa manu ke kanta a da a yanxu kuma ta dawo da ak din.

Fuskarnan tamkar tayi aman Wuta tsabar tsananin fusata,A fusace Ajmaal yayo kan ak duk kuwa da yadda Mr President ke kokarin hana shi amma be hanu ba.

”Kaida kazo da sunan kwatar yaronka to kasani kazo nan da sunan mutuwarka ne!,, A wannan rana a kuma nan wurin idan har ban dagarzaga kasusuwanka to na rantse ni ba namijine”

Wani Dan iskan kallo da ak ya watsawa Ajmaal ne ya sanya jikin Isa manu ya soma karkarwa,shi da ba shi aka ma kallonba.

Wani irin gyara zamansa yayi ya sakko da kafarsa daya dayar kuma ta na kan kujerar da yake kai. Ya dora hannunsa saman kafar like irin kasaitaccen basaraken nan.

”Ko wane mafarauci gwarzone har sai sanda ya fuskanci ingarman zaki. Ba kamar kai da rundunar jami'anku ba!, bana da runduna bana da tsoro a jikina bare naji tsoron mutuwa.

*TUN A HAIHUWATA NACI GALABA AKAN MUTUWATA_*”

Ak ya furta kalaman tare da wani iriin doka hannunsa akan kujerar da yake zaune a kai. Kalaman da suka kusan zauta yar karamar kwanyar duka jama'ar dake setrest din.....

A zuciye wani da suke kira da tonfal babban yaron su Isa manu yayo kan ak, da wani irin salon daukar hankali ak dake zaune ya sanya kafarsa tun kafin mutumin ya karasa ya sarke kafarsa. Ji kake rigifff mutumin ya zube kasa ba tare da ya ko motsa ba.

Cikin kankanin lokaci ak ya sissince arms dake daddaure ya tafi dashi a gaban idonsu ba tare da sun Iya dakatar dashi ba haka suna ji suna gani ya sabi arms a kan shoulder nashi yabar wurin dashi.cikin wannan takun NASA me cike da bajinta,hadi da mazan taka Wanda kallo daya idan kai masa sai hantar cikin ka ta kada.....

”Kai wannan yaro anyi dan tsinanne, kasa sai kace ta uwarka kazo ka zame mana fitina tare da hana mu rawar gaban hantsi”

Isa manu ya fada bayan daya tabbatar ak dade da barin wurin.

Ajmaal da gefen kunnansa ke digar jini ne Wanda ak ya bashi rabon shi. Cikin tsanin bacin ran ya furta.

”Stoppp”

Da karfin masifa ”Na gaji dajin koda me irin sunan sane”

Sai kuma ya dago ya kalli Mr President ya furta.

”Sorry sir. Duk ba laifinka bane da alokacin da na d'ana kunamar bindigata baka tsayar dani ba ai da tuni saida wani bashi ba!, amma ka dakatar dani”

”Babu dai kai ba shiba!”

Tonfal ya fada Wanda babu jimawa ya farfado daga mutuwar wucin gadin da yayi.

”More bit never get one choice but if we take a maximum change we get a big choice”

Mr President ya fada yana gama fadar hakan ya fice a wurin...

A lokacin da akai wannan darbarwar salman yana kasar India yawan shakatawa tare da wayayyun yan matansa.

★★★

”Mommy Wllh duk inda yake a fadin duniyar nan saina dau fansar Jinin mahaifina da yayi, sai nayi sanadiyar barin numfashinsa da gangar jikinsa kamar yadda yaso raba nawa mahaifin da nashi!”

FAROUQ AUDU BASHASHA

kenan da ga audu bashasha shi kadai ya haifa a duniya.Shi yasa yaron ya taso cikin wani irin sangarta da tabara, Duk inda ake neman wani teteros to in akace maka Farouq fakat kenan. A yanxu haka Audu bashasha yana kasar India wurin kwararrun likitoci don kula dashi.

Ashe be mutu ba da sauran ranshi lokacin da ak ya fasha kansa, Sun boye hakan ne domain gudun bacin sunan Sa, shi da kansa shine ya dauke RIYYA, ya mata wani irin mugun boye mahaifiyarsa kuma irin muta nan ne da sammmm babu ruwansu da duniya. Itace ma dalilin daya sanya ta hana.

Cikin muryar da yake cike da tsantsan sarauta Hajiya Khadija suraj sunusu shureim ta dubi Dan nata Tare da furta.

„Idan har Jinin dake gudana a cikin naka Jinin nawa to ban amince maka ba”

Ta furta hakan tare da bar masa palon, shi kuma ya bi bayanta da kallo domin duk wani Iya shegensa da ji da samartaka da zafin kansa jinsa yake shiba komai bane a gaban hajiya Khadija.

Ya ta biyu kenan ga me martaba sarki suraj sunusu shureim.

BY AMMEY LAYLERH

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~□ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... □~*

Page 27&28

ROMANCE

BLACK MONEY

DEEP

BEST LOVE

□□□

★★★★

2 months ago

Haka dai al'amurra suka ci gaba da wakana. Tuni baffa ya kashe waccen maganar haka kwanaki suka ci gaba da juyewa zuwa satikai satikai sukaci gaba da juyewa zuwa watanni.

Cikin iko na Ubangiji meerah ta koma bakin aikin da ko a mafarki ba tayi tunanin komawa ba, Bisa matsawar MD da kuma wasu manyan anguwanni ta koma bakin aikin ta.

Haka kuma maganar aurensu da Salman yake neman kan kama, Wannan abu shi yafi komai ɗaya hankalin meerah matuƙa saidai tana danne hakan a ranta.

Kusan kullum yanzu shike zuwa har ƙofar gida ya ɗauke ta zuwa wurin aikinta saidai ta dakatar dashi first.

A tacen ɓangaren su Salman kuwa wasu irin abubuwa suke ma shirye shirye shida mahaifinsa Isa Manu.

****

Yamma ci ne mai daɗi haka kuma yau din rana ne da ya kasance na musamman wato Jumma'a, ranan da yake ɗauke da albarka da kuma rahamar Ubangiji kala kala.

Wannan dalilin yasa sassanyar iska mai cike da tsananin daɗi da kuma sanya shauƙi ke busawa, a gaba daya ko wani lungu da saƙo dake cikin gidan jaridar zamani TV

Kowa ka kalla harkar gabansa yake cikin tarin nutsuwa, amma banda meerah da tayi zurfi a cikin duniyar tunanin data jima ta faɗawa.

"MEERAH!"

"MEERAH!!"

Disha dake tsaye kanta ta shiga ambata tana me ƙoƙarin rataya handbag ɗin dake hannunta, Wanda kuma ahankali ta ɗan ranƙwafowa da kanta, tana me kallon Meerah.

"MEERAH wake up kodai bacci kikeyi ne?."

Disha ta faɗi tana me gyara tsayuwanta, tare kuma dasa hannu ta zunguri meerah ɗin.

Ahankali ta ɗago kanta wanda ta kifashi akan desk almost 15mn ago.

Sam ba bacci takeyi ba hasalima duk abunda ƙawar nata ke faɗa tana jinta.

Numfashi ta ɗan sauke Ahankali tare da ɗago manya manyan eyes nata me kama dana mashaya masu matukar kyau, Wanda hakan ya sake bayyana tsananin kyawun dake kwance akan fuskarta, Idanunta da suka ɗanyi blue ta lumshe tare kuma da buɗe su aloƙaci guda.

Cikin unique voice ɗin ta mai daɗin amo da sanyin sauti, tamkar ana busa sarewa tace.

"What happen DISHA? ba bacci fa na keyi ba, just I'm tired."

Ta ƙare maganan tana ɗan kwantar da wuyanta gefe.

"What happening kike tambaya? time ɗin tashi a aiki yayi, kalla ki gani babu kowa ya watse sai nidake kawai, oya tashi mu tafi kodai zaman wurin ne bai isheki ba?."

Disha ta faɗi tana ɗan hararanta tare da yin gaba.

Fuska meerah ta ɗan kwaɓe kana cikin yanayin gajiya da kuma tsananin damuwar dake cinkushe a cikin ranta ta miƙe itama. cikin sauri ta rufa mata baya tana me ƙoƙarin rataya jakanta bisa shoulder nata.

Atare suka fito compound ɗin, tafe suke suna fira sama sama abinsu.

"Disha a raina inajin ina gab da ajje wannan aikin nake ga"

Meerah ta furta cikin cushewar yanayi.

Dafa kafaɗarta disha tayi cikin sanyin jiki ta furta.

”Haba meerah komai yayi zafi maganinsa Allah, ki barwa Allah komai Insha Allah shine maganin komai”

"Hmmmmmm!"

Ta sauƙe ijiyar zuciya me ɗan ƙarfi haka suka ci gaba da tafiya har suka fito gefen titin. Napep suka tara suka hau suna mai kwatancen anguwar da zai kai su.

Ko a cikin napep ɗin ma wata sabuwar duniyar tunanin ta ƙara faɗawa. Na irin daskararriyar K'addarar dake kwance acikin jininta wacce ta fara motsawa kanta.

Haƙiƙa akoda yaushe rayuwa tana tafiya ne tare da tarin ƙalubale.Haka kuma kowa da salon nashi Kalon ƙaddarar amma nata ƙaddarar gani take yafi na kowa, domin daga ta fita daga wannan sai kuma wannan ya kutso kai.

Kamar kuma yanda yake a bayan kowani baƙin ciki akwai farin ciki, haka kuma a bayan kowani kunci akwai sassauci. rayuwa mai juyawa ce farinciki ko akasin haka mummunan ƙaddara ko akasin haka, wayewar garin yau sun waye shine da maganar kawo kuɗin aurenta da iyayen Salman sukai har Naira miliyan ɗaya. Wanda ya tashi hankalin jama'ar gidansu, suka wuni zazzaga ruwan bala'i da masifu kala daban daban.

Ita kuwa wacce ake yi ɗin dan ita sammm ba abinda ke gabanta kenan ba. Wani abu ne daban ke damun rayuwarta wanda da tayi ƙoƙarin zurfafa kanta yake neman juyewa zuwa wani ɓigiren na daban.....

Cikin nisan da tayi a duniyar tunani har suka isa ƙofar gidansu bata ma san sunzo ba, Saida disha ta mata magana da ɗan ƙarfi kana tayi firgigit ta dawo hayyacinta Cikin duniyar mutane bata tunani.

AK

Msalin ƙarfe biyar na yamma manyan motocin Ak dake cikin garin Abuja suka ma airport ɗin tsinke.

Wasu irin zafafan motocin kusan goma sha biyar irin su Range Rover, Bugatti Veyron, Toyota Highlander, Toyota Tacoma, Ferrari California,gefe ga wasu mahaukatan manyan jifa jifai har guda biyar da aka ware su baƙaƙe wulik dasu. motocine a wurin babu colourn da babu shi kansa airport ɗin kewaye yake da tsaro na musamman.

Ahankali cikin takun izza dajin kai ya fara tako matakalar benen.

Su kuma samudawan sa na aikin su na take mai baya, cikin sauri manyan security'n dake zagaye da airport ɗin suka shiga bashi kariya wa kallon da jama'ar airport ɗin ke binsa dashi. Don kuwa kallo ɗaya zaka masa ka kasa ɗauke idonka a kanshi. Sanye yake cikin Wani arnen cashmere valley wanda kallo ɗaya zaka ma yadin ka tabbatar da ba karamin kuɗi aka narka wurin siyen shiba...

Ahankali yake taka Fararen sawayensa da tamkar wanda bai taɓa takasu ba haka suke, don tsananin taushi da kuma yadda suke sumil luwai.

Wata kafurar Black blue ɗin Mota ƙirar Mercedez Benz aka buɗe masa Armstrong kuma ya faɗa cikin wata narkakkiyar bakar jeep Wrangler . Suka ɗauki hanyar wannan haɗaɗɗen Hotel ɗin na da sukayi booking tun a daren jiya.

Dake babu wata tazara tsakanin support ɗin da kuma Hotel ɗin babu nisa cikin 25 minute suka isa ƙaryataccen hotel ɗin.

A room me lamba 105 AK ya ɗauka su kuma duk suka rarrabu daban daban.

Kwance yake acikin bathtub dayake cike da ruwa masu tashin qamshi na musamman, Iyaka kanshi ne a waje ya lumshe idanuwan sa ya faɗa duniyar tunani me zurfi, wanda nake da tabbacin ya mantar dashi a duniyar dayake yanzu haka.

ya jima sosai acikin ruwan wankan daga bisani ya wanke jikinsa ya fito towel blue ɗaure a jikinsa.ga kuma wani mini qarami a hannunsa shi kuma kalar light blue yana tsane gashin kansa dake cike sosai baqa wuluk! lotion ya shiga shafe jikinsa dashi tsadadde ya gyara tulin gashinsa da mayuka masu kyau da tsada.

Kayan da aka rigada aka ciro masa ya ɗan kalla a takaice dogon wandon jeans ne blue da shirt fara qal me asalin kyau an mata zanen Lion ajiki da blue din colours, sanya kayansa yayi kafin ya fito zuwa balcony na room ɗin. Hannuwansa zube jikin wandon jeans ɗin. Wurin ba hayani sai sassanyar iskan dake kaɗawa mai cike da tarin ni'ima sakamakon hadarin da yayima sararin samaniya ƙawanya.Hakan yasa garin ya yi luf ga dukkan alamu akoda yaushe a ko wanne loƙaci ruwan sama kan iya sauƙa.

Yana zaune kan Chiar silinder caution ɗin dake cikin balconyn Wata ƙatuwar Toyota land cruiser Prado ta shigo harabar wurin fara ce kal sai faman kyalli da ɗaukar ido take yi.Wurin da aka tanada dan adana motoci motar ta parker,cikin slow mamallakin motar ya yi parking.

Kasancewar glass ɗin motar tinted

ne yasa ba'a iya hangen mai mamallakin motar har saida ya fito.An ɗauki tsawon 10 minutes kafin matashin dake draving motar ya fito. Back sit ɗin motar ya buɗe nan kuwa sai da aka kusan 20 kafin wani siririn matashin saurayi ya fito izza.

Ƙafa ɗaya ya fara zirowa ƙasa sanye da halp cover shoe white color mai adon Stone a jiki irin na sarakuna.Cikin loƙaci ƙalilan ya fito da gangar jikinsa,Dogo ne sosai amma yana da ɗan kauri jikin shi a murje yake alamu na yana cikin hutu da jin daɗi,yana da hasken fata amma ba sosai ba.Farin yadin boyal ne a jikin shi mai ɗauke da ƙananun zane,wanda ya sha ɗinki irin na samarin zamani,sai Black agogo daya ɗaure a tsintsiyar hannun shi na dama dashi,a jikin siraran fararan yatsun shi kuwa ya saka white ring mai kyau a karamar yatsa.kanshi bai saka hula ba sai baƙar sumar shi data sha gyara gwanin sha'awa kamar ɗan India. kyakkyawar face na mai ɗauke da manyan dara-daran eyes balls ɗin da suke kamar madara.

A hankali ya rufe manya eyes ɗin shi yana sauke ajiyar zuciya.Tare da furzar da iskar bakin shi.Manyan wayoyin shi dake riƙe a hannu ya kalla ga dukkan alamu ƙira ne ya shigo.

Ɗan siririn tsaki ya ja wanda idan ba kana gaf da shi ba ba lallai ka ji ba. A kunne ya manna woyar cikin fusata murya a daƙile ya furta.

"Zanci ubanka Wllh Najeeb akan takura min da kayi!, Wllh idan ka tunzirani zan fasa maka visa'n naga uban da zakay ok”

Datse woyar yayi Cike da taku irin na zaratan maza ya fara taku yana nufar cikin hotels ɗin.da sauri driver'n ya mara masa biya da system nashi da dayar woyarsa.

A room na daban shima ya sauƙa tare da kayayyakinsa suka zube akan lafiyayyan gado. ZAYD SURAJ kenan ɗa ga Sarkin kano mai martaba SURAJ SUNUSU SHUREIM.

AK

Cikin bacci yaji ya soma jin vebration na woyarsa, da ƙyar ya iya buɗe lumsassun idonsa. Idanu ya tsurawa screen ɗin wayar dake ta faman ruri, tamkar me nazartar wani abu haka ya tsira wa woyar kaifafan idon shi.

Duk da cewar yasan ZAID bazai ƙirasa haka kawai ba, lallai dole saida wani abu haka nan ya tsinci kansa da faɗuwar gaba. Hannunsa ya miƙa da niyar ɗaukar wayar saidai kafin yakai ga ɗauka ƙiran ya katse.

Ɗin Jim yayi yana me tunanin bin ƙiran saidai sanin da yayi cewar mai ƙiran nasa zai sake ƙira ne yasa shi sauƙe ajiyar zuciya tare da fesar da numfashi.

Anutse ya tashi zaune yana me tunani acikin zuciyarsa, haka nan Idanunsa da suka dan ɗan tara ruwa ya lumshe saboda tunowa da PAAH tare da Momma'n shi da yayi.

”ZAID EMAAR KUWAIT”

Ya furta a saman laɓɓansa woyar ya jawo tare da mannata da kunnensa. Daga cennnnn Zaid cikin yanayin sanyin jiki ya furta.

” ABDOUL-MALEEK PAPA?”

Zaune ya tashi da sauri amma a zahiri ba saurin yayi ba shine a ganinsa yayi saurin.

Cikin fitar sautin da yayi low sosae ya furta.

”Why? Where is my PAAH”

Shiru daga cennn Zaid yayi, Ak kuma jin shirun Zaid shine ya sanya shi furta.

”Ina PAAH yake you will die ko? ka buɗe baki kamin magana Zaid”

Ya ƙarashe cikin sautin tsawa

“Ko ɗaya bai mutu ba anyi poisoning nashi ne agant!, wannan tafi ko wacce iriyar gubar da aka saba poisoning nashi da ita. Domin wannan da wuri zata iya zama sanadiyar rasa shi acikin loƙaci kaɗan, matuƙar akayi wasa to tabbas zamu iya rasa rayuwar PAPA gaba ɗaya”

Wani irin sakur zuciyarsa maganan da Zaid ya faɗa mishi yayi, yana jin daidai yake da bugun zuciyarsa acikin kunnuwansa, haka yake jin maganganun na yankar zuciyarsa.

Saurin fusgo numfashinsa dake ƙoƙarin kwacewa zuciyarsa yayi ta hanyar furta kalman.

“Innalillahi Wa Inna Ilaihirraju’un!!!”

da sauri saurin dake tafiya da gudun bugun zuciyarsa ya furta.

”what? My papa his under incapable survive in the world at this condition? oh god tell me the Truth I'm very dangerous twin!”

Jin yadda lokaci daya yanayin dan uwansa twins dinsa jininsa ABDOU-LMALEEK AK KUWAIT ya sanja ne ya sanya.

Ya shiga kontar masa da hankali, ganin kamar hankalinsan na kwanciya zai yi bane ya sanya ya shiga fada masa kalma daya takkk.

Wadda bansan ko wacce kalma bace itane ta nutsar da AK da kuma lurar dashi.....

BY AMMEY LAYLERH

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

⭐ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page 29&30

ROMANCE

BLACK MONEY

DEEP

BEST LOVE

KUWAIT

Zazzau ne suke a falon maza da mata kowa ran nan a haɗe wasu ido yayi ficin ficin.

Mommah dake dab da ƙafafun MOH JIDDO idanunta sun kaɗa sunyi jazur tana sanye da Alkaybba hannunta rikeda tissue dakuma charbi tanaja, sai wasu daga cikin manyan fada irin su Waziri, Wambai, Makama dakuma Sarkin dawaki, chan kuma saiga wasu Manyan dattawa maza guda biyu sun shigo sun zauna suma, dan faɗuwa gaban Mommah yayi dan haduwan mutanen nan wanda bayan sarki sune masu fada aji a fadan ƙasan Kuwait kasan babban abune, ƙarasowa suka yi tsakiyan ɗakin sannan suka sami waje suka zauna

Zaid ne ya ɗago rinannun eye's nashi tare da duban MOH JIDDO cikin daƙushashshayar murya yace " JIDDO kene kika aika akirani"?

Girgiza kai JIDDO tayi kafin ahankali tasa tisssue saman fuskanta tashare hawayen tasss sannan tace "Wambai ne ya aika kazo zaka ƙira musu wannan tantirin ɗan uwan naka"

dasauri yadagokai yakalleta tare da sauran jama'an ɗakin dake kallonshi yace "tooh" anatse waziri ya furta "yɤan uwanka duka sun iso na kusa dana nesa"

Sai kuma ya ɗan yi shiru a tare dukansu yɤan ɗakin suka zubama waziri ido duk kuwa da sunsan YARIMA MALEEK zai ambata amma hakan bai hana su binsa da ido ba.

"YARIMA ABDOUL-MALEEK fa"?

Ya faɗa wanda iyaka ambatar sunan shi da akayi Saida zuciyoyin wasu daga cikin su ya buga.

Adan hankali Zaid ya sauƙe yɤar ɓoyayyen ijiyan zuciya yace

"naƙi rashi ba adaddi bana samunshi" salati Al-hussein ya saki cikin babban sauti sosae ya shiga furta

"Ban taɓa ganin gantalallen yaro irin ABDOUL-MALEEK ba ohh Allah Ace mahaifinka na ahalin Rai ko Rayuwa amma baka ma san a halin da yake ba"

MOH JIDDO ce ta tare shi da faɗi

"Dama fa ba jinin MARYAM bane yake yawo a sassan jikinsa, kaima da ɓata baki kake Wllh hussein"

cikin murya mai laushi wamzai ya furta "MOH JIDDO adai yi haƙuri muna a halin ciwo ne" ya faɗa yana rusunar da kansa ƙasss

Wani mugun kallo MOH JIDDO tabi wambai dashi wanda suke ƙira da *RIGA DAKI* a yarensu na cennnnn.

Cikin tsana da jin haushi MOH JIDDO ta furta ”Ni na rasa mecece matsalan ABDOUL-MALEEK da ya gwammace ya tafi yawon duniya har wata uwa Nigeria akan abbinda ba tabbacecce bane. Shi burin daya ɗauka alƙawarin cika tashin”

Ijiyan zuciya Mommah ta sauƙe tana jin wani abu na yawo a dukkan sassan jikinta.

“Yanzu ai idan ya riski saƙon mutuwarsa a yanar gizo ya dawo!, nasan duk inda yake aduniyar nan zaiga news na rasuwan mahaifinshi dan haka zamu ganshi idan ya riski saƙon macewar ubansa”

Yana faɗin hakan ya tashi yayi gaba abinsa yawuce yafita yanajan ɗan ƙaramin tsaki aranshi bayan yakai waje.

Cikeda ɓacin rai MANDOOD ya furta ”MOH ve said this time without number to Mai Martaba he should call ABDOUL-MALEEK to order, duk cikin yaran me martaba babu gantalalle kaman ABDOUL-MALEEK, yaƙi zama ya koyi komi na al’addun masarautar mu, sabo da yana jin kansa shi tantiri ne”

TUN DAGA HAIHUWA MA KUWA

Domin Abdoul-maleek hadarine malafar duniya,funkasau babban girki, biri da gatarine shi ajalin me gonna, Jan kasa na bayan daki kowa ya ganshi ya tuna Allah. Shi kadangaren bakin tulune a barshi ya fada ruwa a taba shi kuma ya FASA TULU, Ak ginshikin dutse me kowa yayi karo dashi shika fadi, soja mazan fama namijin mazaje an buga dashi an barshi saidai su buga su barshi kuma domain shi din dashen Allah ne, murucin kan dutse be fito ba saida ya shirya_

ZAID ya furta a cikin zuciyarsa ya miƙe yana ficewa a ɗakin shima domin da biyu yaki sanar musu yayi magana da AK din.

haka suka ringa fita ɗaya bayan ɗaya, ɗakin ya rage daga Mommah sai RAZEENERH mata ta farko ga Me martaba sarki *SARKI HASSAN AL-HASSAN EMAAR KUWAIT*

Wasu irin kaifaffun hawayene suke saƙƙo mata, cikin ƙunar zuciya da irin raɗaɗin dake ƙona zuciyarta ta kwanto da kanta zuwa jikin Mommah MARYAM. Ta fashe da wani gurgegen kukan ɓakin ciki.

”Shin Sai yaushe zamu dena zubarwa da ƙaddara hawayenmu? Sai yaushe abubuwan dake ɓoye zasu bayyana kansu? Na gaji-na gaji NA GAJI MARYAM, inajin haƙuri na na gab da ƙarewa akan abubuwan dake faruwa dani a cikin wannan azzalumar masarautar HABA!”

Ta faɗa cikin sake fashewa da wani gursheshen kukun,

"Haƙuri shine matakin ko wacce nasara RAZEENERH, Ko wacce Nasarar rayuwa da ɗaukaka kuma suna zuwarma baya ne da tarin ƙalubalen rayuwa salo daban daban, me yasa zamu gaza cinye ɗan takin daya saura a cikin rayuwarmu?. Xuwa yanxu AYSHATUL HUMAIRA a bayyane take garemu loƙaci kawai muke zuwa ya bayyana kansa,Ayi walƙiya Allah ya bayyana mana magautanmu na ɓoye dana fili mu gansu su fito suna hawaye anyi walƙiya!!!"

Sosae suka sha kuka me sunan kuka kafin su runguɗa zuwa ga special room donper ɗin da me martaba yake cikin haɗaɗɗen hospital ɗin masarautar.

Dammmmm ɗakin yake tarin yan uwa na kusa dana nesa irinsu garin Makka Madina Saudi Arabia dadai sauransu aurarru da ma'aikatan da suke aiki a wojen ƙasar.

Wani gauran numfashin da sarki HASSAN AL-HASSAN EMAAR KUWAIT ya kawo ne ya sanya baki ɗaya katafanin jama'ar parloun, juyowa zuwa gareshi.

ALHAMDULILLAH wasu suka shiga furtawa wasu kuma zuciyarsu na ƙonewa ne tare da yin baƙikirin tun durun da tsabar masifar baƙin cikin da ke soya zuciyarsu ƙurmus.

Ahankali ya shiga bin kowa dake parloun da ido, cike da tsananin ƙarfin hali da kuma dauriya irin ta zaratan sarakai ya saki kyakkyawan murmushinsa me kyau. Wanda exactly tsananin kamfaninsa da ABDOUL-MALEEK KUWAIT AK suka gama bayyana.

"Alhamdulillah Ban mutu ba Allahu Ya tsare lafiyata a kwanana akwai ƙari don haka kowa ya kwantar da hankalinsa" sarki AL-HASSAN EMAAR ya furta

Wanda wannan maganar nashi ya daki wasu ɓoyayyan rufaffun zuciyoyi daga cikin al'ummar denpor ɗin....

Haka kaifafan idonsa yaci baba da yawo har sauke kallonsa akan Ayeshan shi. Kyakykyawara mace karshe a fannin hakuri mace me kamar maza CE ita wajen danne ko wanne irin ciwon cake damun zuciyarta.

Da wani sassayan kallo ya bita yanajin lallai rayuwar idan babu ita to shima babu amfanin tashi rayuwar, a jinin jikinta taji irin kallon da take binta dashi.

★★★

Abuja

Nigeria

Zaune yake yayi crossing kafafunsa sanye yake cikin shigar kananan kaya na shan iska, loptop ne a gabansa kan dan table tonight din dake gabansa, yana faman sarrafata cikin kwarewa yake latsa keyboards din system din.

A nutse zayd suraj shureim ya karaso har inda AK din yake zaune.

Zaman shima yayi ba tare daya furta komai ba, haka suka shiga zaman kurame har na tsawon 30 minutes, A nutse Zayd dubi AK da yama nuna tamkar besan anyi ruwan zayd din bane yadan daki shoulder na AK din.

Sai kuma ya dan saki wani shegen murmushi domin shima karshe ne fagen tashi izzar Wanda shima sarautar kano ta gama ratsa ilahirin Jinin dake gudana a cikin jikinsa.

”Yaryadi baka yadon banza yau kuma dame kake tafe?, ka kirani ka sanya na baro garina zuwa wani garin Right?' Ka kuma shareni abunka to Dan ubanka Wllh zan komawa na domin inada abubuwan yi dana baro ba kamar kai ba”

Wata katuwar harara ak ya sakarma zayd yana fadin.

”Jeka mana dan uwarka ka gani idan Abbu ko ummieyn Momma basu koromin kaiba”

Ya fada a daidai lokacin kuma ya kammala aikinsa na cikin laptop, tashi yayi tare da yin gaba yana fadin.

”Idan kaga dama same ni a room na baka 2 mint domin INA shirye shirye bar muku kasarku ne”

”Look AK karka ma soma hakan, Don munyi woya da mommah tun a daren jiya ta shaidamin cewar jikin Me mar taba da sauki sosae $0 inaga babu bukatar zuwanka!”

Ko ta kanshi ak bai biba saima wucewarsa da yayi room

Bayansa zayd yabi cike da shekiyanci yake tsokanarsa ai dole ya bashi girma tunda shine autan su momman ak din.

Ganin nan din ma ya share shi ne ya sanya shi komawa seriously tare da furta.

”Muyi abinda ya kawo mu kasan akwai Case's da yawa dana tsalallake na baro dude”

Charkkk kuwa ak din ya tsaya tare da juyowa ya fuskanci zayd din.

Zama sukayi a tsakiyan kayataccen palon hotel din, computer'nshi ya janyo tare dayin wosu yan danne danne said kuma ya juyo da fuskar computer system din xuwa gaban AK.

Da wani black beauty guys ya fara cin karo wanda me sanye cikin kaki na yan sanda.

Tsaye yake chark a gaban Cf of the police babu alamun tsoro a tattare dashi.

Gani yayi wannan ceef din ya mike a fusace yana duban wannan tsayayyen matashin, kafin kuma cikin fusata ya furta.

Akan me zaka harbe shi?, Tambayarka nake me yasa ka harbeshi? Me yasa kai baka Iya sarrafa kankane?

Gani yayi wannan matashin police din ya furta.

Bana Iya sarrafa kainane akan irin wadan nan tantiran yallabai!

Kenan saika harbe shi kuma?

Ceef ya sake furta a tsawace.

Me yasa bazan hukunta wadan da suke barazana wa al'ummarta ba?, nayi rantsuwa da girman Allah zan kare kasata da al'ummata. Akan mene yasa bazan harbeshi bayan shidin gurbatacce a cikin al'ummar?

Ya fada tare da sarawa a gaban Ceef din.

To hakan ba shine dalilin da yasa muke nan din ba?, muna kamasu mu gurfanar dasu a kotu domin karbar hukunci daidai da abinda suka aikata

Tsawon wanne lokaci ake dauka kan a kammala yallabai?

Wannan matashin ya fada cikin sigar tambaya shima.

muna Iya kaiwa tsawon wata biyar ko kuma ma shekara

Kafin xuwan wannan lakacin taya kake Iya bacci?,No bana Iya baccin to yallabai

Yayi maganar cikin tsananin fushi.

Nima wannan shine dalilin da yasan nake ta bibiyar Tanbuwal, duba wadan nan duka sun aikata manyan laifiku!, duk kuma Wanda ke a cikin wannan kundi suma a kashe su kenan?

Ye jefawa matashin alamar tambaya.

Kashe sun shine daidai yallabai idan har muka kare ADALCI to daga nan ne shima ADALCIN saiya zama me bada KARIYA a garemu!

Daga nan Video'n ya yanke.

”Inspector KAMAL RANO kenan, matashin dake aiki da dukkanin rai da zuciyarsa a jihar kano!. Shi din marayane A karamar hukumar kano yake a garin RANO baya da uwa baya da uba dangin duka mahaifansa sun wofantar dashi. Yanzu haka yana zaunane a garin kano anguwar sharada”

Wani dan banzan murmushi ak ya saki kafin cikin muryar nan na no nonsense ya furta.

”ina bukatar ganinsa a cikin week din nan”

Daga haka ya mike yana barin wurin, bedroom ya shigee shi kuma zayd ya bar dakin baki daya.

Bayan sun tattauna wasu muhimmam abubuwa daga baya.

LAGOS

~Meerah~

Sanye take cikin shigar atamfa chiganvy coffee colour ta ɗora dogon shimar din ta har kasa.

Sake kallonta salman ya yi a karo na biyu ganin yanda ta haɗe rai.

"Meerah"

Ya kira sunanta batareda ta kalleshi ba ta amsa da

”na'am”

Wani gauron numfashi ya sauke sai kuma ya furta.

”Naga kamar baki saurarena ai a irin wannan lokacin kamata yayi ace zallar farin ciki kadai za'a gani tattare dake, amma da dukkan alamu ko saurarena ba kiyi bare ki fahimceni ma”

kallonsa tayi da manyan idanunta masu cike da wani irin kwarjini

sai kuma ta dan tabe baki tace

”Ai naga kunnene ki ji kuma ina jinka ko ihu kakeson nata yi kwararo² titi² ina fadin ina jinka?”

numfasawa ya sauke kafin ya furta

”shikenan na baki lokaci kije kiyi tunani da kanki ina fatan za ki yanke shawara mai kyau, kasancewar saura nan da watanni mu zama Ma'aurata”

Wani shegen kallon ta wulla masa yi tayi kamar zata yi magana sai kuma kawai tayi shiru ta juya tabar wajen kawai, domin a ganinta wannnan tsayawa ja'in jar ma aiya sami arzikinta kenan.

Domin a ranta take jin Wannan auren ba tabbatacce bane.

Gefen lips Inshi yadan ciza kadan tare da furzar da numfashi yasan ya shige ajin yarinyan, Bama don ya kadaitu da ita ba har ita wacece da zata dinga wulakanta shi.....

*BY AMMEY LAYLERH

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page 31&32

”Amma dai ba har kin dawo daga firan ba Meerah ba?”

Disha ta tambayeta ganin har ta dawo ga ran nan haɗe babu ko sassauci.

Rabuwa da ita tayi taki tanka mata, ita kuma ganin ta mata banza ne ya sanya fadin.

”Haba meerah bakison mutumin nan kawai ki fito fili ki fadama su baffa fine!, amma shi haɗe ran na mene kinsan dai ba maganin damiwa zaiyi miki ba?"

Wata yar karamar kwafa taja tare furta ”wlh idan har bai yi a hankali ba sai na yi masa rashin mutunci nifa banson irin haka, na gaji da wannan takurar haka nan haba!” ta karashe maganar a tsawace.

”So sorry meerah kiyi hakuri kici gaba da kaima Allah kukan ki, Insha Allah zai duba lamuran”

Nooding kanta tayi tana jingina da jikin duguwar kujerar palonsu. Nan suka ci gaba da firansu amma sama sama, domin meerah bata jin kanta a cikin mood me dadi.

Washe gari da misalin karfe Biyar da Rabi na yamma Meerah da disha ne zaune jingune da roiler din dake harabar wurin. Meerah ta dan dubi Rolex watch din dake hannunta ganin shida na kokarin karasawane. Ya sanya ta mikewa tana fadin.

”Inaga lokacin tafiyana yayi zan wuce bye Sis”

”Laaaa kinga ma motar ya Ayaan ta shigo kizo saimu sauke ki gida!”

Cewar disha, Tafiyanta taci gaba dayi ba tare data dakata ba tana gyara zaman bag din dake rataye a shoulder nata cikin muryan no nonsense ta furta.

"I m so sorry Sis to kar kice wani abu please zan fita bakin gate na tara napep then nasan ma Wannan uban yan nacin na dab da shigowa."

Saurin juyowa disha tayi ta kalleta tabbas idan da sabo yaci ace ta saba da halin meerah, saidai ta gaza sabawar har zuwa yanzun.

Parking car din da ayaan yayi a gabansu ne ya katse maganar da disha take shirin yi.

”Yen mata barkanku da hutawa ku shigo mu wuce” ya fada yana sauke glass na motan.

Gaba kawai ta wuce ta bar disha tsaye, domin meerah bata magana biyu kuma dama ta tsani ayaan din Sabo da masifar kallonta da yake yawan yi.

Dan bata fuska disha tayi tare da shigewa cikin motar ta rufo murfin da karfi. Ta gaban ta suka wuce bayan ayaan ya sake mata tayin shiga amma ko kallo be isheta ba.

Idanunta ta dan lumshe a hankali kuma saki wani dan murmushin da ya bayyana akan fuskarta. Ganin yadda fuskar mutuniyar ta tayi taki ko kallar inda take lokacin da suke wucewa.

Tasan cewar hakan da disha tayi alamane dake nuna cewar tayi fushi da ita kenan.

Ci gaba tayi da tafiyanta har takai bakin gate din fita daga gidan jaridar, haka ta ringa ratsa manya manyan motocin dake wurin. Tafiya takeyi amma gaba daya duk bata jin dadin yanayinta amma ko a fuska baka Isa gane yanayin da take a ciki ba.

Hango wani me napep yana zuwa ne kuma yasa da sauri ta soma daga hannu tana son tare mai napep din.

Cikin sa'a kuwa ya tsaya cikin yanayin dan hanzarinta ta yunkura da niyar shiga napep din.wata arniyar Rolls *R* Rayce ta danno kanta, wacce kiyastin kudinta a dalar amurka yake daidai $25,000. kamar ance daga idonki sukayi 4 eyes da duk da yau din ma idonsa rude yake da blue shade.

Wani dan banzan kallo ta cilla masa tare da murguda bakinta, kafin can cikin kasan muryarnta irin na tsiwan nan ta furta.

{MARA GASKIYA DAI KO A RUWA GUMI YAKE}.

Fadawa cikin napep din tayi tayi sai kuma ta shiga furta kalmar

”La ilaha illa anta's subhanaka inni kunti minazzalin!”

A bayyane domin zuwa yanxu dai tasan wannan mugun wani abun yake sake nufi da ita....

”Malam nace don Allah kuwa kasan wancen mutumin na cikin motar cennnnnñ?”

Ta fadi da kokarin nuna masa motar, saidai me? Sama, kasa, haka ta nemi motar ta rasa.

”Hajiya wacce motar fa?”

Muryar dan sahun ya farkar da ita.

Ijiyar zuciya ta sauke tana fadin ”muje kawai anguwar dadin kowa zaka sauke ni farkon layi!”

Ta fada tana me sake kallon inda taga motar da yake ciki.

"To Hajiya zaki biya 400"

Me napep din ya fada yana kallonta.

Nooding kanta kawai tayi batare kuma da ta nemi ya rage mata ba, ta bude bag din ta kudin ta bashi yaja suka tafi.

So kawai take taga sunkai gida don Anne'nta tace mata zata aiketa gidan hajiya umma,amma intai dare ba zata aike tan ba ko kafin ma ta dawo ta aika Raiha.

Wani irin kyakykyawan murmushin daya sanya me napep din kallonta ta tayi.Tuno da Anne da tayi Ita kanta batasan iyaka adadin son da takema Annenta ba, Kawai dai tasan Wani irin so takeyi mata na musamman, son da yake tafiya da tausayi mai tsanani bata da kowa aduniyar nan daya wuce mata Anne'nta itane komai nata Garkuwanta haka kuma farinciki agareta ita da Raiha dinta. Hannuwanta da suke hade wuri guda ta sake dunkulewa, tana matukar tausayin Anne'nta sabo da ta tashi ne ba uwa uba Yar uwa Dan uwa wani nata a tare da ita.. Ahankali kuma ta jingina bayanta da jikin kujeran motar.

{INASONKI ANNE NA}

Ta fadi hakan acikin zuciyarta tana mejin tsananin shaukin son mahaifiyar nata na ratsata.

Uwar da takejin babu irinta a fadin duk duniya, Uwar da take fatan faranta mata akoda yaushe, Uwar da take matukar son farincikinta fiye da kowa da komi na cikin duniyar.

Aikuwa basu wani debi lokaci ba suka iso gidan kuma babbar sa'arta data ko shirin tada sallah ba'aiba.

Da sallamarta ta shiga kota kan mutanen da suke zazzaune bata biba, Da Anne'nta ta fara cin karo a palo tana duddura humrarta me azabar kamshin gaske. Gaida ta tayi dama kuma al'adar tace hakan, duk idan ta dawo a wurin aiki takan gaida Anne'nta.

Amsata annen tayi da Yar fara'arta tana fadin.

”Ai kuwa da baki zo ba saidai ki tarar Raiha ta tafi!”

Anne ta fadi da dariya a saman kyakykyawar fuskarta me kama da bata yan Nigeria ba.

”Ai kuwa da kuka zanta miki Allah Anne!, kinsan na dan kwana biyu rabo na da gidan hajiya umma ”

Ta fadi cikin muryan shigoba tamkar wota baby.

”Crying Mumu gurl ey kuwa da har videoing dinki zanyi na dora a media with caption ”

Dan micilon bakinta ta turo gaba tare da fara Mirza kafa a palon.

”Yowwa Anne dakko min eyken kinga gudu na tayi, daga gidan su maman Mujaheed din. Aysha CE ma ta tsayar dani na mata wasa, badon haka ba Ina ba mummy Hafsah aikar zan dawo!”

Duk Raiha CE me Wannan maganar ba tare data bari ko numfashi tashaka ba.

Da sauri Meerah ta mike tana ma Raihan hararan wasa.

”Anne dakko saimu tafi tare kafin a shiga sallah”

Da to Anne ta amsa tana shigewa uwar dakan ta babu jimawa ta fito hannunta rike da laida. Harta mikama meerah ta tuna ko abinci bata Ciba.

Dauke wani wargi a idon ta tayi cikin kamewa ta furta.

”Zauna sai kinyi dinner tukunna”

Fada fuska tayi kadan sai kuma ta furta. ”Ayya Anne kinga fa naci tare da disha”

Gyara zaman ta Anne tayi cikin no nonsense ta furta ”Ashe baki shirya fita ba kenan okay?”

Tana gama fadar ta mike tayi tayo tsakar gidansu.

Haka ba don taso ta janwo plask din abincin gabanta, washe baki tayi ganin dan waken fulawa ne.

Ai a tamanin ta janyo gabanta Raiha tace suci tace mata ta koshi. Sai kuma ta dan matso kusa da meerah din tana fadin.

”Kwai da Kwai Maman Mujaheed ta bani, Ashshalle kuma ta bani rufaida yoguht”

Ta fada tana kyafkyafta ido kamar wata mara gaskiya,domin tasan idan Anne taji kashinta ya bushe.

Dan dole suka tsaya sukayi sallar magriba kana suka amshi sakon suka tafi....

Tana fitowa tafiya kadan sukayi ta hadu da Fatima kawarta da suke layi daya, A cikin wata hadaddiyar motar ta prado. rashin kyawawan halin da fatiman bata da shine ya sanyata meerah din yakice ta a jikinta, Amma ita fatiman sosae take kaunar kwayancensu da meerah din, rashin fuska ya sanya itama janye mata amma duk inda suka hadu tamkar tasa zani ta goye meerah din haka takeji.

Tun kamin su karaso tayi parking motar ta.

Fitowa tayi cikin fara'arta ta fito tana ma meerah din magana.

”A ahhh kawata wannan fa ba girmanki bane kina tafiya da qafa zuwa wani wuri, gaskia bakyama kanki daidai ace kina mace cikakkiya da acikin matan make Ishasshiya ce meji da tashen kyau da cikar zatin halitta da haiba fara kyakyawa ga diri son kowa qin maqiyin Allah zaki zauna kina yawo a kafa,Dubeni koni da banbkaiki kyauba dubi irin motar da nake hawa bare ace 500 hundred ta gagareni na hawa napep. bareke kyakykya son kowa kin wanda ya rasa kullum ke fuska kwakume da niqab kina cutar kanki, wllh meerah kullum bazan gaji da gaya miki gaskiya ba akan kiyiwa kanki fada, yanxu dai shigo na rage miki hanya”

Ta fada tana wani iyayi ita nan ga me mota.

Wani dan iskan kallo meerah ta watsa mata kafin kuma ta saki murmushin takaici ta furta.

”Ai dana shigar da aka sameta ta haram kwara na shekara ban kai inda nake son kaiwar ba, dadai na shiga motar da ake sameta ta kyazamtacciyar hanya maras kyau!”

”Nifa abu mafi bani takaici dake befi yanda kike cewa wai bazaki shiga motana ba abu kadan kice haram, ina zinar bajikinki nake kaiwa ba nawa ne kuma bake kikai ba, amma ace kina kawata kina tafiya da kafa gaskia Impossible shigo mu tafi”

”Fatima kenan koke fatana Allah ya shiryar dake babu wani kalar kaddarar da zai Sa Insha Allahu na aikata zina. musamman irin wacce kukeyi fatima karuwa tsirara babu ko sakayawa shine sunan da kike amsawa. Kina wofintar da darajarki ta ya mace kina wulakanta suturar da Allah yai miki kina kaiwa mazajen bariki jikinki,suna amfana da ni'imomin jikinki suna halllakar dake! suna amfani da dan abinda Allah ya basu na dukiya suna dulmiyar dake suna rudar dake!, yayinda su nasu yayayen suna cen a killace a nasu gidajen a garkame.

Auren da ze gagareki nan baba su nasu yayan na gata suke zasu musu wanda dan gwamna se yar gwamna! Yar minister kuma se dan chiaman, Dan shugaban qasa kuma se yar minister'n kudi ko mimister'n fetur!!! Yayinda ke kuwa aure ze gagareki koda dame daukar ruwan layin kune sabida wanda suke batancin dake sune dai zasu koma su zageki!!!”

Wani numfashin bacin rai ta fesar kafin taci gaba da fadin.

”Koda yaron abokanansu sukaji zasu aureki zasuce ke yar bariki ce! Yar Bariki shine sunan dazaki samu daga bakunansu amaimakon Fatima ko *TESTY* din da suke kiranki dashi!!! Ya kamata zuwa yanzu Kima kanki fada fatima ki saisaita nustuwarki da rayuwarki”

Dan tabe baki fatima tayi tace

”Bari kiji ko annabi dakanshi yace mu nemi tsari da talauci daga wurin mahaliccin bayi!, Sanin kanki ne kin rigada kinsan irin kuncin rayuwar da muke a ciki. Duniya taki kowa kanshi kadai ya sani, Masu kudi basa bada taimako domin Allah talaka yana cikin wani irin hali na kani kayi, da qyar da sidin goshi kake samun na break, wani kuma saiya kwana ya wuni be ciba alhalin ga masu kudin cennn sun tara sun rasa yadda zasu dashi. Ba dole muje su amfanu da albarkatun jikinmu su bamu mu kashe wutar gaban mu. yanzu kuma Allah yamun hanyar kasuwanci bazan cuci kaina ba allah ma ya gani”

Fatima ta fadi cikin kwarin gwiwwarta.

girgiza kai kawai meerah tayi wato kudi masifane kuma daudar duniya. ta furta a cikin ranta tare da duban fatiman ta furta.

”Karuwanci yanzu shine sana'ar? dan Allah fatima ki dawo madaidaiciyar hanya duk wani mutum indai masoyinki ne na gaskiya fatan shiryar ubangiji zai nemar miki, bawai ya famfa kiba wllh zina masifa ce fatima, Annabi bafa cewa yai muyi zina ba cewa yayi karmuyi zina mu kuma nesanta kanmu daga duk hanyar da zata hada mu da zina!. ma'ana karmu kusanceta mezesa ki kira wannan da sana'a?”

yatsine fuskarta tayi alamun gajiyawa da qosawa da zancen ta furta

”Meerah banida wani zabin daya wuce wannan idan na dena neman kudi da jikina ke zaki ciyar damu nida mahaifiyata da yan uwana? Ki sani wllh meerah ina sane sosai da haramcin aikata zina amma wllh bazan bari mu rayu da yunwa ba nida yan uwana”

Dan lumshe idonta tai tana me qoqarin hana qwallan idonta zubowa.

"Fatima ki barwa haramcin nan don Allah na rokeki, Kuma fa karki manta na gari basa taba karewa a cikin duniya duk kuwa irin lalacewar da zamani yayi”

”Fatima muje wata maganar kinga ma wani ana kirana wani alhaji ne yake son tear leather a ledar ta, da zaki yarda ai dana jonaku Wllh ki kwashi rabonki kema”

Shiru kawai meerah tayi domin fatima tayi nisan da batajin kira,wannan ya sanya ta Jan hannun Raiha sukayi gaba abinsu. Ganin lokaci na tafiya har Isha'i na shirin kawo kai.

Tafiya suke amma gaba daya cikin kunan rai take tana mamakin wannan rayuwar da wasu suke ganin hanyarsuce madaidaiciya.Tasan a yanzu haka da za'a kasa Mata kashi dari da kyar a samu kwararan talatin na gari, towai meye matsalar? Daga kuma ina abun ya samo tushe?, Rashin hakurinmu?, Rashin kai zuciya nesa da kuma son zuciyoyinmu.

A fili ta furta

”Ya Allah ka mana maganin dukkan matsalolin da suke kewaye da rayuwarmu, ka Zama gatan Mara gata, ka sanyaya zukatan bayinka ya Allah ka kuma nesan tamu daga cikin gurbatattun bayinka”

Haka da taci gaba da tafiya cikin wani irin sanyin da jikinta yayi. Haka sukayi tafiyan babu armashin komai, Ko a gidan hajiya umman ma sama sama suka gaisa suka bata sakon suka dawo gida.

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~□ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... □~*

Page 33&34

Bayan dawowansu dake lokacin anyi isha'i sallar tayi kana daga baya kuma tayi wanka. Shirin bacci tayi bayan tayi nafilanta kamar ko yaushe,kwanciya tayi tare da daukar wayanta Deta'nta ta kunna ta shiga WhatsApp nata, sama sama tadan galli status na mutane, sai itama ta koma wurin status din tare da rubuta.

*_BEAUTY IS NOTHING WHEN BRAIN IS EMPTY_*

Tare da sanya emoji na hamma. Har zata sauka sai kuma taga anyi tagged nata a group nasu na *Jonalist empire's*

Shiga tayi hayatudden taga yana tuna mata da fitan da zasuyi gobe da hantsi zuwa wani park. Da _OKay don't worry Allah ya kaimu_

Ta bashi amsa tana sauka.

district Abuja

Yana kwance akan irin wannan doguwar kujerar me kama da gadon nan. Lallai sai yau na sake tabbatar da kamannin AK da dirin jikinsa da wannan actor'n Indian film din suke tasananin kama wato *PRABHAS* Sai naga fuskan shin ma kusan nace a ga nina ma yafi *PRABHAS* din ma

haduwa da hasken fata the guy is faultless and flawlesss and very cleaning skin.

Sanye yake cikin wata Riga Latvia Lithuania Luxembourg da wando na kamfanin dior hormes white shirt and a very soft white, masu tsananin taushi da kuma laushi.

Suman kanshi is silky black and shining gashin nan kwance har keyarsa inda ya masa wani dan iskan aski. A hankali ya shiga ware lumsassun idonsa dogayen eye lashes dinsa me suka shiga motsawa, harya samu ya bude idon a kasalance.

He loves keeping straight face din na a matse kamar kullum, Nikam zan iya rantsewa ban taba ganin mutun mai son bata rai kamar AK ba.

well pampered yatsun hannun shi da suka ji gyaran manicure ya lankwasa su suka bada sautin *BASSs* kai Wllh duk inda ake Neman cikakken namiji Ak shine katt kuma babansu, don he's goddam porschy sosai yaji wankan aji da Hutu hadi da haduwa.

Door bell daga taba ne ya sanya shi dakatawa daga niyan nufan bedroom da yake, cikin muryan nan kasa sosai ya furta ”come here"

Arms ne ya shigo shima cikin nashi shigan na bakaken suit, zama yayi tare da kaida ak din a takaice.

Shima zaunen ya koma tare da daukar woyansa yana latsawa.

”Already flight namu zai tashi ne da 4:00pm”

”okay alright”

Ya fada tare barin palon zuwa bedroom, shower ya sakarma kansa.

After 45 minutes sai gashi ya fito Sanye da bathrobe sky blue a jikinsa, daya soft hannunsa kuma dauke da wani towel yana sharce gashin kansa.

Soft fatar Jikinsa sai digar ruwa take, jikin nan yadda kasan kwai da madara don santsi da daukar I do.

Cikin be ko wanne lokaci lokacinsa ya soma shirya kansa, babu jimawa ya fito zuwa harabar hotel din kai tsaye parking space ya nufa. Domin yana da wata fitane kafin jirginsu yabar Abuja.

Meerah POV

Dake yau suna ta fita baccinta tasha sai sha biyu saura kana ta fito sanye cikin Arabian jallabiya ta mata. Anne tama sallama 1k ta bata tunda tasan inda suka nufa yau. Adda'ar samun nasara ta data da kuma binta da fatan alkhairi.

Haka ma saida ta shiga wurin baffanta shima sallamar tamay. 1k ya kuma bata sai ta fada masa anne ta bata. Shima adda'ar ya mata ta fito kai tsaye gidan jaridarsu ta nufa.

A bakin gate din gidan jaridar suka hadu da disha da hayatudden sai mardiyya, wacce take faman banka mata harara.

Ita kuwa disha tama manda da batun woni fada da suka yi jiya, da gudu ta karasa suna rungume juna.

”kai masha Allah dear yau kinyi kyau sosae"

Murmushin gefen baki meerah ta saki tana furta ”zaki farako”

”Kar dai Ku sanya mu yi leet oya Ku shiga muje”

Hayatudden ya fadi yana bude musu motar. Da sauri mardiyya ta bude gidan gaba ta shige.

Oho itakam ma merrah batasan abinda take ba.

12:00 suka Isa park din da zasuy aikin ranar akan wani kusa.

Shiga ciki sukayi bayin sun nuna I d card nasu. A inda ake faka motoci suka ajje nasu, kai tsaye A cafeteria suka yada zango order juice sukayi tamkar a gaske. juyar da kanta tayi tana kallon reception din park din yanda iska ke kadawa kaman za'ayi ruwan sama, flowers din reception din sai kadawa suke suna making sounds, wani iri taji zuciyarta namata da bazata iya cewa exactly ga yanda yake mataba. wani iri iri dai haka takeji kamar ana kallonta hakan yasa ta juyo dakanta adan hankali

Duk da yadda take da dakakkiyar zuciya hakan be hana gabanta faduwa ba. Wai me wannan mutumin yake nema da itane da yake ta faman bibiyar rayuwarta haka.

”Naga kinata kallon waje meerah ko wani abune yake damunki, gashi ko juice din baki shaba”

Hayatudden ya katse mata tunani.

Saurin dawo da nutsuwanta tayi tana furta

”babu komi kawai banajin sha ne”

Sai kuma kamar wadda aka tsikara ta mike tana ce dasu ”pls ina dan zuwa”

Ta fadi tare da mikewa tsaye kai tsaye cikin park din ta numa, Ahankali take binsa tamkar me sanda. Woyane a kunnensa cikin yaren labarcin da tamkar a bakinsa aka ruwaito shi yake wayar. Kafin daga karshe taji ya ambaci room 0035 3rd floor. Ganin kamar zai juye ne ya sanya ta saurin komawa baya a haka ya bace mata.

Rasa ma yadda zatayi takai kanta room din tayi, cennnn wota dabara ya fado mata wata maid service CE tazo zata wuce ta gefenta. Ai kuwa cikin sauri tasha gaban wannan maid service din tare da furta.

”please go to room 0035 a 3rd floor ”

”okey biyoni”

Wannan maid din ta mata jagora har xuwa gaban room din. Gabanta faduwa yake sosae amma haka ta danne ta tunkari kafar room din.

A hankali tamkar wota barauniya ta dan leka kanta cikin room din,Da kafafunsa ta fara cin karo Wanda suke sanye cikin wani sgegen bakin shoe Sandal's. Zara² fararen kafafunsa sunyi wani mugun kyau ta cikin takarmin.

”Boss kamar yadda ka umarta mun dauko shi yana dab da kawowa park din!, ba tare da bodyguards nashi sun ankare ba. Kana kana da zama da misalin 5:35pm da kamal Rano ya sauka shima tun 10:00 am”

Ita dai keyarsa da gashin kansa ke zube kawai take Iya kalla.

Dake shi komi nasa irin na muna fukai da marasa gaskiya yake samm bata ji abinda yacema dayan mugun ba.

Wani irin shegen zaro ido waje tayi ganin Wanda suka zo wurin domin shine wannan mugun yayi kidnapping dinsa.

Sosae jikinta ya shiga rawar tsoro domin taga wannan mutumin da gaske mugu ne, kashe mutane da sacesu kawai ya Iya.

Cikin wani mugun tashin hankali ta juya tana barin word din, tsabar ma ta rikice ta rasa ta wacce hanya suka biyo haka ta ringa sanja hanyoyi amma ta gane inda suka biyo da wannan maid service din.

Gafff taji tayi karo da wani Abu. A tsorace taja baya dake a mugun tsoracen take dama. Ai kuwa bisa tsautsayi kafarya ya zame tayi wani irin baya.

Wani razanannen ihu ta Saki tare da rimtse idonta da karfin bala'i ganin ashe kasa tayi. Baki daya ta gama saddakar da cewar yau saidai wata ba ita ba a cikin wannan duniyar. Shikenan ashe dama sallamar karshe ne tayi da annenta tare da baffanta.

Wani irin fusgota taji anyi babu zata,kai tsaye kan faffadan kirjinsa dake tashin wani irin bala'in kamshi ta fada. Ba tare da tunanin komi ba ganin ta tsirane ya sanya ta wani kankame jikin wanda ta fada da karfin gaske tana sakin wani raunataccen kuka.

”Allah Sarki Anne'na da tuni na mutu yau ba tare da nemo miki koda daya daga cikin ahalinki bane!”

Ta fada tana cikin muryan kuka sosae.

Wani irin fisgeta a jikinsa yayi tare da jifanta da wani shegen kallo yana Jan tsaki.

Tana yin ido hudu dashi a matsayin Wanda ya temaketa ta kwallara kara tare da furta. ”Kai cho na Wllh daka temakeni!, Wllh dana San Kaine kara na fada kasan na mutu, Allah ya Isa ban yafe maka ba! Mugu! Azzalumi!!!”

Tana fadar hakan ta kwasa a guje da gudun masifa tana yin kasa.

Tana dira a gabansu disha da suka haukace a nemanta. Itama a haukacen ta furta. ”Nafsi Nafsi Wllh kowa yayi ta kansa ga mala'ikun duniya nan”

Ta fada da karfin masifa tana kara kwasa a 449, haba tuni sai gashi sun take mata baya ganin yadda take gudu cin karfinta, domin sun San duk abinda ya tsorata MARYAM ABDULLAHI GWANI harya sata gudu to ba karamin abu bane. Da sauri hayatudden daya rigasu Isa gaban motarsu ya bude musu, su kuma suka fada yaja da mugun gudu suna barin wurin. Ai kuwa suna daf da fita a cikin park din idonta ya sauka a kanshi, alama ya mata da saina gimtse miki wannan shegen bakin. Tamakar kuwa tasan abinda ya furta din ta turo dan karamin bakin nata gaba tare da murgudawa.

”wai meerah meya faru?, dasu waye kuma kika hadu bayan mun jiyo ihunki daga can cikin park din, kafin kuma gudunki ya biyo baya?”

Hayatudden ya tambayeta disha kuwa da mardiya in banda faman sauke ajiyar zuciya babu abinda suke aikin yi.

”Hmmmmm kude Ku bari da masu kidnapping mutane na hadu, ihu na kuma da kuka ji kidnapping nawa suka so yi Allah kuma ya kubutar dani”

Da wata kafurar harara mardiyya ta bita tare da furta. ”Dama sun dauke kin Wllh da an rage mugun iri”

Wani Dan banzan kallo meerah ta watsama mardiyya tare da fadin ”Nifa idan na Rena kasuwa ko sautu bana mata, haka idan akace mutum kwakwalwar kifi gare shi to bana tayawa bare nima na samu nawa rabon na toshewar kai!”

Ta fadi tare dajan wani mugun tsaki.

Fadane ya so ballewa tsakanin mardiyya da meerah amma dai Allah yaso be farun fa. Ta hanyar shiga da hayatudden yayi.

AK

Wuraren 4:30 na yamma yatashi awahale domin samma ya manta da batun ganawar da akace zaiyi da kamal Rano. addu'an tashi daga bacci yayi kafin ahankali ya sauko daga saman clean royal bed nashi. juyawa yayi ya kalli agogen dake bed side nashi yaga karfe nawa ne yanxun, ganin shida saura ne ya sanya shi tashi a hanzarce tare da nufar kofan bathroom ya shiga, wani irin hadadden babban bathroom ne mai hade da closet an raba wajen part biyu bangaren dama wani irin hadadden closet ne komi na wajen blue and white ne, ga kaya kala kala dake jikin hanga ga kuma yar stool a tsakiyar wajen sai bangaren haggun kuma koface wacce bayi ke ciki bude kofan yayi ya shige bayan ya zame kayan jikinsa ya zira bathrobe.

Yay kusan 30 minutes kafin yafito daga bathroom din sanye da wasu lafiyayyun Riga da wando sai yar gadon wato pcarp daya daura gashin nan dake walkiyar kyau da baki ta zuba har kasan keyar.sai nose mark da bakin safa akafanshi sai uban kamshi yake, jinginar da kanshi yay ajikin bangon dakin kafin ya dago kai ya dunkule hannu ya daki bangon dakin da karfin bala'i yana tsaki ganin hoton fuskar wannan fitsaratun a cikin kwayar idonsa tana yimay rashin kunya.

”damn it” ya fada fuskan mace bai taba tsayamai arai kaman na yarinyar nanba but why?! Kiran sallan dayaji daga masallacin anguwar ne yasa ya mike tsaye, wasu tausasan slippers ya zira da sauri ya bude kofa yafita daga dakin, yana sakkowa arms yayi saurin mikewa sauran kuma suka rufa musu baya zuwa masjid danyin sallan magrib. Basu dawo ba saida akayi sallan isha'i dama kuma al'adan shine baya dawowa daga masallaci idan anyi sallan magrib, saida wani kwakwkwaran dalilin. Kai tsaye stairs yahau ya bude kofa ya shiga dakinshi mayar da kofan yayi

ya rufe harda saka key ya jingina da kofar yana sauke ajiyan zuciya,ahankali ya daura hannunshi kan heart dinshi da duk single beat remains him of her in his arms, ahankali ya daga kai ya kalli plain sky blue chiffon curtains din dake jikin babban window dakinshi dake kadawa sosai sakamakon iskan da akeyi na hadarin da yama samaniya kawanya ta hanyar yi mata ado da gajimare, garin yay duhu sosai kaman irin tsakar dare din nan sabida hadari sai walkiya sama take, ahankali yatashi daga jikin kofan yafara tafiya kaman kwai yafashe mai aciki yay wurin window ya tsaya ahankali ya mika hannunshi ya taba labulen slowly kafin yakai dayan hanunshi yasa duka hannayen shi ya raba curtains din kowanne yatafi bangare daya hakan ya bayyana window daya ya dan budu kadan, hannu yatura ya bude window duka yadaga kai yana kallon sama, bai damu da ko iskan da ake kadawa ba irin me kurar nan kan iya shigar mai daki ko ido bs, shiru yayi yana kallon sama iska da kamshin kasa dana trees yawani irin blowing suna ratsa duka jikinshi suna karasashi jin wani iri da baitaba jin kanshi aciki ba, ahankali ya mika hanunshi ya fitar dashi waje ta window yana feeling yanda iskan ke dukan hannu dan yayyafin da aka fara na zuba akan soft kyakykyawan hannun shi, hannun ya kafe da ido jikinshi namai wani iri tuno yadda ta rike hannun kafin ahankali ya furta ”what is happening to me?, me zubin kazar mayu”

Inba mayta ba ina ita ina shi ma me hadinsa da ita? Da baya baya ya koma yana kaiwa zaune a bakin bed, sosai Michel dake tsaya daga bakin kofa yana ta famar yimay knowkin don kawo mishi dinner na dare.

Amma haka wannan Dan bawan allan ya share yaki ya tashi ya bude. Dole sai komawa yayi da abincin don yasan ai yana da dangin su snacks da chocolate a cikin deep freeze nashi dake bedroom din....

Misalin sha biyu da kusan rabi na dare wasu motoci guda uku suke tafiya akan shimfideden titin inda motocin suka fiti daga wajejen daji dajin gefen hanya, kai tsaye suka yanki hanyar dazai sada su da airport.

titin shiru sosai yake babu wasu motoci dake wucewa banda su haka babu motsin ko wanne rai me numfashi a cikin tsakiyar wannan dare, benz guda biyu ne suka saka wata black din jeep a tsakiyan su me tinted windows. kaman daga sama power bike din Ak ya yanko daga cikin wata siririyar hanya da wani irin fitinannen gudu, gaban wadan nan motoci ukun yasha rike hanun bike din yay da hannu daya ya janye dayan hanunshi daga dayan hanun bike din yakai hanun tabayan wandonshi ya ciro karaman bindigar shi daya saka mata silencer abakin sabida kar dai kara. A kuma daidai lokacin motocin su arms suka kayo wurin suma, domin satar hanya yayi su kuma dake ankare suke da duk wani motsin uban gidan nasu ne, ya sanya suka rufo mai baya ta cikin budaddiyar hanya.

Kallo daya yama motocin su arms ya dauke kai, be fasa ba ya saita bindigarshi tare da harbe tayan jeep din tsakiyar,

ya harbe na jeep.

Wani irin juyi motocin motan ta shiga yi sakamakon fashewan tayan a guje mutanen dake sauran motocin suka bubbude motocin suna fitowa a rude domin bama yan uwansu dauki.

Kai tsaye wajen motar Farouq audu bashasha suka nufa da suke protecting suna gyara bindigar su batare dasun damu da jinin da jikinsu ke yiba. Koda suka karasa gaban motar saidai me?, wayammmm ba farouq a cikin motar babu dalilinsa daga shi har yarinyar da zasu bar kasar da ita bisa umarnin mahaifinsa audu bashasha. Daya bukaci da yaron nasa ya taho masa da RIYYA din cennn kasar India inda yake jinyar kansa.wannan shine makasudin fitiwar su kenan a cikin motocin.

”wat is happening?” daya daga cikin yaran ya tambaya ya tambayi sauran waima me yake faruwa?. Hhhhhhh Ashe her boss in naku sleeping powder ya bade shegu dasu a lokacin da suka yunkuro da niyar kaima ogansu dauki. Kowa sai ya shiga waige waige sai kuma dukansu kusan a tare suka hade baki wajen furta

”WHAT?”

Da karfin masifa ganin hasken rana a akan idonsu, saurin kara mutsitstsike idanunsu suka shiga ganin dai tabbas hasken rana ne ya sanya daya daga cikin yaran furta.

”Impossible”

Da karfin gaske, in banda rainin hankalima taya za'a ce haka ta faru dash to waye ya musu wannan aikin?, *ÊÀGLÉ ÆK* Idon Sa yakai kan kan dan note din dake dauke da sunan ak din cikin salon burgewa akayi shi akansa rubutun.

Wani ihu ya sanya yana wawuro Dan sauran note din tare da kukuruwa yana matse note din akan tsakiyar kirjinsa.

Sai kuma ya ware ma yan uwansa note din Yana furta *ÆK* da karfin gaske.

Duka a tare suka dune shi ”Yeah wannan aikin bana kowa bane sai tantirin tantirai, nifa Wllh da zanyi ido hudu da wannan ak din ba abunda zai hanani rungumesa harma na furta masa *I LOBE YOU*”

Ya fadi yana kara nade note din a cikin duka hannuwansa biyun.

Gudu take sosae akan Pawer bike ride dinsa motocin su arms na mara mishi baya suma a mugun gujen. Suna kaiwa cikin hadadden mention dinsu kai tsaye samansa ya haura.

Arms ne da yake dauke da Riyya ya shimfideta akan sopar Palon tare da furta

”RIYYA? RIYYA!!! Weak off”

Shiru babu alamun ma tana jinsa ganin ko motsi taki yine ya arms yakai zaune kan sopar shima dago kanta yayi tare da tapping fuskarta adan rude yace

”RIYYA! Hey Riyya”

Sai kuma yayi saurin kallon axton tare da furta

”get me the water pleaseee”

Ya fada da karfi domin shi kadai yasan irin halin da yake ciki na tashin hankali.

Fesa mata ruwan sanyin da axton ya kawo masa yayi. Wani gauron numfashi ta kawo a wahale tare da bude kyawawan eyes nata.

Akan Armstrong ta fara sauke ganinta.

Ai da mugun gudu ta rungumeshi tare da fashewa da kuka tana fadin.

”YAYA!!!”

Da sauti me karfin gaske tana sake cusa kanta cikin kirjinsa.....

BY AMMEY LAYLERH

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page 35&36

#AK POV

#MEERAH RIYYA join

#kamal R

#Curruption

#POVERTY's

#Deep friendship

#playful

_____

Kano

____”Baban Mariya har yanzu ba'a dace ba ko?”

Yar matsakaiciyar matar ta jefawa mijinta tambayar cikin nuna alhini karara. Ijiyar zuciya ya sauke tare da fadin.

”Ban samu ba su'ada” ya fada cikin rashin jin dadi da mutuwar jiki. Kallonshi tayi cikin tsananin tausayawa itama, kallonta yayi ganin yadda take kokarin maida kwallar da suka mata ido. Cikin tsananin tausayinta dake cike a ranshi ya furta.

”Na tambayi duk wanda na sani amma ga baki daya kowa yaki taimakona!, damuwata itace abinda ka Iya faruwa da kuma me gobenmu zata haifar mana”

Hannuwanta da suke manne a cikin juna ta matse sosai tana son hana rauninta bayyanuwa a gaban adalin mijinta, domin karya ga rauninta hankalinsa ya sake tashi fiye da yanxun. Sama ta kalla cikin raunin murya da nuna jarumta tace.

”Àduk lokacin da Ubangi ya jarabceka ka mika al'amurranka gareshi kawai. Anan ne zaka gane cewa lallai da akwai dalilin daya sanya ya jarabcekan”

Wasu hawayene masu zafin gaske suka sakkomai

"makomar mariya shine abinda yafi komi tsaya min a cikin rai da rayuwana!, ina tsoron a karo na uku aurenta ya fasu akan rashin kayan daki umayma"

malam yusufa ya fadi cikin nasa hawayen daya gaza boyuwa a garesa.

murya a tausashe wacce ya kira da umayma ta furta . "kada ka samu damuwa malam insha allah allah shine zai kayo mana dauki lokacin da bamuyi zata ko tsammata ba bi'izinillahi"

"amma ke ina iya ganin damuwa akan fuskarki umaymatu, kuma kinsan bazan iya juriyar hakan ba"

da sauri ta juya tana barin wurin domin kada ta raunatawa mijin nata zuciya.....

kanta ta hade da jikin bakin kofar da take tsaye hawaye masu zafin gaske na zubo mata. tana tsananin umminta da babanta, wai sai zuwa yaushe rayuwa zataji kansu su fita a halin kani kayin da suke a ciki na halin rayuwa sai zuwa yaushe suma zasu dandani irin yadda zakin rayuwa yake?.

"Ya Allah!"

mariya ta furta cikin wata iriyar raunatacciyar murya. sallan magriba da aka kira ne ya fitar da baban mariya cikin tawakkali da karfin zuciya.

Cikin sanyin halinta kamar koda yaushe anutse ta mike kanta duke a kasa, saidai ahankali take matse lips dinta da kyawawan teeth dinta. kai tsaye gaban dan karamin fanfom dake gaban bishiyar mangoron gidan ta nufa....alwala ta daura tana jin duk ma yanayin baya mata dadi baki daya.

shi kuwa malam auwalu da mutanen anguwa ke kiransa da baban mariya bayan idar da sallar isha'i, dake shine lilaman masallacin anguwar yana zaune har saida kowa ya gama fita kana ya mike da zimmar fita. wata farar embulons ce ta fado daga saman jikinsa cikin rawar jiki ya shiga waige2 saidai baiga kowa ba....

saurin fitowa yayi a masallacin da shi ya fara cin karo,wani irin dafe kansa malam yusufa yay. me yasa aduk lokacin da yake da bukatar taimako sai shine kadai me taimakonsa.

jiki a sanyaye ya karasa xuwa gaban farar motarshi da yake tsaye, sanye yake cikin kakin yan sandan shi kamar kullum. "Na rasa wanda zai taimakeni amma ba wanda ya taimakamin, duka na tambaya haka ban samuba! amma kai bamma tambayeka!" ya kasa karasa maganar shi sabo da kukan da yaci karfinsa.

"Aina riga na fashimci komai dana kalli cikin idanuwanka. wannan ba komai bane"

inspector KAMAL RANO ya fadi

"bansan ta yayene zanyi wani abu game da yata ba. ban kuma san da wanne irin idon zan dubesu ita da mahaifiyarta na fada musu cewar auren ya fasaya!. bayan fitowana daga cikin gida zuwa masaaci. KAMAAL?"

Malam yusufa ya kurayi sunan shi cikin karyewar zuciya. cikin tsananin.zafin dake narka kirjinsa ya furta.

"A yau da kai danane dana zartar maka da wani hukunci kai tsaye! ko kuma in baka umarnin aikata min wani abu"

idonsa daya tara kwalla ya dago yana kallom baban mariyan. kafin cikin muryan da kai tsaye ba zaka iya tantance taba yace.

"Ya kuma zakace haka baba? kenan niba danka bane kome?. matsayinka a wurina ya wuce makwabtaka ni KAMAAL IDREES RANO A MATSAYIN MAHAIFI NAKE KALLONKA, ka bani ko wanne irin umarnine ni kuma in aiwatar maka shi cikin sauri da tsananin biyayya"

hawaye da kuka ne suka zowa baban mariya lokaci daya, cikin jin yakini da kuma karfin zuciya ya furta.....

"KAMAAL A MATSAYINA NA MAHAIFINKA NA BAKA UMARNIN AUREN MARIYA!"

wani irin dokawa kirjin kamaal yayi amma saiya danne hakan cikin cikakken bin umarnin nashi kamar yadda ya daukar masa alkawarin ya furta.

"A MATSAYINA NA DANKA NA AMSHI AUREN MARIYA, AMANA SAI DAN AMANA! HALACCI SAI DAN HALAK, zan amshi wannan auren bisa wakilcin waliyina ABDOUL-MALEEK"

Da karfin gaske ya rungume kamaal din yana fadin "nagode na gode nagade kwarai da gaske bana da haufi akan baka auren mariya da nayi kamaludden uban daraja uban kamala"

.....Umayma cikin karfin hali ta gama kammala girkinta bayan fitar mijin nata. har zuwa yanxun da bayan tayi sallar isha'i take zaune gaban dakin malam liman, da abincinsa da take jirayin shigowadsa!

shigowar malam cikin tsantsan fara da kuma murmushin dake kwance saman fuskar sane ya sanya itama nata murmushin fita da sake fadada, "Alhamdullih umayma lallai Allah maji kan bayin sane ne, cikin hikimarsa da buwayarsa ya mana canji da mafificin alkhairinsa"

ya fada yana kaiwa zaune kan tabarmar da umayman ke zaune, sai kuma ga kai dubansa dakin mariya tare da kwalla mata kira. "MARIYA"

"na'am baba!" ta amsa shi cikin faduwaf gaba tana fitowa tare da tsugunnawa a gaban mahaifan nata. sannu da zuwa tama tayi mar kallonta yayi tare da mata nuni data zauna. zaman tayi tana sunkuyar da kansa kasa.

"kaddara wata abace me tsanani haka kuma me sauki! sannan kuma wata abace da ba'a iya ganin launinta da ido, hakanne ma yasa ba'a iya sauyata daga mummuna zuwa kyakkyawa, acikin kowanne rayuwar ɗan Adam akwai salon tarin ƙkaddarori masu tarin yawa, akowacce duniya akuma koda yaushe kaddara tana tafiya ne daidai da rayuwa. Sannan kuma babu wani bawa wanda ka iya gujema tarin ƙkaddarorinsa. haka kuma ana haifar kowanne bawa ne da salon tashi ƙkaddarar, kisa a ranki shima musan baya cikin kyakykyar kaddararki mariya. domin kuwa iyayensa sun janye kamar yan baya, amma da ubangiji ya tashi miki zabinsa saiya sanja miki da mafificin duka sauran samarukan da suke fasa aurenki. data tashi saiya baki kamaludden me kamala, me karamchi, me nagarta ki amshi wannan zafin a matsayin zabin ubangiji domin kuwa shi kadai yasan manufarsa akan hakan"

ita dai tunda baban nata ya fara fadar maganganunsa bakinsa kawai taga yana motsawa kamar sauran lokutan baya. Ita kuwa meta rayuwa da take juyin wainar masa da ita, daga wancen kasko zuwa wannan kasko? kodai ta aikata wani zunubine da yake ta bibiyar rayuwarta?.

KUWAIT

***** *****

Cike titin yake da motoci ba komai ya haddas hakan ba sai wani uban shegen go slow da wata ƙshegiyar bakar mota mai kyan gaske ta hada kirar lexus. anyi crossing dinta akan titin yadda ta rufe titin completely duk glasses dinta tinted ne. dan haka ba'a hangar wanda yake cikin motar,mutane sai hayaniya suke.

kallo daya zaka ma motar kasan ba dan karamin kudi aka narka wajen siyar motar ba.

gurin ya cunkushe mutane sai hayaniya suke yi,abu mafi ban mamakin shine normally gurin yake babu traffic, murfin wata farar mota aka bude wata kyakykyawar matashiyar budurwa ta fito sanye cikin shigarsu irin na larabawa. bakar abayane a jikinta tayi rolling da siririn vail abayar, sai bakin shadow data sanya a fuskanta da alamu sabo da kare hasken rana ta sanya shi.

kai tsaye inda akayi bloocking hanyar ta nufa a nutsenta.

cikin harshen larabci wani matashin balarabe ya furta "yan kibi a hankali mutumin is very dangerous, shegun kasar kuwait kenan ake magana anan" ko inda yake bata kalla ba saima ci gaba da tafiyarta da tayi.

wasu shegun manyan motocine guda shida suka ratso ta cikin titin da wannnan motar tayi blocking hanyan, dole sukaci burki suma kafin mamallakin motocin wanda yake sanye cikin wata iriyar shiga ta alfarma ya bama daya daga cikin tight security'n umarni ha duba ya gani mene ya haddasa wannnan go slow din.

"ba bukatar a duba ZAID EMAAR'S ne"

mahboob ya fadi dake zaune a kusa da sit driver.

"innalillahi yanxun dama gantalewar zaid din shima harya kai haka? bayan shigo mana gida a bugu banda yawon club's club's dinsa ashe harda tarema mutane hanya ya iya!"

cewar MOH JIDDO da take zaune a kusa da AL-HUSSEIN EMAAR'S.

a mugun fusace AL_HUSSEIN ya bama wannan tight securityn umarnin

su farfasa motar su fito dashi suyi masa shegen duka su jashi su kaisa gida.

cikin cika umarnin alhussein suka diddira a motocinsu suka nufi inda motarsa yake.

dai dai windown driver wannan mudurwar tayi knocking a hankali zaid dake kwance cikin motarsa ya kure A/CN yana latse latsensa a wayana ya dan dubi inda ake knocking glass na motornshi.

da sauri ya sauke glass din fuskarsa ta bayyana dauke da murmushin mamaki ya furta.

"Hey JESRA me kike yi anan?"

dan bata fuska tayi tare da daura hannayenta akan windown tayi tagumi ta furta

"unguwa zanje kuma yayana ya tare min hanya yaya kenan?"

ta fadi cikin dan bata fuska kansa ya ciro ya kalli dandazon motocin. da suka taru a tsakiyar titin tare da sakin wani dan murmushi kadan ya furta

"lallai kice yau dara taci gida kenan?"

ta fadi daidai lokacin da security'n suka karaso wurin. Tafiya suka yi har zuwa bakin motar saidai ganin jesra tsaye a bakin motar ya sanya suka ja burki. domin su basusan waye a ciki ba sudai umarnin su may duma kawai aka basu.

Bai san da zuwansu ba sai ganinsu yayi a gabansu.

wani shegen kallo zaid ya jefa ma securityn tare da furta

"Duk wanda yasa darty hands ɗinsa ya taba ni kuwa sai na kwantar dashi a gadon asibiti kuma ya bar aikin sa kenan har gaban abada, bama a cikin gidanmu ba harma kasar baki daya saina lalata duk wani offer nashi na samun aiki"

ja da baya security'n suka shigayi suna barin wurin baki daya.

jesra ce ta furfa

"me yasa har abada a jawa oummey magana kake? bawa kai ba bawa shi wancen din ba! zuwa yanxun ya kamata ace kun fuskanci rayuwa daidai akie"

ta fadi tana shiga cikin motar woyarta dake cikin hand bag dinta ta ciro ta kira driver'nta tace ya koma gida. Mazaunin driver ta zauna tana zare glass din idon ta ko kallon inda yake batai ba ta furta.

"Ina muka nufa?"

..shima bai tashi daga kwancen da yake ba ya furta.

"BELOW SNOW muka nufa"

"gun wasa kuma me zakayi a wurin wasa?"

"AIKI"

Ya bata amsa a takaice tare da furta "ke ina kika nufa"

"four seasons hotel alshaya na nufa tare da willtopin fun tiki back future"

wani irin dan yatsine fuska yayi tare da furta.

"nafa kusa janye wannan shegen aikin naki JESRA na sanya kai a hadari kina matsayin mace"

saurin kallonshi tayi tare da banka masa harara ta sanya hannunta ta dunguri keyarsa tare da fadin.

"to bismillah sa idanawan duniya kai duk abinda kake oummey ko paah basuce sun gaji da kai ba saini?"

ta fadi daidai tana shan kwanar below snow din da suka kawo. a bakin wurin ta ajje shi tana fadin

"bari na wuce domin nine nake son fara haska latest amazing story innan akaf kuwait"

"take care ki kula sosai fatan nasara uktie"

zaid ya fadi yana shigewa cikin gun wasa.....

POLAND

Salman pov

A lullume garin yake sakamakon yanayin sanyin da garin yake da, Hazo ne ya yi wa samaniya ado ga iska mai ƙkarfi dake ta shi tana ƙkara haddasa sanyi irin mai shiga jika nan, yayyafin dusar kankara aka fara wanda hakan a wurin mazauna garin ba komai bane.

A wurin bako kuwa wannan sanyin ka iya haifar masa da wata illar.

Analya's hotel

kayataccen hotels ne wanda ba kafasai people ke iya zuwa hotel din ba sai wanda yaci ya tada kai ne kadai ka iya xuwa hotel din analya's.

3:28pm cikin tsakiyar talatainin dare ne mai dauke da tsananin duhu tare da cushewar yanayi kasancewar babu yalwar iska ko kadan dake kai komo acikin daren,yayinda ko ina ya zama shiru babu motsin kowa ga wadan da suka so hakan.

baki daya garin bama iyaka cikin hotels din ko ina ka ratsa hasken street light ne tako ta ina, wani irin sautine yake tashi daga wani sashi na daga cikin jerin rooms din dake cikin hotel din. sautin sosae yake tashi a cikin room din sautin ko nace growing din irin mara dadin jin nan ne.

Salman ne kwance da wata black american wanda suke shike ayarsu a irin duniyar su ta marasa kan gado da aikata sabon allah.

wani irin shafan saman kirjinta xuwa fuskan salman yayi, ita kuwa wasu shudaddun idonta ta dago da suke a rikide, cikin wani irin shegen salo ya ziro tongue nashi ya dan lashi saman kirjinta tare da saman idonta yana sake fxxk upp nata. wani irin gauron numfashi taja tana sake selling kanta zuwa gare shi taja dan jan yaji kadan.

shi kuwa ogan sautin nishin sane kadai ke fashi sai zufan dake faman zubo mishi tako da ina, ita kuma sai sharce masa take da mini towel din dake hannunta.

(Wa iya zubillah ubangiji ka shirya mana dukkan yan uwanmu musilmi a duk inda yake)

10:12am

Sanye suka fito a tare manne da juna ita kuma sai wani takwar kwasasa kawai take yimay ita ala dole ya gama gajiyar da ita.

cinyanta ya shafa da take manne da nashi cinyan tare dan kallonta kadan yana fadin.

"ke dai kin fiye raki ne kawai dolly,amma kwata kwata round 4 kawai fa nayi"

a iskance ta dube shi tana tura masa pink lips dinta tana sake shigewa cikin jikinsa. A gefen bed suka zauna a tare shida kansa ya shiga shafa mafa mayuka. Woyar sane tayi ring hannunsa ya mika ya yanwo wayar sunan daddynsa daya gani ne ya sanya shi daukan woyar nasa da sauri tare da mikewa yana barin wurin. "Daddy's boy ina son duk inda kake kayi kokarin dawowa 9"

Saida yadanja numfashi kana ya iya furta. "Alright mebi ina tafe a cikin week din nan, domim har yanzu branch din da nake ta kokarin ganin na hada tare da mutanen nan be faru ba"

"Dakyau yaro ne na sha'afane ma da zancen branch din ne ma wllh! Kadai san duk yadda zakayi kayi ka tabbatar muna da shere a cikin company'n (E)Graup din nan daddy's boy"

Dan shafar sumar kanshi dake adan hargitse yayi tare da fesar da numfashi tare da cewa, "Don't worry daddy zanyi duk yacce zanyi ganin mun hada hannun jari da mutanan nan"

"Fatan nasara yarona"

Daga haka suka yanke woyar shi kuma ya koma ciki suka karasa kimtsawa shida dolly suka fice yawan shan iskar su da shan chocolat.....

LAGOS

ÆK

Zaune yake daga bakin kayataceccen pool din dake kewaye da flowers kawawa masu launi daban². kafafunsa zube a cikin ruwan yana wasa dashi, hannuwansa duka biyun ya hada ya tallafi kasarn keyarsa lumsassun idonshi a rufe ga wata kalar iskar da ake kadawa me dan karen dadi. Sai hakan ya bada wani kalarn yanayi na daban. yanayin da zaka so kasancewa a gurin idan kana cikin ko wane irin hali zaka iya zama gurin dan nishaɗi, jikinsa sanye da kananun kaya na shan iska blue inda colorn yayi matukar haskaka kyakkyawar fuskarshi. dogon hancinsan nan irin na larabawa da ya kara fitowa dodar, lallausan gashin kansa kuma yana sanye ne cikin Shower cap gudun kar ruwan ya jika may gashin.

Ware idanunsa da suke a lumshe yayi sakamakon *ORCAS* din da yaji yana wasa da kafansa. Nutso ya danna a cikin ruwan kai tsaye cikin yanayin nishadi, saman orcar din ya haye kamar jira katon kifin ya danna iyo dashi harcen karshen ruwan.

Wasa yayi sosae a ruwan wanda shi kansa yama manta rabon shi da cilling irin haka.

One hrs

Kkarfe 5:26pm ya fito daga bedroom ɗinsa sanye yake cikin wasu American suit coffee colour ya tufke gashinsa da wani mitsil din ribbons kunnensa ɗaya ɗauke da diamond ring gold color.

kallon parlon ya yi akan Riyya dake tare arms ya fara sauke idonsa, zaune yakai kan luxury caution din da Riyya ta karkade may. Sai da ya zauna kafar nan daya kan daya kana ya dubi Riyya cikin muryan no nonsense ya furta.

"Yau zaki ga Tambuwal na rigada ma shirya miki fitan!"

Yana gama fadin haka ya gyara zaman Bluetooth ɗin dake makale a kunnensa da dukkan alamu waya yake mai muhimmanci.

Arms ne ya shigo sanye cikin bakaken suit a gajiye ya karaso tare da zube wasu files a dan table din dake gaban ÆK din, "Duka komi da komai ne a ciki boss"

"Da kyau lion ka shirya domin tare nake son ku fita aikin nan tare da Riyya right"

"It's okay don't worry EMAAR's"

Wani shegen kallo AK ya watsama Arms, wanda ya sanya arms barin wurin a guje yana rike dariyarsa dake gab da kubce mishi. A ransa yake tunano wasu abubuwa masu yawan gaske cikin ranshi, ya sani Allah ne kadai ya kaddara sanadiyar haduwarsa da AK, wanda yake ma kallon yar uwa, dan uwa, kai uwar ma kanta da uba. Duk wadan nan matsayin ak ke amsawa a gareshi yana ji a ranshi zai iya bada rayuwarsa akan ak din. Guntun kwallar da suka sakko masa ya dauke yana karasa hayewau upsaid nashi.....

Isa masu

Wani kalan kayataccen Murmushi ne kwance saman fuskansa, yana kallon gudan jininsa daddy's boy dinsa wato salman. "Kullum maganar aurenka sake kusanto kanta garemu take banji kuma kana wata magana ba dangane da auren ok"

Wani shegen murmushi ya salman ya saki tare d shafar kasan keyarsa sai kuma ha furta.

"Daddyyyy!!!"

"Uyummmm daddy's boy ya ake ciki?"

Wani kalar karyar da wuyansa yayi a shagwabe kuma ya ce.

"I'm very happened dad yanxu nan da 2 week merrah Amatsayin wifey na take I love you so much daddy" ya fadi tare da rungume dad nashi.

Da wani irin kallo me kama da harara momm ta jefi salman dashi. Mtsss taja tsaki tana barin wurin, domin yar yayarta taso ya aura da harya amincen sai kuma daga baya da dad nashi ya shigo da maganar auren merrah ya kiya daga baya. Duk da kallo suka bita daddy kuwa bakinsa ya tabe irin ko a jikin san nan.....

MERRAH POV

By AMMEY LAYLERH□□

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~□ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... □~*

Page 37&38

#He has hunger for power, He has lust for money

#Deep friendship

#playful

#Hope

#Courage

#Humanity

#Survival

#Inspiration

_____

MERRAH

Tabbas wata tafiyar bata sauri bace kuma bata nawa bace musamman tafiyar dake cikin ko wanne zanen ƙkaddara toh baya bukatar sauri ko nawa. Da anawa ganin gani nake kamar zancen auren salman dake kaina ba tabbatacce bane, amma akwana a tashi sai wayar gari nayi da zanen kaddarar aurenmu daya zana kanshi da kanshi,wanda ya rage mana yau soran 6 days kenan daurin aurena ni Maryam Abdullahi gwani.

A sautari wasu lokutan mutanen da muke musu kallon bango ko jigojin rayuwar mu suna iya zama sune masu nisantar mu, mutanen da bamu san sun damu da mu ba kuma su iya zame mana bango majingia. Ba zan iya bama kowa amsar da take cunkushe a cikin rai da rihuna da kuma zuciya naba!. Domin Sunan shi kadai shine ya sanja zanen kaddarana, kuka na ya kasance a boye bayan murmushina. tambarin da kaddara ta bani ya sani kara ninkaya a cikin tafiyar zanen wata ƙkaddarar izuwa wata alkaryar ta daban.

Kaddara wata abace wacce bawa baya iya tsallaketa kowa da kalar nashi salon ƙkaddarar haka kuma kowa da akwai silar nashi ƙkaddarar.

Haka ba'a iya guje mata domin ita ta kasance rubutacciyar aba ce tamkar zanen dutse a cikin kirjin ko wanne bawa. haka take duk yanda zakayi bazaka iya gogeta ba no matter who are you or what you have nobody can change her destiny either good or bad.

Ayau daya kasance ranar lahadi 1 ga watan takwas na OGUSTA dangin salman suka kawo jibgin kayan akwatunansu gidan. Kayane iyaka kaya wanda mutanen gidanmu harma da yan anguwa zancen kayan ake, media kuwa babu inda zancen be zaga ba domin magana ake ta Ajebor irinsu salman.A lakacin dana budi ido naga yadda pisc nawa suke yawo a media Raina ba bakaramin baci yayi ba, domin abu na farko danafi tsana kenan yada photo's nawa ya media.

Martanin kowa wannan lokacin shine ashe dama shine dalilin daya sanya kullum nake makale a cikin nikaf.

Ashe nasan abinda nake ma kaina tanaji tunda gashi ata sanadiyar auren dan shahararre kuma tycoon isa manu empire pisc nawa sun gama karade ko ina.

Masu iya magana sukance ba iyaka yaudinka shike tabbar maka da nasarar goben kaba, haka zalika yau dinmu ba itane madubinmu goben mu itane madubinmu abin alfarinmu...

Nayi kuka, Nayi kuka Nayi kuka wanda ni kaina bansan iyakar shiba a wannan rana.

Karin wani abin mamakin kuma idan nace muku Anne sammm bata farin ciki da wannan auren karkuyi mamaki ko al'ajabin hakan.domin memakon kaga tarin farin cikinta saidai kaga akasin hakan, Ko yanzu ma kwance nake tarin abubuwa sunbi sun cunkushe a tsakiyar kirji. Ganin dumuwa na neman sanya ni a wani halin ne ya sanya ni bude DATA na, WhatsaAp nawa na fara lekawa bayan sakwannin mutane dana dan dudduba saina koma kallar status na mutane. Bear man shine status na karshe dana kalla wanda ya bani mugun haushi sosae, Pisc ne marasa kan gado yayi status dashi nace kunsan waye me wannan sunan Salman!.mutumin dake dab da zama mijina shine me wannan sunan, don ni a zahirin gaskiya idan na kalleshi da dan biri yake min kama karfa kuce wai don bana son shiba.

A ahh bawai don bana son shi bane har zuciyana da gwaggon biri yake min kama.

Fita nayi daga whatsaAp din na koma Facebook nan na dan dubba abubuwan da suke wakana a median kana nayi search na sabon littafin *SPECIAL*

TA DABAN

Na AMMEY LAYLERH da zata fara domin kullum saina duba amma haryau bata fara ba, tun akan litattafanta uku dana karanta na mato akanta Wato litafinta na.

KAREN BANA

JALAAL AREEF

KAUNA BIYU

Sai kuma wani dana fara karantashi amma be zama complete ba wato *PRINCE SAPWAN*

{Sanyi ya haifa wuta }.

Saidai kash yau din ma banyi dace ba har yanzun bata fara ba mebi domin tun daga dandanon kadan daga cikin labarin na gane zai bada fire sosae.

Haka na hakura na sauka tare da kashe data na ammafa ban sauka ba saida na ajje mata message a facebook dinta don bana da whatsaAp number nata.

Sallamar da Hajiya umma ta rafkone ya sanya ni tashi zaune ina amsata tare da kashe data na. Karasa shigowa tayi gaidata nay ta amsa ni tare da tambayar inda Anne take, ganin bata parlon kallonta na danyi sai kuma na sunkuyar da kaina da hannu na mata nuni da bedroom dinta.

Meeting room

Wani irin hadadden parlon ne mai mahaukacin girman gaske parlon ne mai kamada wata fadar kana ganinsa kasan wasu ishasshun mutanene ke rayuwa a ciki, akalla mutanen dake zaune a cikin parlon sunkai wajen su ashirin da biyu, ko wannensy zaune yake akan street table din gaban ko wannensu dauke da juice da gorar ruwa sai dangin su snack.

Manyan masu kuɗin mu kenan manyan kuma yan siyasarmu ne ake magana. A tsakiyarsu ga system jone da dukkan alamu video call suke, wani babban mutum ne kwance jikinsa sanye da uniform irin na marasa lafiyar nan. Zaune ya tashi cikin tsananin fushi kafin cikin miryan fusata ya ce.

"Na rasa mema kuka tsaya yi dahar yanzu baku kawar da wannan shegen yaron ba, tsananin fusata kukeson ta bayyanane kawai manu!, in banda haka ace yarona yana wurinsa duk kaninku babu wanda yayi wani yunkurin kwatar shi daga cikinku Right?"

Tambuwal ne ya dube shi shima cikin nashi kalan bacin ran ya furta

"Kafi kowa sanin wanene wannan yaron bashasha kai a tunaninka zuba ido mukay kenan kome, toba shiru mukay ba karka manta cewar governor da minister da kyar suka sha, zafin kan yaron ni kaina na bani tsoro

ɗan zafin kaine dabi'arsa kuma kan firgitar dani sammm baka taba gane alkiblarsa baka taba sanin koshi ainihin wanene shi!?”

" Saime! Nace saime dan dabi'arsa na firkita zafin kansa kuma kan baka tsoro toni sammm kwata² bana tsoron haka, nima dan zafin kanne aiiiii ko ka manta waye Audu bashasha na tuna maka"

Ya fada a fusace cikin fusatar kanta.

"Duk ba wannan bane ya taramu muyi zaman daya taramu kowa ya kama gabansa, yanzu abu tsaye a raina shine bikin yarona idan an gama komai ya biyo baya. Kuma idan baku manta ba ji ina mun kashe wancen maganar tunda ita kanta yarinyar tana dab da zama tamu ne"

Ijiyar zuciya duka suke saukewa kafin ya dago kaida ganinsa kaga wanda baya cikin hayyacinsa, "To wai ma bikin saura kwana nawa ya rage mana ne ma?" Ya tambaya yana komawa kwance domin yar hayaniyar nan harya fara hawar masa kai.

Daga nan suka shiga tattauna manyan maganganunsu na sirri daga haka zaman nasu ya tashi. Domin tanbuwal har Allah Allah yake su tashi domin yana da wajen zuwa karfe taran dare.

A slowly katuwar bakar jeep din ya parker a wurin adana motoci na cikin Park din, Sanye ta fito cikin riga da wando bakake sai wata falmaran Ash color data dora saman riga sa wandon. Idonta toshe cikin bakin glass tayi rolling da siririn vail din riga da wandon wanda suka kasance disigners ne.

A hankali ta shiga karema wurin kallo, Kallon wajen kawai Riyya keyi lik kamar irin bata san wurin nan ba. iyaka haɗuwa wajen ya haɗu park ne mai girman gaske ko wanne passege yana da nashi kalan kyaun, basarwa tayi tana jingina da jikin motornta babu dadewa kuwa wata arniyar Rolls {R} Rayce blue black ta sanyo kanta cikin park din. Har dab da idan take tsaye motorn ya faka kafin matashin alhajin dake zaune cikin motar ya fito.

Jikinsa sanye cikin wasu shegun Cashmere me laushin tsiya da tsadar gaske wanda kai tsaye bazaka taba iya zartarma da kayan kudin da suka lashe ba.

Tun daga kan motarn ta fara kallon shigar shi da irin makudan kudaden da suka lasa.

Bvl $15, 000

Cartier $5, 000

Rolex $35, 000

Rolls {r} Rayce $250, 000

Wani irin numfashi ta sauke tana dauke kanta a kallonsa, yana karasowa dab da ita ya sakar mata wani tsadadden murmushi yana mata nuni data biyo shi.

Bayanshi tabi suka bi wata hanya cikin wani kayataccen special gun shan iska suka tsinci kansu, kan wasu kujeru wanda suke zagaye da wajen suka karasa zama yayi tare da mata nuni data zauna itama.

Kujerar dake facing dashi ta zaune suna zama wata waiter ta iso wuin tana basu jotter na jerin abubuwan da suke dashi. Shine ya zabi tarin abubuwan da yake so tare da bata umarnin taje ta kawo, babh jimawa ta kawo katon nrey tray xuwa kan table din dake gabansu.

kallon ice-cream ɗin merrah ta yi amma bata ɗauka ba saima wayarnta da take famar latsawa, Dan gyaran murya yayi tare da fadin "Baby ya kamata ace kinsha ko wani abune"

Ya fada cikin Kasa da murya sosae ba karya kamm jijinsa sai fidda daddan kamshi yake.

Ajje woyanta gefen tray din tayi sannan ta ɗauki ice-cream ɗin guda ɗaya ta fara sha. Har wani lumshe ido take saboda daɗin da ice-cream ɗin ya mata, hakan yasa tambuwal binta da wani shu'umin kallo kana ya sanya hannunsa ze ɗauki ɗayan, dan buge hannunsa tayi kamar irin bata sani din nan ba. Dan kadan ne ya zube a jikinsa dan sunkuyawa yayi da nufin daukar tishu tayi saurin jefa masa kwayar dake dunkule a hannunta. Dan turo baki ta yi iri cikin shagwaɓar nan ta ce

"Ayya beby ban kula bane sorryy" tayi maganar tana tura masa robar Ice cream din gabansa. Dauka yayi tare da fara sipping a nutse har wani dan lumshe ido yake domin gardinta na kai may har inda ya dace.

Cikin abinda bai wuce 5 mint ba ya tafi luuuuuuu, Arms dake tsaye bayansa ya taroshi zuwa jikinsa hannunsa ya sanya ya sakali kafadar tanbuwal din tare da ziro hannuwan tanbuwal ta cikin wuyansa. Dashi ya fara tafiya a jikinsa Riyya ta mara musu baya tamkar dama cen a taren suke.

Har bakin motarsu sukaje ba tare da kowa ya farga da abinda yake faruwa ba. Shigowarsu kenan cikin park din idonta ya sauke akansu kasancewarta mutum me tsananin karantar yanayin halayyar dan adam ya sanya kai tsaye ta gane cewar kidnapping ne sukayi, Duka sauran yan tafiyar nasu babu wanda ya lura da hakan sai ita kadai, "xcuse mee!"

Ta na fadar hakan tayi kamar mantuwa tayi ta jikin motar tawuce tare da manna musu wani abu dake hannunta, A kuma daidai lokacin suka tayar da motar suna barin wurin.

Ciki ta koma tana sake gyara zaman jakarta da daidaita nikaf dinta da taji kamar yana kokarin sarkafe numfashinta.

Kano

National Police Headquarters.

_Criminal Investigation Department (CID

Inspector kamal ne dake tsaye yaci gaba da kwararo bayanai yana mai nuni da welpaper screen din.

Hoton wani farin wani dattijone ne na'urar ta haske. Cikin tsananin sanin makamar aikinsa yaci gaba da fadin.

"wannan al'amari ba abinda za'aji ai shiru bane, tunda harya cutar da daruruwan mutane ta hanyar amfani da karfin iko hakan babban zunubi ne yallabai!. Be kamata mutum irin wannan yaci gaba da shakar yantacciyar iskar duniya ba.

Kamata yayi ace zuwa yanzu numfashinsa baya tare da gangar jikinsa, ko ace yana cen prison yana girbar abinda ya shuka! Yana yin duk wasu haramtattun harkalloli kwatsam kuma ace ya zama babban commondi of soldier's?"

Wata iskar bacin rai ya fesar tare da dora hannuwansa biyu saman desk din dake gaban yallabai din yaci gaba da fadin. " A koda yaushe damar shan iska muke basu!, shine babban kuskuren da mukeyi yallaabai a koda yaushe tazarar itace zarrarsu a garemu"

"Uyummmmm na fahimceka kamaal baka sanshi bane shiyasa mutum ne shi me matukar hadari"

Wani irin tirjiya yayi tare da yowa baya ya fuskanci yallabai din kafin kuma ya saki murmushin takaici ya furta.

"Kace bansan waye shi ba? Shiba Aihuwarsa akay kamar sauran mutane ba? Aiba daga sama ya fado ba, ka sani kotu zata iya amince da maganarka, doka zata iya amincewa. Amma Allah bazai taba amimcewaba! Idan kana ganin yafi karfin hukuma to kasani Allah ne zai iya hukunta duk wani mugu dake mulkar bayinsa. A yayinda shirun Al'umma zai zamto tsawa hawayensu yayi ambaliya tamkar tekun maliya. Ko kuma tarin radadin dake bisne a cikin zuciyar kowanne bawa ya koma makamin da zai ceci rayuwaesu Allah ne kadai zai iya hukuntawa Allah daya"

Ya fada a tsawace tare da bugar desk din yana barin dakin taron. Baki daya da kallo suka bishi officer Hassan Arwai ne ya dubi yallabai tare da fadin.

"Zafin kansa yayi yawa! Jin kansa yake a matsayin da bai kawo ba, haka daukar kansa take a matsayin zarrarsa"

"Stop!!! "

Yalaabai ya fadi domin yanzu bai bukatar su sake hargitsa tunaninsa.

"Pls every body get out"

Ya sake fadi a tsawace tare da dafe kansa da hannuwansa.

Kai tsaye gidansa ya nufa zuciyarsa na masa tsananin zafi da suya, Allah ne kawai ya kawo shi gida lafiya bawai don iyawarsa, dan yadda ya bama motar wuta kawai idan ka kalla ka tsoratama.

Ganin wata siena fake a kofar gidan shine ya sanya shi tunanin su waye kuma domin shidai yasan baya da wanda zai kawo masa ziyara, tunda danginsa sun jefar dashi gudun kada susha wahalar dawainiyarsa, Allah ne kadai ya raya shi in banda haka da bai kawo wannan lokacin ba.

Ruwa iska sanyi tsananin rana duk akansa suke karewa baya da matsugunni duk inda ya raba korarsa ake kamad kare koma yace annoba. Ijiyar zuciya ya sauke domin sammm bama ya bukayar ya ringa yawan tunano rayuwanshi na baya domin hakan tafarfasa zuciyarsa yake, kirjinsa kuma ya masa nauyin da yake gaza sarrafa kansa da fushinsa idan har beyi fashe².

A nutse ya bude motarsa ya fito yana fitowa baban mariya na fitowa daga cikin gidan kamaal din, hannunsa dauke sa tray.

Tsaiwa yayi ya fasa tunkarar gidan. Fuskansa da fara'a ya karaso har ganan kamaal din yana cewa.

"Yan uwanka ne na rano da yan gwarzo suka zo wajen ka" ya fadi yana kama hannun kamal din. "Yan uwa dai baba?, ni kuma a ina nake da yan uwa ai bana da kowa....mebi mistake sukayi ne bara na karasa daga ciki"

Ya fadi yana yin gaba.

"Harda Malam Haruna rano shima baka san shiba?" Baban mariya ya jeho masa tambayar data sanya kamal tsayawa cakk da kafafunsa. Wata zubar bacin rai na karyo masa, wato sai yanzune ma suka dashi a jerin yan uwa, kenan raina masa hankali sukai tunda har suka san inda yake zaune kai tsaye.

Cikin bacin rai yayi cikin gidan yana fito da yar karamar pistol din dake sakale a jikinsa, da karfin gaske ya tura kofar parlon wanda hakan ya sanya jama'ar dake zaune a parlon firgira.

Ganin wani matashin bazaraten saurayi tsaye a gabansu me tsananin kamanni da Suraj din sune ya sanya jikin wasu fara rawa. Da sassarfa wani dattijo ya karaso inda yake tsaye da nufin tabashi, wani irin jaaaa baya yayi cikin fushi ua furta. "Me kuke nema?wannan yaron da kuka jefar kuka guda dan kimanin shekaru goma ko wa!?, to ku sani inma shi kuke nema wannan ya dade da mutuwa, wannan dake gaban ku ba kowa bane niba kowa bane face bawan Allah wanda ya raya shi bisa

tafarkinsa na gaskiya da kuma bashi kariyarsa acikin duka lamuransa don haka I say get out in my house tun kafin ku fasata wannan bawan allah"

Hawaye sosae suke suna rokonshi daya yafe musu sunsan sun aikata kuskure amma ya taimaka ya yafe musu, wani da suke kira da kawu ilu ne ya rarrafo gabansa cikin kuka ya shiga fadin.

"Tabbas munyi kuskure!, munyi kuskure kamaludden amma ka yafe mana kowa a lokacin ya guji daukar kane sabo da gudun dawainiyarka, duba da tsananin azabar da talakan kasa yake sha. A namu banzan tunanin gani muke ba zamu iya ba kaidin zaka zame mana nauyin da bazamu iya dauka ba!, a jikin takarda naga hotonka ina gani na nemo shamsu nace ya karanta min. Kamal rano kadai daya ambata ya bani tabbacin kamal dinmu ne kamal din da kanina yamutu yabar min!, kamal din da talauci yasa na gaza daukarsa a matsayin.....

Sai kuma wani irin kuka ya sarke shi janye kafarsa Jamal yayi da karfi tare da daka musu tsawa a karo na biyu yana fadin su fuce may a gida.

Wani kyakykyawan bahagon mari baban mariya ya dauke fuskar kamal dashi. Cikin fushi ya furta " Idan har ba karya kamin ba da kace a matsayin mahaifi kake kallona to ban yarda ka kare furta ko wacce iriyar magana wa danginka ba inhar bame dadi bace! Kana ka basu masauki me kyau naji kuma wani abu ya biyo baya kaga yadda asalin fusata take.

Fuuuuuuuu ya fice a parlon yabar kamal da hannu rike da fuska, sunkuyar da kanshi yayi domin hakan da baban mariya yayi na masa nuni da cewar tabbas beyi rashin mahaifi ba Wani irin girma da kuma darajar baban mariyane ya sake dabaibaye kamal. Domin a wannan zamani samun wanda zaiga kana aikata ba daidaiba ya tsawatar ma kanyi matukar wuya. Wani idan yaga kana aikata ba daidai memakon ya hana ka saima ya sake ingizaka da ingiza fushinka

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page 39&40

ROMANCE

BLACK MONEY

DEEP

Hope

courage

Survival

Humanity

Inspiration

□□□

_____

Suuuuuuu suuuuuuu suuuu haka Lafiyayyun baƙaƙe motocin ke sura uban speed saman shimfiɗeɗiyar kwaltar. Tun daga anguwar Victoria island har zuwa fitacciyar anguwar banan island duk inda suka gifta zakaga basu hanya ake, domin kuwa kallo ɗaya zaka ma motocin da irin uban speed ɗin da suke bayarwa ka gane bana lafiya bane.

Cikin dan kankanin loƙaci sai gasu a gaban wani haɗaɗɗen plat house ,sannan kai tsaye suka fada danna hancinan motocinsu gidan wanda uban security'n suka wangale musu ƙaton get ɗin. dukka motocin suka shige ciki suka kuma samu wajena gurbin da aka tanada don ajjiye motoci suka faka. Kafin mutanen dake ciki sanye da baqaqen suit suka firfito suna bada tsaro wa na cikin motar. dukansu sanye cikin baƙaƙen kaya gaba ɗayansu manyan bindigune a hannayensu.Cikin da zafin nama ɗaya daga cikin security'n ya isa ga motar dake tsaye dukka qofofinta a kulle yayi knocking baqin glass din motar tare da ma arms magana, yar ƙaramar magana sukayi kafin ya bar wajen.

sannan ya sake zagayawa right side na seat ɗin bayan motar ya buɗe qofar,yaja baya cikin girmamawa don bawa mamallakin motar fitowa.

Saida yaja wasu yan sakanni kafin kyawawan sawayensa su fara fitowa, sai daukar idanu suke saboda tsananin kyau da tsafta, Saida ya sake ɗaukar wasu sakannin kafin ya zuro dukka jikinsa zuwa waje. Zara zara yatsun hannunsa ya sanya yana qoqarin cire wayar dake maqale a kunnensa,kyakkyawar fuskarsa mai cike da wani irin kwarjini haiba da cikar zati a dinke tsaf babu alamun fara'a ko kadan tattare da ita.

Kyakkyawar soft fatar jikin san nan me murjajjen jiki da babu wani waje da yake a rame ko ya nuna alamun qashi,saima kakkarfan siffarsa da cikakken zatinsa daya nuna kansa da kansa ta jikin wasu haɗaɗɗun riga da wando na combat Reva net. Sai wani haɗaɗɗen luxury Rolex watch ɗin dake ɗaure a tsintsiyar hannunsa.

Lallausan sumar nan kuwa da tasha uban gyara daure a kasan ƙeyarsa ya kwanta yayi luf luf saboda wani irin gyara na musamman da akayi masa,

Baqar sumar da baƙaƙen kayan dake jikinsa suka haɗu suka sake haskaka farar fatarsa tarrrr tamkar fitowar rana a farkon wuni. Shade ɗin daya toshe idansa dashi shine ya sake saka kyawawan qwayar idanunsa dake da wani irin shape mai matuqar fusgar hankali,idanun dake cike da wani irin kwarjini mai tarin yawa kwarjinin da a kullum yake lullube da fushi da kuma fusata. Sai nose mark daya sanya wanda kai baka isa gane waye shi ba.

Wani irin daddaɗan ƙamshine ke tashi a jikinsa irin me ɗaukar hankalin nan. Ko yaya ka qara taqi kaɗan kusa dashi kana iya shaqar daddaɗan ƙamshin turarensa da ba lallai ka gane ainihin wanne irin turare bane,saidai yakan sanya nutsuwa ga duk wanda ya shaƙeshi ya kuma ƙara kwarjini ga ma'abocin ƙamshin.

Kyawawan fararen hannuwansa zube cikin aljihun tsadaddun riga da wandon dake sanye a jikinsa,Sake gyara zaman bindugunsu security'n sa suka sake yi a tsare cikin shirin kota kwanar karbar umarni daga gareshi. Wata zazzafar Iska ya ɗan furzar kafin ya taka zuwa gaba. Arms tare da wasu mutum biyu daga ciki sukayi gaba kamar masu masa jagora,sauran kuma suna biye dashi. Cikin takun cikakken gwarzon namiji yake takunsa har zuwa cikin ƙayataccen Royal parloun da yake ƙawace da wasu irin Italian Wikipedia chair. Daga nan duka bodygourd nashi suka tsaya a parloun shida arms ne kaɗai suka nufi entrance door ɗin da sai sadasu da duka sassan gidan.

A gaggauce suka wuce zuwa lipter da zai sadasu da dakin da zai sauka,cikin mintunan da ba zasu wuce 5 mint ba ya tsaya a parlou 3. Saida yayi scanning card a bakin qofar tayi qaramar qara alamun samun izinin shiga.

Palace tenpor room ɗin suka nufa kai tsaye Wanda ko ina na gidan Gellary odyssey ke walainiya tako ta ina.

Saida ya buɗe deep freeze ɗin dake makale da dab shiga asalin living room ɗin ya ɗauka kwallar wine ɗin sa. Nan ma Saida Gellary odyssey dpy ɗin yayi on locking up nashi kana ya suka shige Mahaukacin katon parloun da ma'adanar cctv footage ɗinsa yake. Wani irin matakan tsaron na'urori ne kawai ke magana a wurin.

Tanbuwal da tun da aka jeho hi aka garkamesa jiya be kuma sake jin motsi ba sai yanzu. Da wani irin sauri ya sanya hannunsa yana kare Mahaukacin hasken daya kusan ɗauke ganinsa, jikinsa rawa ya fara na tsabar azabar yunwar dake kwakular cikin sa.

Zaune yakai kan Chiar silinder caution ɗin dake facing da wannan mutumin. Ƙafarsa ya sanya tare da mirza ƙafar tanbuwal babu shiri ya saki wata ƙarar azaba cikin tsananin wahala ya furta.

"Pls kuɗin su waye ku? Me kuke nema daga gareni?, Kuɗi!?, Suna?, Mulki?, Ko kuwa ƙarfin Iko kuke da buƙata?"

Ya faɗa cikin muryan jigatuwa da wahala.

Shiru babu alamun amsa hakan ya sanya shi sake faɗin "please let me know waye kai?"

”Makwamishin guba! Mashekin rayuka matunzirin ruhi. Sannan kuma mai kare mabuƙata! Ni dabaibaiyi ne me harɗe duk kan wani azzalumi na kaishi har kasa ÆK”

Ya furta a fusace tare da kwance ɗaurin da akama tanbuwal ɗin. Wani irin mugun shock ne ya ziyarci ƙwaƙwalwar tanbuwal, AK AK AK haka sunan shi ya shiga masa amsa kuwa a tsakar kansa. Cikin Wata iriyar jarumtaka tanbuwal ya sheƙe da wata mahaukaciyar dariya kafin ya dakata. Cikin Wata irin dangerous voice ya furta.

"Ai baka cika cikakken NAMIJI ba tunda Saida ka hada hannu da mace kafin kawoni i zuwa gare ka,karkaga ina karkashin ikon ka ka zata zaka iya min wani abu.

duk da cewar zaki shine sarki a dokar daji amma karka manta damisa itace gwana wajen iya farauta"

Wani irin lalataccen kallo Æk ya wurgama tanbuwal tare da Crossing ƙafafunsa yana kora kwalbar wine ɗinsa. Cikin wani irin hosky voice ya ce.

"Ko wanne mafarauci garzone har sai sanda ya fuskanci ingarman zaki.

Wannan haushin ƙaramin kuykuyon kare kake! Ka sani haushin ɗan ƙaramin kuykuyon kare kuwa ba gurnanin damisa bace! Ammah Ka jira hasalin yadda gurnanin ta yake. Ka sani ABDOUL-MALEEK ba kamar sauran sharar daka saba takewa bane, wannan Asalin Cikakken fusataccen damisar daya fito domin farauta ne a gabanka"

Ya fadi tare da rotsa kwalbar wine ɗinsa kwalbar tai ratsatsa ta baje a wurin. Zuwa loƙacin babu komi a tare da Ak sai asalin fusatarsa kawai ake iya hangowa.

Armstrong dake tsaye ne ya tunkari inda tanbuwar ɗin yake tare da soka masa allura a gefen yuwansa Yana bin bayan Ak ɗin shima. Bai tarar dashi a main sequence parloun gidan ba, wayarsa ya fidda tare da tambayar su Boss ya fito ne?, Tabbacin be fito ba suka bashi hakan ya sanya shi sauke wayar tare da bin ko wanne entrance door da kallo.

Wani irin zafaffen numfashi ya fesar tare da tsananin tausayin uban gidan nasa. Kabar ƙasar ka kabar gidanku kabar danginka kazo ƙasar daba taka ba kana musu aiki da dukkanin zuciyarka da rai da ruhinka. Ko dan wannan abin ma bai ci ace gurɓatattun cikin ƙasar Nigeria'n sun sauya ba da kunya ma ace an rasa gwarzo zakwakurin da yake tsaye akan ƙasar sa. Kodan sun riga sun sanya tsoro ne a zukatan al'ummar OHO? Duk wani namijin da yake jin kansa da zafin kansa ta kawo akan ƙasar to kuwa Insha Allah sai an san yadda akayi aka kawar da wannan mutumin. Shin me masu kuɗin duniya da masu mulkarta suke son zama ne???. A kullum shine tambayar dake bisne cikin zuciyar Armstrong. Shi kikakken ɗan Nijeriya ne amma baya alfari da hakan saboda gurɓatattun cikin ta da ɓata garinta suka kewaye ko ina na cikin ta. Kasar data zamo koma baya ko lissafinta ba'ayi a cikin duniya.

A cikin gidanku ma babu adalci bare akai ga wani wuri me nisa, a gaban idonsa dangin mahaifinsa da suke yɗan uba suka sanya wuƙa suka yanke makogwaron mahaifinsa sa!, Akan dukiyar da guminsa ne shima ya bashi ba sata yayba ba kuma haram yabi wajen tara taba. To taya muke tunanin duniyar mu zata gyaru a cikin gidajenmu babu adalci? Sai tsananin azaba yakai tsanani mu dinga ƙiran Allah gyara. Tofa baya gyara ba dole muma sai mun gyaro ɓarnar dake cikin gidajenmu. Bawai Ƙasarce a ɓace ba mu al'ummar cikin ta mune a ɓacen mune ɓatattun dole kuma dama gyara ta cikin gidajenmu yake farawa. Idan muka gyara halayenmu sai Allah ya gyaramu Amma muma muna da kaso mafi girma akan tarin abubuwan dake faruwa da kasarmu uwarmu.....

Wani irin zafaffen numfashi ya furzar tuno yadda ƙanwarsa yɗar shekaru uku a loƙacin take kuka tana dukan ƙirjinsa tana ƙiran mommy na daddy na. Gaba ɗaya jininsu ya ɓata jikinta. Wasu hawaye Masu zafin gaske ne suka zuba masa a lokacin daya tuna sadda mahaifinsa ke faɗin.

"Ka gudu! Ka gudu kai da ƙanwarka ka tabbatar kun rayu ABDOUL-MAJEED, ka reni zuciyarta akan gaskiya da gaskiya ka tabbatar ka kulamin da RIYYERNERTOU, ka zama gatan ta,haskenta, ita kaɗai ce danginka yɗar uwa ɗan uwa ku tafi ka tafi wata duniyar kaje zaka rayu tare da tsarkakkiyar zuciyar da zata reni taku zuciyar da irin tashi zuciyar da ɗabi'arsa.kamin alƙawarin zaka zamo mutum na farko da ƙasar sa zatayi alfahari da shi...

Wadannan sune kalaina na karshe da suka tsaya masa cakkkk acikin tsakiyar ƙirjinsa. Mahaifiyarsu kuwa ta mutu ne ba tare data iya furta masa komi ba sai idonta dake kan Riyya. "Ka gudu karsu dawo su sameku domin a zatonsu kuna makaranta ne, yanzu haka sun tafi ne da niyar su dauko ku kuma su kashe ku. Wannan kuma shine babban zunubi mafi girma da zasu aikata idan har suka taɓa lafiyar koda ɗaya daga cikin kun!..... Be ƙarasa maganar da yake shirin faɗar ma rai yayi halinsa haka ya ɗauki RIYYERNERTOU akan shoulder nashi ya gudu da ita. Sun sha matuƙar walahar gaske har tsawon shekaru uku a lokacin yana shekara na goma sha biyar ita kuma riyya tana da shekaru bakwai. A haka wani baƙin dare ya riski rayuwarsu shida ƙanwarsa.

Daga nan babin sabuwar rayuwarsu ta fara shida ƙanwarsa ta hanyar keta mata mutuncinta ta hanyar mata fyaiɗe Anyi Raping ɗin.

Masu iya magana sunce ko wacce ƙaddara tana da nara madubin,sudai nasu madubin Ak ne domin a lokacin da yake tsaka me wuya cikin mugun yanayin makauniyar ƙaddarar data riski ƙanwarsa. A daidai lokacin Allah ya kawo masa Ak shine ya shige masa gaba akan komi! Shine yake amsa sunan UWA UBA a gare su shida ƙanwarsa har kwanan gobe da safe. Ya basu tarbiyya ya inganta rayuwar da tarin ilimin addini da na boko. Ya shige musu gaba wajen ganin sun zama wani abu A koda yaushe Har abada abadan abada ABDOUL-MALEEK KUWAIT shine kashin bayansu.

Hawayen tausayin gwagwarmayar rayuwarsu da suka fuskanta ya share ya nufi entrance door ɗin da yake da tabbacin anan Ak ɗin yake. Shima ɗaya daga cikin room din ya fada yana kokarin ganin ya kawar da tunanin dake kokarin zeroying maid nashi.

Duk kokarinsa nason ganin ya kawar da tunanin dake neman addabarsa abin yaci tura, kansa ya jingina da jikin kofar tare da lumshe Idonsa. Numfashi yake fitarwa Ahankali yayinda yake furta kalmar. " Innalillahi wa'inna ilair raji'un,² Ya hayyu ya qayyum" daga cikin zuciyarsa domin kuwa tsabbb komai din da yake gudun ya faru ya rigada ya farun. A take kwakwalwar kansa ta nemi juyewa amma ambaton sunan Allah da yake hakan ya sanya. Ahankali nutsuwa ke saukar masa acikin zuciyarsa yayinda yaji tarin damuwarsa na gushewa.sosea yaji sanyi da cikakkiyar nutsuwa da salama acikin zuciyarsa.

Gaban fridge bottle water ya nufa kai tsaye tare da ɗauko bottle water ya ɓalle murfin, ya kafa bakinsa Saida ya tabbatar ya shanye ruwan dake ciki tsabbb kana yayi wurgi da gorar. Wata iriyar ajiyar zuciya yake saukewa tare da sanya hannu ya ya dafe kansa. duk yanda zuciyarshi taso sanya shi dogon nazari yaki aminta da hakan haka kuma yaki bama brain nashi daman yin tunani kamar yanda ya saba a wasu lokutan.

Ya jima a tsayen da yake kafin ya nufi bathroom, ya sakarma kansa ruwa Ya ɗebi mintoci kafin ya fito jikinsa na faman ɗigar da ruwa, mini towel ɗin dake rike a dayan hannunsa na aikin tsanewa.

Wani farin trouser ya zira da t-shirt ita ma farar directly ƙroom din daya tabbatar da ak din na ciki ya nufa, tare da danna door belt din bedroom din yana jiran a bashi umarnin shiga.

★★ÆK★★

Yana shiga bedroom din kayan jikinsa kadai ya cire tare da daura fari tass din towel wanda ya ma wani irin lago lagon dauri kafun ya wuce bathroom. Kai tsaye cikin bathtube ya shige wanda ya hada ruwa me dumi da fresh out din wankan daya zuba. Aqalla sai da ya shafe mintuna masu dama kafin ya fito,tamkar wanda yake sauya fatar jikinsa. Fatar nan sai uban daukar ido da walainiya take ta kota Ina Ak namiji ne tsayayye da babu abinda yake masa shamaki da cikar zatinsa.

Lafiyayyar fatarsa dake daukan idonsa ya kalla ganin wato shi Hutu da jika cikin arziki da nutsuwa Wani abu ne na daban da idan Allah yayika cikinsu basa taba boyuwa ko yayana.

kauda idanunsa da suka dan canza launi sakamakon shigar ruwa cikinsu ya mayar ga madubi yana qoqarin tsane sumarsa data jiqe da ruwa,abu guda daya tak da zai

fara gaya maka AK din ba asalin bahaushe bane, kodan yadda farar fatar jikinsa take da kuma tulin gashin kansa da yake amsar kudade masu gwabi wajen gyaranta.

Tamkar babu wanda yake jiransa haka ya kammala shirinsa a nutse cikin wasu Ash din riga da wando Armless marasa kama jiki.wasu tausassan flip flops ya zura dogayen qafafunsa wadanda kamar basa taka qasa dan tsabar laushi da kuma taushinsu. kana ya kwashi wayoyinsa tare da daukar rimot ya danna kofar bedroom din ya bude. Waya ya fito yana yi cikin yanayin sakewa kadan.

Gaidasa Arms yayi tare da fada masa an shirya dining.

Bai ajiye wayar ba ya dan dago ya dan kalle shi kadan tare da amsa shi da kai, bai kuma janye wayan ba har zuwa lokacin.

Cikin ishashshen takunsa ya nufi dining din har kuma lokacin yana manne da woyarsa, Ba wasu abinci masu nauyi bane junk food ne kasancewar babu restuarent a kusa ga kuma a wannan gidan babu kuku's. Idan ka dauke sikuriti babu kowa dake rayuwa a gidan. Wannan kamar gidan horo yake.

A nutse ya jagali food din bame yawa ba yaci ya tashi har lokacin kuma woyarsa yake hankalinsa kwance. Kai tsaye coumpaund na gidan ya nufa da jikin railer ya jingina yayi crossing kafafunsa. Rigar nan da bata kama shima iska sai dade kwantar da ita a jikinsa take kan babu yar gadon fcarp.

★★★ ★★★

A dab plat din me napep ya sauke ta kamar kullum yauma sanye take cikin dogon shijjab har kasa, yau ba nikap ta sanya ba nose mark kadai ta sanya sai idonta data rufe da bakin glass. Rolex din skmee 2/1 din dake daure a hannunta ta sake dubawa da kyau don tabbar da nan din ne inda na'urar biyayar ta kawo ta.

Tun daga kan uban tight security'n dake zagaye da get din ta tsorata. Amma kasancewarta mutum bame nuna sarewarta a fili bane ya sanya ta nufar katon get din. Cikin rashin tsoro ta tunkari get din baki daya kawunansu a sama yake hakan ya sanya ta yin sadab sadab taje a sukwane zata shige suka farga da ita. Ko kafin su dago kuwa wata farar kwalbar dake rike a hannunta ta musu fesar turare da ita ji kake "fesssss" yuf tayi ta fada gidan.

Sadalaf, satalaf haka ta shiga kutsa kanta cikin gidan dayafi kama dana barayine ma zatace kome, gadai yadda hantar cikinta take kadawa a zahiri amma kuma ta

danne tsoronta haka ma a yanayinta baka isa fuskantar a wanne yanayi take a ciki ba.

Kasancewar duhun magrib na dab da kawo karasowane ya sanya ta ringa bin jikin manyan flower's din coumpound na gidan. A haka har takai ga jikin katuwar railer din dake coumpound na wurin,Kamshin da bazata taba mancewa dashi bane taji sun kawoma kofofin hancinta ziyara. Kanta ta dago daga kokarin tafiyar da take shirin ci gaba dayi,Ido biyu sukai daidai Yana kammala wayar shi. Wani irin mugun tsoron kai tsayene yanzu kammm taji ya ziyarceta, Hannuwanta da suka shiga mazarine ya sanya ta dire Robar dake hannunta ahankali gudun kada ya subuce mata, wani shegen kallo ya jefeta dashi a kuma daidai ta sake dago kanta aikuwa yaja kyawawan fararen idonta masu kama dana mashaya a cikin nasa ta hanyar sarketa da nashi catizeen eyes dinsa.

Yau kam ta gama tabbatarma kanta tata kuma ta kare tunda ta kawo kanta da kanta gidan wannan me satar mutanen.

Muryarta na yankewan tsoro da mamakinsa cikin qaramin sautin ta furta "pah pa pls don Allah.....

Wani shegen kallon daya jefa mata ne ya sanyata kimtse bakinta tayi shiru. Gashi kuma daf da juna suke sosai Kai tsaye hancinta babu Abinda yake shakar mata bayan mayen kamshinsa.

Wani numfashi taja ahankali tareda dauke idanuwanta daga kallansa gabaki daya saboda tsoransa da taji yana nema Kamata.

Jikinta ne ya fara mazari na tsatsanin tsoronsa ganin yana sake matsota, ja baya ta shiga yana sake binta yana ci gaba da jefa mata wannan dan iskan kallon nasa.

Kankame jikinta tayi wuri guda tare da toshe kunnuwanta ta fasa wata uwar kururuwar data sanya duka mutanen dake cikin gidan yowa wurin a guje.

Wani irin fusgarta yayi a fusace yana yin wata boyayyar hanya da ita. A daidai lokacin kuma harsu arms dake cikin gida sun kawo wurin, wulgawarsa kawai suka kalla ba tare da sun lura da Meerah ba.

Suna kaiwa wani wuri ya danna wata na'ura me kamar botton kai tsaye sai gasu a cikin wani fitinannen hadadde tsararren cumputer room. Gaba daya shiga dakin na'ura ta dauki shelar shigowarsa dakin tare da ambatar cikakken sunan meerah kai tsaye. Hakan ne ya sanyata kwatar hannunta daga kyakykyawan rikon daya mata tana bude idonta da niyar mata masa wasu maganganu masu irin myankar zuciyar nan. Ai kuwa bata sauka idonta a ko ina ba sai kan grey 11/in/21 rose glasses out din da kai tsaye hoton mutum yake irin rarrabewa nan, idonta bai sauka akan ko ina ba saikan hotonta daya rarrabe kusa ashirin da wani abin. Sai nashi daya juya

baya iyaka lafiyayyar farar fatar jikinsa kawai take iya gani!, Ai bata san sanda ta tafi da wani irin mugun gudu ta fada jikinsa ba tare da kankamesa tana sakin wata gigitacciyar karar daya sanya baki daya nu'urorin dakin daukar karar itama. Wani irin kulle idanunsa yayi tare da sakar mata wata razananniyar tsawar da kai tsaye ya idasa tafiya da numfashinta, domin dama tana dab da somewar na a lokacinma numfashinta ma seezing yake sai tsawar ta idasa tafiya dashi kai tsaye.

"Ochhhhhh!"

Ya furta yana ma rasa yadda zaiyi da ita saiya saketa daga tsayen da yake, muguwar buguwan da kanta yayi ne ya sanya numfashinta dawowa. Ahankali ta shiga kokarin wara idanuwanta, Dashi dake zaune kan wata kafurar luzury caution ta sake bude idonta.

A take komau daya faru da ita yanzu ya sake dawo mata da rarrafe cikin muryan kuka ta isa gabansa. "Don Allah ka taimakeni! Na rantse batar hanya nayi ne Anne nace ta aikeni gidan gwaggonta"

"Really?"

Ya fada da alamar tambaya yana fiddo da wata yar karamar aba daga cikin aljihun dogon wandon dake jikinsa tare da fadin.

"Kodai kin biyo wannan abar ba ohhh"

Wani irin zaro idonta tayi tare da fara jijjaga kanta zara fara magana yayi saurin katseta cikin dakilalliyar muryan san nan na no nonsense ya furta.

"Shiiiiiiii"

Da alamar zeeping na bakinta sai kuma yace. "Ki sani gidan nan da kika samu damar shigowa duk a cikin target nawa ne, don hatta napep in da kika shigo duk cikin tarko nane domin ni kaina na'ura ne. Motocin na kaiwa inda nake na tabbatar da akwai wannan cctv footage nan"

Ya karasa da jefa mata abarta yana mikewa tare sai kuma yadan juyo kadan yana sake fadin "Ohhhh Ashe bayan arhar da kike da harda jarum ma kin iya na jinjina miki dama nasan ko waye me ita dole yazo weldone ashe ba silly girl ce"

Daga haka ya juya da nufin tafiya ta gudu ta biyo bayansa tana

"Niban fadama kowa ba don allah ka fitar dani na Kar hankalin Anne na ya tashii bata san na fito ba da mij.....

Wani wulakantaccen kallon daya watsa mata ne ya sanya ta shanye sauean maganarta. Cikin tafiyansa na kamar koda yaushe ya fice ai kuwa tayi wuff ra wawuri hannunsa ta kankame a kirji suka fito tare a dakin.

Da wani kyakykyawan lafiyayyan mari ya sauki kyakykyawar fuskanta me kama da atafa don tsananin laushi da haskenta.

Ba karamin gigitata marin yayi ba amma ta gwammaci ta juro ta shanye daya dai barta a wannan killed house ne ma ko die house zatace mane oho. Zuwa lokacin kuma har an fara shiga sallan magrib hannunsa ta samu ta yankama wani azabben cijon da saida ta fasa mar fatar hannu, amma kota kanta be biba saima wurin daya bari cikin sauri don masallacin da za'ashiga.

Ai kuwa kamar yadda ta shigo yanzun ma tanan tayi nasarar fita kasancewar duk security'n sun riga da sun wuce masjid ne, amma duk da wani gudun bala'i tabar gidan tana faman sauke ijiyar zuciya, Kai tsaye ta sami napep ta fada tare da fada masa sunan anguwar data nufa dab da zata shiga suka hada ido ya mata wannan shegiyar alamar tashi, baki ta murguda masa da yimay alamar yanka wuya tana cewa me napeo din suje.....

A lokacin da suka kawo anguwarsu har ana dab da fitowa a masallacin baffanta, da gudu ta fada zauren gidan saida da tsaya ta daidaita numfashinta kana ta shige cikin gidan. Sa'arta daya babu kowa domin duk rashin mutumcin mutan gidan basu wasa da sallarsu, da sauri sauri tayi alwular itama tana fadawa dakinsu a sukwane.....

By Ammey laylerh

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

⭐ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page 41&42

ROMANCE

BLACK MONEY

DEEP

Hope

courage

Survival

Humanity

Inspiration

□□□

_____

Koda Anne ta idar da sallah tambaya daya ta mata shine "daga ina kike? Sai after magrib kike dawo bayan kuma tun sanyin la'asari kika fita?"

Dake ita sammm bata iya karya ba inma tayi karyar nan take ake gane tane ya sanya soma inda indar fadar inda taje din.

Uban tsawar da Anne ta daka mata ne ya sanya ta fadin. "Gi gidan su su di sha naje Anne"

Ta fadi mafanar a rarrabe ga rawan da muryanta yake. Wani irin kallon baki da hankali annen ta cilla mata tare da fadin. "Saidai kuma kinyi kuskure domin dishan tazo nemanki itama tama jima anan din, don haka ina kikaje DIDI!?"

Anne ta sake jeho mata wata tambayar. "Zamu fita wani aiki ne dama shine da bata zo na tafi"

"Kuma ita karyar ta miye da kai tsaye kika gaza fadamin?"

Wasu hawaye ta share amma kuma sake zubowa suke yadda annen ta tsareta da ido ma shi kadai firgitata yake. Haka dama anne take zakayi wasa da ita amma kuma bata karbar no nonsense,sai kuma annen ta sake dubanta a nutse cikin tsantsar kulawa domin ba ta lura ba iyaka tsoron tuhamar da tay mata take gani dangane da Didinta ba.

"Ki dauke tamkar babbar aminiyarki, yayarki kan uwarki kana ki dube ni a matsayin mahaifiyar da baki da kamarta, ki fadamin meke damunki?, domin na lura tunda wancan abun ya faru mood naki ya sanja sosae. Idan har bakiji tausayina a matsayina na mahaifiyarki kin fada min damuwarki ba wanne hali kike tunanin nizan shiga? Karkiji tsoron komai ki fadamin komai din da yake faruwa da rayuwarki MARYAMA"

Kife kanta tayi akan kafafun annen domin ta yarda kafff duniya bata da ya mahaifiyarta. Komai na labarinta da Ak bata boye mata har dauketan da yayi da irin yadda take ganinsa ya kwamushe mutane. Har zuwa yau data sake cin karo dashi wanda ita ko a ranta bata taba kawoma ranta cewar shi ne ba....

Kuri Anne tayi da ido tana kallon didin nata kawai tama rasa ta yadda ya kamata ta fara, cannn taja wani numfashi kadan tare da duban meerah din ta fara jeho mata tambayoyi tana bata amsa ita kuma.

Haka harta ta bata shawarwarin dasuka kamata duk da ma ita nata ya kusan xuwa karshe domin suna cikin satin biki ne tsulum tsulum. Dama kuma daga yau din Anne'n tayi niyar hana abarta fita domin killace ta bata gatan da ake bama ko wacce ya idan za'ai aurenta. Duk wasu hidinduminta suna a gidan hajiya ummah na a gidan kuwa yadda Kasan ba biki za'aiba haka gidan yake domin ko tada zancen ba'ayi. Ba danma wannan rikitacciyar tsohuwar kakar tasu tazo ba da itama kanta har mantawa take da wani zancen aurernta.

Amma itama da biyu tazo yau kwanaki uku kenan domin bata kaunar Annenta sammmm acikin duka matan baffanta ita kadai tafi takura mata sa'ar annen ma daya da take da tsare gida bata daukar wargi ko wanne iri ne kuwa daga wurin ko wanne mutum. Shi yasa sau da yawa matan gidan ke shakkarta yadda kasan irin jinjn saurartar nanne ke yawo a jikinta haka take. Ita kanta meerah din wani sa'in kawai kallon annen nata take. Nan anne ta bata shawarwari sosea kuma taji dadinsu tare dajin nutsuwa ta musamman. Don duk wannan tsoron saita nemasa ta rasa Lallai sai yanzu ta yarda da wannan karin maganar ta bature Na *_A problem shared is a problem solved*_ Sai gashi tun ba'aje ko inaba komi yazo mata da sauki.

"ALHAMDULILLAH!"

Meerah ta fadi incheerfully.

★★KANO★★

Yau kwanakin su baffafofin kamal hudu a kuma yaune suke shirin komawa. Amma sai baban mariya yazo da batun kawai su tsaya a daura Auren dansu a gabansu, da sunso kin tsayawar saida kamal din yayi magana kana suka yarda zasu tsaya a daura auren.

Bayan sun sake kiran dangi sun sanar musu wohoho zokaga yadda ake bidiri a dangi nan fa mata da maza suka ringa yowa tururuwa suna dannowa kano gidan kamal. Sunce shima sai sunyi may auren gata irin na ko wanne da, Wasu a gidan kamal din suke wasu kuma a gidan baban mariya aka sauke su. Da yamma kamar yadda baban mariya ya bukata aka daura auren KAMAAL SURAJ RANO da amaryarsa MARIYA USMAN SHEKA akan sadaki dubu dari da hamsin. Akwatuna kuma daga baya zaiyi kwasam saiga abinda ya kusan gigita duniyar kamal domin ga sanarma Ak a kurarren lokacine don besha ma zaiga sakon shiba. Amma sai gashi ya niko gari tun daga lagos zuwa kano dake dama ya taba zuwa sau daya bayan Shi kamal din ak din ya kirashi abujan nan da yaje.. Shi da kansa ya amsawa kamal auren mariyan ya kuma hada musu party dinner a wani katon holll. Ya kuma turama kamal din zunzurutun kudi har million biyu.

A daren yabi girjin dare ya koma wajen sha daya da wani abu yabar kano shida arms, Washe gari aka sake sabon biki kana mazan suka tafi sauran maran kuma sai an gama shagulgulan bikim kafin su tafi. A wata sabuwar anguwa kamal yasai gida yabar wannan baban mariya ya aika a gano gidan don su gane girman gidan saidai abin mamaki kamal ya zuba komai babu abinda bai zuba musu ba. Dade da kayan kitchen ya zuba musu wasu sai yan tsitstsinen da ba'a rasa ba.

Umayma harda kukan ta a lokacin da danjinta dana malam ke sanar dasu abinda kamal din ya musu. Dama yar gudun mawar da yan uwa da aboka nan arziki suka hada musu zasuje su mata kayan dakin, kayan kitchen kuwa dama basa lissafi dashj lallali kamal ya zo busu da wani babban al'amarin da bazasu taba mantawa dashi ba, zuwa yamma aka shiga jibje musu wasu shegun akwatuna masu shegen kyau da tsada. Wannan aikin nabban abokinsa ne ZAYD suraj. Wanda wani aikine ya taba hadasu a wata cout akan shariyar wata yarinya da akayi raping nata kuma kamal ne dan sandan daya jagoranci case din har zuwa sanda yayj winning ta hanyar mikasu ga cout din da anan ne suka hadu da Zayd din wanna shine wanda ga karasa aikin ta hanyar jajircewarsa harka aka yaron senetor na garin kano a prison. Kunsan magana ake ta sarauta a wurin.

Akwatuna saida aka sauke musu set uku ko wacce da kolonta. Yaufa ake yinta dan fulani yaje asibiti dubiya an bashi lemo da kaji akace kado fito yace ahhhhhhh ai nikam naga makwanci. To hakace ta kasance da iyayen mariya Hakika duk wanda yayi hakurin dafa dutsi to asannu zaisha romansa. Sunci wuyar sun shanye dakan da dukan sai gashi sama taka allah ya basu dami a kala.

Duk wasu abubuwan al'ada suma saida sukama kamal suka mika a hannun danginsa. Dare nayi aka mika amarya mariya wa gidan mijinta a yanzu kamaal suraj rano.

Sosae tasha amarya mariya tasha kukanta kasancewarta mutum bame hayaniya bane ya sanya sammm babu wani batun tada hankali akan maganar auren.

Haka dai al'amura ke wakana cikin kwanciyar hankali komai yaci gana da tafiya.

★★Lagos★★

Gidansu salman kuwa mahaifiyarsa da yayar mahaifiyarsa ganin dai tabbas auren na shirin tabbata ya sanya hankalinsh tashi matuka, yanzuma zaune suke itada yayarta me suna Aunty mariya sai kuma yarta sury idon nan yay hulu hulu dashi nashan kuka. Ran kowa a wurin a bace yake, cikin kuka sury ta rarrafa gaban mom salman ta kama kafafunta fadi take.

"Mom don allah ki taimaki rayuwana wllh ni salman nake so shi kadai nake kauna a matsayin abokin rayuwata! Mom taya kuka min haka bayan kunsan cewar ni shi kadai nake so"

Ta fadi tana sake rushewa da wani kukan Salman da shigowarsa kenan yaja tsaki "Mtsss ni kuma uban wa yace miki zanso mace kamarki babu baya babu gaba, ki sani rayuwar ma da kikai dani costa risca ba ason raina bane. Don dai kawai muna gida daya ne kuma babu wata beb din a kusa shi yasa ma har na nemaki nayi maleg dake".

Yana fadin hakan yay haurawansa upstsaid nashi.da wani mugun kallo umma mariya ta bishi kafin da dubi mam ta mike a fusace tace aidai kina jin abinda wannan watsatstsan yaron naki yake fadi a gabana, amma kikai shiru to wllh idan har ina numfashj a duniya babu wanj shegen daya isa daura wannan auren alkawarinane wannnan kuuma kinfi kowa sanin daukan alkawarina daidai yake da bi takan kowanne shege ne, koda kuwa za'a zan bada da kisa ne to kuwa saina cika wannan alkawarin.....

Fuuuuuuhhh taja hannun yarta suna fucewa a gidan Zeey dake kitchen a lafe ta share wasu hawaye tana jizar labbanta. Tare da fadin "ai wallh inda numfashina na gangar jikina ahalin wannan gida kuda kwanciyar hankali kuma kunyi sallama". Tana fadan maganar tabar kitchen din tare da laluben wata number a wayar da kawai wata jar alama ta mata babu suna.

Woyar na shiga ta zube akan gwawowinta tare dayin sujjada daga inda take.ta furta "Ran uwar gijiyata ya dade". Daga cikin woyar kuw wata kakkarfar tsohuwa ta wagaje wargajejen bakinta ta hakwaran sukayi tsatsa ta kwashe da wata dariya me kama da kukan jaki.

Kafin ta shiga fadin "An gaida kura me dauke da fatar akuya Birinya baki jelen banza kedin kamar hadari kike malafar duniya ba shirgi maganin bari ta wajena, meke tafe da wushuwatu na?"

"Alfarmar kamar ba alfarma bace a badini da za'a juwa gabansu zuwa bayansu bayansu ya koma gabansu nake ga hakan kawai zaifi, domin naga kamar ba masu ganewa da fahimtar bane"

"Hhhhhhhhhhhh

Hhhhhhhhhhhhhh

Hhhhhhhhhhhhhhhh

Rainon shegu karki damu dumuwasi na tare dake yar shegiya uwar tsinannun, jaraba a cikin jarababbu makata a cikin makatattu annoba a cikin al'umma hinge kike babu me iyawa dake wushuwatu, dan daukar fansa aka yiki"

Wata iriyar dariga zeey data koma wushuwatu ta barke dashi tana saisaita yanayinta ya koma normal daga na mummunar halittar data koma zuwa zeey din asalin da muka sani..

Shi kuwa salman saman lafiyayyan gadonsa ya fada tare da fiddo wayarsa kai tsaye data ya kunna tare da kiran dolly video call. Fitowarta daga wanka kenan tana daure da wani guntun towel ga wani bature kwance akan lafiyayyen gadon hotel din, ya tukun kune jikinsa da tattausan farin duvet daga shi sai wani transpared pyjamas. Woyanta da dama alread datanta yake a bude ta dauka, ganin me kiran saida ya sanya tadan bata fuska kana ta dauki woyar zama tayi akan stool na mirror'n. Kallonshi tayi yana kwance daga shi sai longsleev pant sleek wani irin numfashi ta sauke cikin muryan yar shogwaba ta furta.

"Ohhhh my babyna I miss you somuch mua" ta bashi wani kyakykyawan kisses ta cikin woyar. "I miss you so much dee" ya fada yana gyara kwanciyarsa yana dan lumshe ido domin tunda ya baro poland bai sake mu'amulantar wata mace ba,

domin shi ba da kowacce mace yaje iya mu'amularsa shi ne ma dalilin daya sanya ya ware dolly ita kadai dinta.

A hankali ya shiga bude idonsa sai ya hango wani kakkarfan bature yana nufo dolly'nshi, Wani irin shafarta baturen yayi wanda hakan ya zoma dolly a bazata domin ita har tama manta cewar tare take da wani.da karfin masifa ya rumtse idonsa yana jin jijiyoyin jikinsa na tashi na tsantsan bacin rai. Me kenan?Amananshi dolly taci kenan kome? Meye wannan yake yi a tare da bai karasa maganar zucin saba wannan baturen ya finciki mitsil towel din dake jikin dollyn tare da wani irin hugging nata.

Wata kara salman ya saki cikin tsawa ya mike tsaye a fusace tare da ambatar.

"Dolly!!!"

Wani irin mikewa tsaye dolly tayi babu wata² ta dauke fuskan baturen nan da mari cikin tsawa tace "I hate yhu Vham I hate that"

Salman kuwa tuni ya datse kiransa wani irin dafe kansa da hannuwansa yayi kansa na wani irin sara masa lokaci guda, bathroom ya fada ya sakarma kansa ruwa kozaiji dan sausauci jin zuciyarsa yake tamkar yankar naman kirjinsa take tana zazzabowa kasa.

Da bathrobe ya fito sanye a jikinsa sai kamshin shower gel yake da sauri sauri ya shirya ya fito da nufin xuwa club haka ko park,don ragema kansa takaicin dolly.....

Mom nashi ce zaune a parlon har lokacin laptop ne a gabanta dana famar sarrata cikin kwarewa, sai zeey dake dan matsa mata kafafunta sama sama. Har yakai gab bakin kofa mom bashi ta tsayar dashi ta hanyar ambatar sunan shi.

Cakk kuwa ya tsaya tare da juyowa yana kallonta "Dawo inason magana dakai ne" ta fada cikin rashin wargi.

Dan yamutsa fuskarsa yayi yana fadin ta jira yanzu zai dawo cikin muryan no nonsense ta furta "Dawo nace"

Dan dole ya dawo yana zama tare da tankwashe kafafunsa a gabanta yana fuskantar cikin yanayin jin haushi.

Kallan shi mom nashi tayi tana ajje laptop din dake kan cinyart zuciyarta na quna tace.

"Se yaushe ne zaka daina kuntamin da rashin daukan maganar mahaifinka fiye da nawa, sai yaushe zaka me amfanin dazanyi alfahari dakai amatsayin dana Salman?

Kullum mahaifinka shine a samana akan dukkan wasu lamuranka!. Menene yake faruwa acikin kanka ne da kwata kwata babu ranan da zakasa nayi alfari dakai a matsayin dana? Ban isa dakai ba ban isa sakaka abu ka yimin shi ba cikin dadin rai....

Hannuwanta ya kama yana hadewa cikin nasa tafin sai kuma yadan rausayar da kansa yana sakar mata murmushi. " Mommah me yasa kullum kike ganin tamkar baki isa sani abu nayi ba? Kullum maganar kenan sabanin ra'ayine kawai muke samu dake. Shi kuma daddy so tari ra'ayinmu kanzo daidai dashi so shiyasa zakina ganin kamar bana bin umarnin, pls my mommanah kimin afwa Ina matukar son Meerah ne har zuciyata wllh"

Wani irin rumtse idonta tayi tare da zare hannunta dake cikin nashi zuciyarta na mata daci kalamansa na kona zuciyarta. Ya zama dole tayi wani abu akan wannan auren da har cikin zuciyarta taji bata kaunarsa kwata². Tashi tayi tana barin parlon da kallo ya bita domin tsaff ya gama sanin so take taga ta dakatar da auren nan kota halin kaka, ficewarsa shima yayi a parking space ya dauke daya daga cikin manyan motocin dake shake da wurin ya cilla saman kwalta tare da daukar hanyar hotel din Asas rayallerh.

★★KUWAIT★★

Duk inda ka wulga bayine da kuyangi bila adadin akowace kusurwa ta cikin babbar masarautar. kowanne da aikin daya duqufa yanayi wasunsu kuma a kakkame suna gadin hanyoyin wucewa da kowace qofa ta cikin masarautar. Musamman entrance din da sashin me martaba sarki HASSAN AL-HASSAN EMAAR KUWAIT yake, Wasu mahaukatan Samudawane kewaye da sashen baki daya.

Kallo daya zakama dukkaninsu ka gane ko wannensu yana cikin yanayi na tashin hankali ne.

Wani irin shiru ne ya ziyarci wurin tamkar wanda mutuwa ta gimla ta wajen.Kowa a take ya shiga nutsuwarsa Wanda suke a daidai hanyarta suna rabewa gefe tareda sunkuyarda kai kasa don bata hanya saboda takun tahowar gimbiya ADEENERH.

Wanda sautin anklets din zinarin dake kafarta shine yake ankarar ma duk wani hadimi isowarta ko tahowartar tundaga nesa.

Wannan sautin sarkar shine ke sanarda tahowartatahowarta tun daga yarinta harzuwa yanxu data manyanta saboda mulki a jinin jikinta yake. Macece me takukar izza dajin kai kagata yar zafin kaice ba komi ake mata ya burgeta.

Tana da wani irin boyayyen hali na tsananin jin dausayi, idan akace kowa ya tsani abu to ita kuma zai kasance tana yi ma wannan abun ko maye wala mutum wala sabanin hakan. Idan kuma aka daukaki abu to kuwa zaka tarar ne sammm wannan abun beyi mata ba koda kuwa kyansa ace yakai zinare kyaune.

Tana karasowa hanyar dazata shigarda ita bangaren mai martaba sarki ta tsaya cak batare da tace kala ba saima juyowa da tayi ahankali tadan kalli gefenta.

jakadiyar dake gefen tace tayi saurin matsowa tareda juyawa takalli kuyangin dake take musu baya kusan su shida, kallo daya tayi musu suka ja baya ahankali suna tsaya tareda sunkuyarda kai domin sun san ma'anar hakan...

BY AMMEY LAYLERH

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page 43&44

ROMANCE

BLACK MONEY

DEEP

Hope

courage

Survival

Humanity

Inspiration

✔✳✳❇

Boyayyar ijiyar zuciya tasauke ahankali saida nu'ura ta tantanceta kana ta sanya kanta zuwa kayataccen parlon.

jakadiyart na mara mata baya Parlour ne mai wani irin girma da tsari dayaji adon royal chairs gold and golden kamar zinari sai kyalli da daukar ido suke. sai komai daya kawata parlourn yazamto shima gold and golden colour dinne splits aircon kusan guda biyar sai aiki suke sanyi yakama parlourn tako ina sabida wata irin dukiyace ta musamman aka narkar a parlourn. Wanda tsabar haduwa da girman parlourn yasan ya sammm alkalamina yayi kankanta daya rubuta muku irin kayatuwar parlour kuyi emaging kawai aranku yadda parlourn zai kasance.

Babu kowa parlourn kasancewarsa parlourn farkone dazai sadaka da palon sarauta harzuwa turakar sarki. Saima wani irin shiru da parlourn ya dauke.

Sake tsayawa cak tayi tareda sake sakin wata nannauyar ijiyar zuciya akaro na uku zuciyarta na harbawa batareda tajuyo bangaren da jakadiyar ke binta ta mata alama data dakata.

Ajiyar zuciya ta sauke a karo na ba adadi kwawan idonta sun rikide sun koma jajaye. Hakan na sake bata tabbacin jikin Mahaifin nata ya matsa kenan da gasken?.

Adeenerh ta fada acen kasan makoshinta kafin ta tattaro duka jarumta da karfin gwiwanta.

Ratsa dogon palon tayi kai tsaye kofar da zata kaita ainihin parlourn mahaifin nata ta tunkara zuciyarta na neman karyewa. Saida ta runtse jajayen idonta kana tayi kundunbalar tura kofar bedroom din.

Wani bedroom ne na alfarma babu kowa sai qarar ac dake tashi ahankali.

Zaune yake cikin shiga ta alfarma saidai Kallo daya zaka masa kasan bama ya a hayyacin sane, jin motsin shigowane ya sanya Zaid dago da kansa kallo daya yayi mata da idanuwansa masu tsananin kwarjini da firgitarwa ya dauke kansa.

Duk da taso rudewa tayi saurin daidaita kanta ta tattaro nutsuwa da karfin halinta baki daya. Duk da kasancewar Zaid kani yake gareta amma ba karamin kwarjini yake mata, kasancewar kwarjin mahaifinsa ne ya dauka reality shida Biyuninsa Maleek.

Karasowa tayi cikin sanyin jiki da fargaba ta kallesa ta rufe idanuwanta dasuka fara canxawa tana durkushewa gaban zaid din. murya na rawa tace "Me martaba! Paapana zaid Ya abana"

Idanuwan daya sake watso matane yasan ya jikinta sake daukan mazari ga shirun daya mata shi kansa babban tashin hankali da azabtarwane wa zuciyarta.

Sake dukar da kanta tayi saboda gudun ganin yanayinsa. ko dagajin yanda ya dauke wuta yaki ya magantu ya sanyata rushewa da kuka wai ko zai magantun, domin ita wllh tsoro take! Tsoron dunkarar dakin sirrin me martaba take gudun abinda ka iya zuwa yaje. Gudun kar tayi gamo da abinda zai sanya zuciyarta bugawar lokaci guda.

A kalla sai da dauki tsawan wani lokaci tana rairai kukanta nan ma shiru yaki kulata.

Kamar daga sama taji dakakkiyar muryarsa cikin ikon mulki yace.

"Me martaba me mutuwa paah yana nan da ransa, domin mikiyansa ba zasu taba iya kaishi kasa ba. Kimin shiru anan domin wannan kukan naki sake fusata zuciyana yake, ki sani Sarki HASSAN AL-HASSAN EMAAR dashen Allah ne hadari ne shi malafar duniya duk wanda yace zaiyi dashi yaja da ikon Allah ki shiga idonki ya kalla miki shi. Dole wannan karon dan zaki ya bayyana akan mikiyansa. Lokacin dawowarsa yayi Masu gudu su gudu domin kowa yasan karon ba dadi!!!"

Ya karasa fadar maganan nashi a fusace.

Dagowa tayi takallesa idanuwanta na canxawa zuwa kalar tausayin dan uwan nata. Tare da zubo da wasu kwallar zafin da zuciyarta ke mata, tana jin tsananin kaunar yan uwanta a ranta duk da kasancewar ba uwa dayace ta haifesu ba. Adeenerh itace babbar yar me martaba mahaifiyarta ta rasune a lokacin tana yar shekaru shida xuwa bakwai. Ba tare data sake kallon inda zaid din yake ba ta mike tana nufar daking room din data tabbar anan me martaba yake. Tamkar yadda ya bata umarni haka ta ratsa ta shige cikin parlourn.

Duka wadanda suka dace ne a cike tare da dakin kowa rannan bace babu me alamar sassauci. Kowa ta shiha bi da ido anan ta itama nata idon suka kallar mata

Mutanen dake ma paah dinta kallon ka mutu kawai muhuta din nan.

Zaune takai ta bangaren da Oummey ke zaune, shiru ne yaci gaba da wakana a dakin zamanta da kamar mintuna biyar MOH JIDDOH ta dubi Oummey tare da furta.

"Wannan karon saiki kira lalataccen dayan dan naki, dan wannnan jinyar tasha banban da sauran, mebi ta ajalinsa ne tazo kuma ta gaskiya da gaskiyar kenan.

Wani irin mikewa tsaye Adeenerh tayi cikin furyar fusatar zuciya da dacin murya ta furta.

"Wannan kalmar marar kan gado fa JIDDOH! Ki sani gudun hatsaniya ne ya sanya mutanen da suka kasance mugwaye a cikin zuriyarki ya sanya mutumin daya kasance shiru shiru ya fusata!. Inason ki sanarma azzaluman cikinku cewar idan har akaci gaba da fusata shi to ki sani tarwatsa masarautar zaiyi kinsan da hakan?. Uwa uba kuma Zakin da kika dade kina ikirarin ya dawo to ki sani yau sai adda'arki ta karbu dole ya dawoooo.....

Kowa da yake daking room din babu wanda jinsa da ganinsa basu tafi hutun wucin gadi ba. Kai tsaye Adeenarh ta zari wayar Oummey directly numbern da tayi lakabi da *Willion gargalion* ta dokama kira tare da manna woyar da kunnen oummeyn "kima danki magana a gaban kowa ki sanar dashi ya isa haka paah dinsa da kasar shi na bukatarsa suma, har wadan da ba'a gayyata bama na muradi da dawowarsa mahaifarsa EMAAR's kai tsaye ABDOUL-MALEEK HASSAN AL-HASSAN EMAAR's take da bukata!”

Tana fadar hakan ta juya a fusace tabar dakin.

★★NIGERIAN/ LAGOS★★

Fitowarsa kenan wayarsa ta fara ringing ransa adagule yacirota da nufin kashewa gaba daya. Domin tunda yayi waya da zaid komai ya gama kwance masa. Saiya sami kansa da tsurama woyan nashi ido ganin sunan dake yawo akan screen na

woyan *_Sweet Oummey_* wani iri rintse idanunsa yayi ransa nakuma dakulewa. Saida woyar ya katse kana ya sake calling nata againt.

"*GARGALION*"

Kai tsaye sunan ya tafi ya ratsa har cikin tsakiyar zuciyarsa.

"Paah! Dinka EMAAR's na bukatar Tsayayyen matashin zaki majinginarsu. Ka sani shi marar jin magana sai ammasa hukuncin jaki yake ganewa. domin kawo gyara acikin al'umma kuwa dole sai wasu sunsha duka dole wasu sai sunsha jijjiga, maza ka dawo GARGA!!! Kai kadai ne mafaraucin da zaiyi wannan farautar”

Wani irin fesar zazzafan numfashi yayi tabbas duk Wanda yake da hannu a poisoning na paah dinsa sai yayi dana sanin saninsa arayuwa. Babu ruwansa da wani yar uwa, dan uwa, dangi domin babu tsoro ba fifitawa ba kara ba alfarma ,zai hukunta duk wanda yake da hannu akan paisoning na paah dinsa. cikin suyar zuciya data ruhi ya Wani irin kaima glass di car din da yake shirin shiga naushi. nan take glass ya tarwatse. bai damu da ciwon dayajiba.

Cikin dakakken sautinsa ya furta, “tabbas kafin suga bayan paah ni zanga nasu bayan oummu!!! rayuwar mahaifina bazata salwanta abanzaba! Saina wulakanta dukkan masu hannu aciki kosu waye su wlhy oummey numfashina fansa ne akan mahaifina!!”.

Dole saida oum tacire wayar daga kunnenta saboda yanda Ak ke magana cikin matsananciyar tsawa.

Buga wayar yayi da kasa batareda ya katse kiranba. Nan take ta tarwatse wata uwar tsawa ya dakama security'n akan suje.

Gaba dayansu cikin rawar jiki suka nufi motocin da ke fake a wajen, ko jira abude masa baiyi ba yabude yashiga.

Hankalinsu a tashe yake daganin yanayin boss in nasu, sunsan ba karami abune kesa ran boss ya baci haka ba.

Saida suka fita daga gidan suka hau kwalta kana suke tambayar ina suka nufa?.

Tamkar bazai tankaba sai kuma furta "airport" dake arms yana cikin dayar motarne ya sanya baima san abinda ake ba. Sai dayaga sun dauka hanyar airport din ne ya gane tafiyan nasu ashe na yanzu ne. Domin dama tunda yayi waya da zaid ya shirya tafiya amma sai washe gari.

Cike airpot din yake da tarin security na tashin hankali tamkar irin wanda suke gadin gidan mutuwar nan. Sanya yake cikin normal cashmere me tsananin taushi

da laushi wanda tsadarsa yake a baiyane, kafafunsa sanye cikin wasu tsadaddun shoe cambot bleim.

Kasancewar yau babu komi a face nashi hakan ya bayyana hasalin kyakykywar fuskansa ga jama'a kai tsaye. Nan securityn suka shiga bashi wani irin tsaro na musamman.

★★★★

A hankali Maleek ya ɗago manyan idanunsa tare da kallon taswirar kasar sa da suka iso tsakiyarta.

Haka nan yake jin wani irin abu a cikin jinin jikinsa. Ji yake tamkar ya tafi yabar wani abu mai muhimmanci nashi ne a kasar ta 9j. Numfashin mai sanyi ya fesar tare da ƙkara ware manyan idanunsa yana jin yadda zuciyarsa ke hautsinawa bugunta na sake bugu.

Misalin karfe sha biyun dare Jirginsu yayi saukar angulu a cikin babban Airport din kasar kuwait. Din na Hammad international airport.

Da sauri arms ya kalleshi sai kuma yayi sauri ya mayar kallonshi gefen damanshi ganin har an buɗe ƙkofar jirgin.

A hankali ya fesar da sassayan numfashi dai-dai lokacin daya fara taka step na forko wanda ya fito da kanshi sararin garin kuwait yana shakar yancin iskar kasarsa.

“Yah Salam”

Ya furta Sabida wani irin ni'imtaccen iskar kasar sa mai dadi mai cike da salama da ke ratsashi yana shiga duk ta inda hudar gashin jikinsa yake.

Wani rin amintaccen numfashin mai cike da yanayin sauke ajiyar zuciya ya shaka like irin Wanda baya tare da natshwar nan yau kuma ya samj cikakkiyar nutsuwar.

A hankali yaci gaba da taka steps din yana sakkowa kasa.

Wani saurin runtse idanunsa yayi lokacin da ya dire tafin ƙkafarsa akan kasarsa. A take yaji naman jikinsa na wani irin tsuma tun daga can cikin jikinsa da zuciyarsa yakejiyo wani irin abu na kokarin fusgar numfashinsa. "Subhanallah!"

Ya furta a saman lips inshi yana karasawa ware eyes nashi sosae akan kasar sa. Bawai baya zuwa bane yana yawan zuwa kasar saidai zuwan yana kasancewa na sirru ne. Dan baya cikakken 5Months bai leko kuwait din ba.

Wasu shegun hadaddun dunkulallun luzury car's ne suka kutso kansu cikin airprt din. Wanda ko wacce bayan mota me makaon lamba dauke suke da sunan *GARGALION*. Ba'a taba ganin mitocin idan harba mamallakansu ne yaso a gane hakan ba. Duk wata shekarar da zata shude tana shudewane da duk samfurin sabuwar motar data fito na GARGALION din.

Wanda kai tsaye kowa yasan mamallakin sunan. Zaid ne da kansa yazo daukar biyuninsa airport din ba tare da sanin kowa ba a cikin masarautar.

Da yar sassarfa zaid ya karaso tare da hugging dan uwansa hana sumbatar shi a goshi. Tare da fadin

"Ur well come 2 u in my country twin"

Dan bubbugawa bayansa Ak yayi tare da furta "Well come back againt daya na"

Sake hugging nashi zaid yayi kana ya isa ga arms daya kasance amini a gareshi shima yayi hugging nashi.

Sake hugging Ak yayi kafin su nufi wurin dunkulallun motocin dake jiransum

Da sauri daya daga cikin tight security's din wanda ke gefen damar motar ya kai hannu jikin handle din ƙkofar ya bude Ak.

A nutse ya fada cikin motar kana sauran suka shishshiga, saida fadawan suka tabbatar da cewar ya rigada ya shiga kafin su shiga wani irin busa sarewar dake ma duk wani mahaluki cewar GAGALION ne a wurin. Domin busar da ake may ta daban ne irin me sanyin nance dake ratsa zuciya ya tsuma namomin jikin dan adam.

Wani irin lumshe ido yayi tare da budesu a firgice wata sabuwar izza da kasaita na zuwar masa.nan fa hankalin duk wani dake cikin airpot din yayo kansu duk da kasancewar tsakar dare na, amma sukam babu ruwansu wasun suma su yanzun shine rana a garesu.

Mandood dake daya daga cikin jama'ar airpot dim shima hankalinsa ba karamin tashi yayi ba. Su kuwa jama'ar sauran airpot din kowa kokarin gani yakai wurin tarin car's din, saidai security's sun hana hakan ta hanyar bashi garkuwa.

Mirza kan lafiyayyun motocin suka yi kyakykywan kwaltan airport din har zuwa EMAAR's MENTION.

Cikin tafiyar da bai wuce 50 minutes ba suka iso gaban katon get din masarautar, katon screen welpaper odysss na mention din na welcome nashi. Dauke da full

name nashi shudaye da jajayen da blue din abubuwan ke zana sunan ak din. A get na farko, nu'urar dake tantance mutane ce ta tantance motar kana suka danna get na gana duk inda suka gilma sai kaga kowa a yanayi na kamewa da zuke numfashinsu na dan wani lokaci. Da wannan kaifaffan eyes din nashi yake bin ilahirin masarautar din da kallo.

Haka suka dunga shige get get ko wanne da kalan nashi tarban da sukema Ak din. Shi kuwa yana hakimce cikin tsumammiyar lafiyayyar kujerar motar ya nutse, sanyi da mayen kamshim sa na dada sanyi shi yin relax acikn kujerar mortar.

Gefe guda kuma daddadar kira'ar Afif muhd taj na tashi.

Nan din ma daya daga cikin bafadawan ne ya fito yana bude mai motar tamkar mai gudun tashin yaro a barci.A kalla saida aka kwashe sama da awanni goma ciff be fito ba, kana aka sake dibar wata gomar kafin almurin bakin takalmin shoe combat dinsa mai adon golden ya sauka saman maroon carpet din da aka shimfede masa ahankali. Sai da aka sake jan wasu sakannin kamar uku kana dayar kafar ma ta sauka sky blue din wandon cashmere nashi ya bayyana. Sannu a hankali sauran gangar jikin ma ta fito. Kaf wajen ya dauki wani irin tsitttt na bayyanuyar AK din tsaye akan diga digansa.

Tsaye yake kam akan tsahonsa na tsayayyen namiji da babu ko rankwafawa. Lallausan cashmere din jikinsa da ba sai an zauna bata lokacin lissafin kudin da suka lashe ba. sun masifar zauna masa da tabbatar da Ak din a matsayin jaruminsa mai gwara kan naira ta yanda duk yaso bisa damar da Allah ya bashi. Kamilalliyar fuskar san nan ma'abociyar kamewa da tsare gida kamar kullum a tsuke,

Saidai yau din ma dai akwai ring diamont barima manne da kunensa, hakama zanen tattoo dinsa mai fuskar lion na nan zaune daram. gashin nan daure daga kasan keyarsa ya dauresa har yana dan sauka jikinsa. Kai tsaye saiya fiti a hasalin balarabensa. Babu mai ganin idanunsa kasancewar toshe yake da shade mai duhu sosai. Wanda hakan shine ya sake bayyanar da taswurar halittar kyawun hancinsa daya zauna daram kan fuskarsa. Kafin kace mi tuni kamshinsa ya baje wajen, Gaba daya securityn ne suka sake kamewa kansu sukai cikin nuna tsantsar girmamawa a garesa. Wani irin dakune fuskansa yayi daidaj lokacin da fadawan ke zunewa akan gwawowinsu.

Sassanyan iskan dake kadawa da kamshin furanni ya sake shaka. Kafin ya fara takawa a hankali cikin yanayin izza da zallar sarautar dake ratsa shi gaba da baya. Kai tsaye part dinsa dake tsakiyar masarautar ya nufa dake dama zaid da kanshi ya gyara may tare da jesra sukai aikin.

Wohoho anan fa akeyinta mutanena Ni naga ikon Allah a wurin nan.

Tashin kai tashin gari kenan, na tabbata idan mutum karamar kwakwalwa gareahi babu abinda zai hanata juyewa a wannan lokacin, zanso ace kunga yadda

Nera da nera ke kuka a cikin bangaren Ak. Luxury da luxury life ake magana malam, komai dake Cikin bangaren luxury da luxury ne ka iya siyansa sa, wani irin mahaukacin passage ne me kayatarwa, a nutsetstsen lafiyayyen parlounshi na farko oummey'nshi sai jesra ne a zaune domin gani suke tamkar kafin goben abinda suke son gani ga gudan jinin nasu ya disashe.

Wani irin murmushin bazatane ya bayyana a saman kyakykyawan farar fuskan shi da gudu jesra ta fada jikinsa tana saki kuka mara dalili. "Trouble meker har yanxun baki girma yhuyhu gurl"

Sai kuma yadan yi jimmmm tuno waccen yarinyan da yayi. Oummey ce ta karaso itama tare da hugging yaronta tana sama lallausan gashin kansa. Gashin kansa tadan ja tare da balla masa harara irinta uwa da dan nan.

"Ouchhhhh Ommu!"

Ya fadi yana kaiwa durkushe gabanta.....

BY AMMEY LAYLERH

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page 45&46

ROMANCE

BLACK MONEY

DEEP

Hope

courage

Survival

Humanity

Inspiration

✔

Wani colourn kyakykyawan murmushi ta saki tana sake janyo kansa tana dorawa akan kafafunta.

Kafin wasu hawaye masu zafi suka shiga zubo mata. "Garga me martaba! Lokacin bayyanuwar boyayyiyar gaskiya ne yayi, Alkawarin kare masarautar EMAAR's nake son kamin....

Ta fadi hawaye sosae na balle mata wani irin dauke kansa yayi yana kallon bayansa. Sai kuma ya juwo tamkar wani zaki ya goge mata hawaye ya ce, " You don't have to cry since you have me, i promise Insha ALLAH to be there for you no matter the weather, I promise to you and I promise to be your one and only till the end of time! Na dauki Alkawarin kawar da gurbatattun cikin masarautar nan Insha Allah Oummeyyy!!!"

Ya fadi yana me dafa saman kanshi da hannunta yake hade da nashi hannun. Wata nannauyiyar ijiyar zuciya ta sauke tana mikewa tsaye.

Ganin dare ne ya sanya oum yi masa sallama ita da jesra suka tafi, har bakin part dinsu ya mikasu da kansa cikin daya daga cikin motocin da suka daukosa.

Shima zaid nashi bangaren ya wuce dake jikin ma ak din daga barin damarsa, kayan jikinsa ya zame tare fadawa bathroom wanka yayo duk da kuwa cewar dare ne, Silk kayan barci mara nauyi ya zira bayan ya feshe jikinsa da mayun turarukan.

kai tsaye lafiyayyan hadadden gadonsa me kama da alkaki ya nufa. Dakatawa yay daga shirin kwanciyar da yake ya sake dora idanunaa akan yar karamar cctv footage din dake sakale tsakanin wasu manyan flowers guda biyu, murya kasa kasa ya furta.

“camera?”

Wani irin bacin raine ya ziyarceshi lokaci daya tare da furzar da huci mai zafi daga bakinsa, sai kuma ya cije lips inshi yana ayyana shikenan da aure ne ma dashi. Camarar ta riga ta gan may mata masu ita su gane masa sirrinsa, Sa'ar shi daya shi mutum ne da bai iya tsiraichi ba kowa shi kadan sane kuwa. Wani irin naushi ya kaima manyan flowers din a take suka tarwatse.

Duk wani lango da sako na bedroom din sai daya bincike ko ina. Babu wata kamara bayan wannan din dai, fasa kwanciyan yayi ya dau systerm nashi ya fara aiki cikinta, da dukkan alamu ransa a bace yake daga yanayin yadda yake sarrafa laptop din kadai zaka gane haka.

Kiran sallar farko ya mike tare fadawa bathroom alwala ya dauro yana ficewa a part din kai tsaye. Babu wanda ya ganshi in banda ladanin daya kira sallar, Kai tsaye bangaren ladani ya nufa yana zama haka har mutane suka cika masallacin Aka tada sallah!.

Babu wanda ya san da zuwansa haka babh wanda yayi tsammanin ganin a time din, Wannan nutsatstsiyan muryan nashi shine ya ankarar da mutanen dake cikin masallacin tare da zaburar da wasu da sanyasu faduwar gaba. Haka sautin kamilalliyar muryansa yacu gaba da tashi cikin kyakykyawar kira'arsa a cikin suratul Ma'ida. A kuma daidai lokacin me martaba sarki Hassan Al-hassan gabban jikinsa suka fara motsawa ata sanadiyar jiwo wani babban gurbin dake cikin tsakiyar kokon Ranshi. Sanadiyar karatunsa daya karade baki daya katafanin cikin masarautar.

Haka muryansa ya ringa karade ko ina da ina na cikin fadar tare da ratsa zukata, inda wannan muryan dai ke firgitar da wasu! Wasu kuwa ta saukar musu da nutsuwa tare sa sanyaya gabban jikkunansu.

MOH JIDDOH kuwa wata kalan katantanwa tayi jin sautin fitar muryan da ko baka gaban me ita take da tsananin rusuna zuciyar mutum da ladabtar dashi.

AL-HUSSIEN kuwa dake daya daga cikin na gaba gaban jam'i baima san sanda kafafunsa suka soma rawa ba yana neman kaiwa zaune. Amma ya dake yaki bama ko wacce alama nuna kanta a tattare dashi, Yana sanye ne cikin cikakkiyar shigarsu

ta larabawa cikin wata farar kuwait jallabiya sai shiramin daya nade kansa dashi, sai wani farin glass din daya sanya.

Bayan idar da sallarn nashi sosae yayi karatu tare da gabatar da adhkar, Har zuwa sanda gari ya fara haske. Xuwa lokacin manyan dogaran fada sun kewaye gaban babban masallacin musamman ma hanyar da zai fito ta wurin, Wambai, Waziri, maga tajarda, Riga daki, suna can sashen me martaba zaman isowar Garga din, Cikin wannan izzar da dan banzan takun nan nashi ya fito nan fa dogawarawan nan suka masa wani irin dafifi. Kowa nason bashi garkuwa wasu suna gaba wasu suna baya.

Kai tsaye apartment din me martaba suka nufa yana a tsakiyarsu, sun sanya wasu kyawawan sandunan zinare gefe da gefen Ak din. Hasken streetlight din dake kewaye da ilahirin masarautar na sake

Duk inda tawagar Ak suka gitta hadimai zubewa suke akan gwuwowunsu suna mika gaisuwa. Ko sau daya bai daga ido ya kalla kowa ba, sai hadimansa ne ke amsama duk wanda yay gaisuwarn. Tun a harabar shiga babban sashen me martaba sarki Hassan Al-hassan din ak ya dakatar da dukkanin hadiman. Sashen Sarkin shine shahi mafi kyawu da kawatuwa da duk wasu kayan kyale-kkyale a masarautar EMAAR's din. Gini ne da aka ginashi da zallar gilashi. Yana da hawa biyar dan haka sai da lifter kana kake isa apartment na sarki hassan din, Asalin apartment nashi kenan zama lissafa muku irin uban dukiyar da aka narka a ciki ainahin fadar me marta ban batama kai lokacine kawai.

Su kansu dogayen benayen dake gine a fadar abin azo a kallo ne. Idan kahau hawan karshe kuwa na cikin ainihin fadae duk abinda ke faruwa a cikin masarauta EMAAR's din kana iya kalla daga saman fadar.

Kai hatta da wajen masarautar ma kana iya hangowa. Hadiman dake tsaron sashen matsayin sojoji suka maye gurbinsu wajen take ma Ak din baya har xuwa parlourn farko. Anan din ma hadiman zubewa suka dingayi kasa kawunansu a risine domin girmamawa a gareshi har zuwa falon na biyu. Haka anan dinma wanda suke tare dashi zuwa parlou na biyu suka dakata, na falon na biyun na take masa baya har zuwa parlour na uku suma iyakarsu nan,Anan kuwa wani basamuden soja daya ne ya masa rakiyar wanda shine amintacce da yake iya haurawa har zuwa falo na hudun. Wani badakare ne kwalli daya tal a hawan karshen wanda saida amincewarsa ne kake iya ganin Sarki hassan Al-hassan kai tsaye din,Anan riga daka ha kwashi gaisuwa wurin Ak tare da bashi izinin ganin me martaba kai tsaye.

Saida na'ura tayi kururuwar isowarshi tare da tantance shi kana ya sanya kansa zuwa hasalin FADAR EMAAR's din. Wani irin numfashi ya sauke me dumi yana jin yanda namomin jikinsa ke wata iriyar tsuma, Ahankali ya lumshe kaifaffan idonsa yana ambatar sunan Allah. Kafin ya sake bude idon ahankali kai tsaye akan MOH

JIDDOH dake harde bisa kilisa tana cin inibi cike da ƙkasaita irin ta masu isa ya fara sauke idonsa.

Itama daga idanun kadan tayi ta dube shi a sheke tare da zubarwa

tare da kara hura hancinta sama,

Wata Kujerar narkakken zinaren dake dunkule lik rug maga daka ya janwo zuwa gaban Ak. Wani irin zaune yakai zaman nan nasa mai cike da isa da tsantsar izza. Wanda hakan ke haukata wasun su domin zamane da yake fidda tsananin kwarjini da haibar da Subhanahu wata'ala ya masa.

Crossing kafarsa yayi daya kan daya yana jan trow trey'n dake gaban MOH JIDDOH wanda yake shake da yayan itatuwa.

Inebin dake narke cikin zuma ya dauka tare da kaiwa bakinsa yana dan cirar kadan. Wani irin motsa bakinsa yayi tare da lumshe idonsa saboda yadda tsananin zakin inibi da zumar suka tsinka yawun bakinsa. Tare da ratsa har tsakar kansa kai tsaye.

Wani irin marin bazata takai ma fuskan Ak din da idonsa ke lumshe MOH JIDDOH tayi. A bazatan taji shima ya rike hannunta karafff tare da bude tsayayyun idonsa yana dan girgiza mata kansa. Irin I DON'T CARE MANNER's din nan.

Kyawawan idanunta ta juya a fuskar Al-hussien sai kuma ta janyesu zuwa ga Mahboob da mandood. Dama duka sauran mutanen dake cike da dakin.

Shi kuwa Ak dake rike da hannun Moh jiddoh yi yayi tamkar besan abinda ya aikata ba, saima maida idonsa da yayi yana sake kullewa. Yanda yai tamkar besan mike faruwa a wajen ba shine ya sake hasala Moh jiddoh..

Cikin muryan daya fara manyanta amma kuma yana fita da tsananin kaushi ta furta

"Me kuke bukata da bazaku wanke min fuskan wannan tantirin yaron da mari ba! Kana kumin dumu dumu da jikinsa da duka? Ko saina baku umarni ehhhhh!!?"

Ta fadi tana watsama su Alhussuen din wani mugun kallo.

Cike da girmamawa Al-hussien ya dan rankwafa. Tare da fadin. "An gama Ya ummienah Umarninki shine abin jiranmu kana kuma wajibane a garemu"

Kamar yanda be motsaba ba haka be bude idanuwansa. Saima karkada kafafuwansa da yake yi cikin isar da yake jin yakai koma ya zartata.

Yunkurowa Al-hussien yayi da niyar kashe fuskan AK da mari. Wani irin bude idaniyarsa yayi tamkar zaki wurgi da hannun Moh yayi tare da damkar na Al-hussien din yana sauke firgitattun idonsa akan shi.

Kafin ake yayi wani abu Moh ta dauke kyakykywar fuskarsa da wani lafiyayyan mari.

"Ka sani HAU'WA KULU bata yafiya haka bata daukar kuskure koda kadan ne bare kuma me girma irin naka, ka sakar min da hannun yaro daka rike shi da kazamin hannunka da bashu da tsarki!. Ka sani taba hannun mutum irinsu Al-hussien sai hannun daya cika duka sharrudan musulinci, ba kazami irin naka ba daya gama cakuduwa da dattin zina"

Atare Oum, Adeenerh, jesra, al-mustapha suka wani irin kulle idonsu da karfin masifa.

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un!"

Oum ta furta tare da RAZEENERH da suke kira da MAH. Mahaifiya Almustapha sai kuma yarta ta fari wacce tayi batan dabi sama kasa aka nemeta aka rasa.

Shi kuwa boss din wani irin tsuma jinin jikinsa ya dauka.

A fusace zaid da bazai iya jurema cin mutumcin da ake ba biyuninsa bane ya mike.yana toshe kunnuwansa tare da furta

"STOP"

Mandood ne ya mike tsayen shima ta hanyar tarar zaid din yana jefa masa wani shegen kallo tare da fadin.

"Me yasa kake da taurin kaine?, Idan ba'a kasa dakai ba baka gaggawar dauka domin gudun abin fada ko martanin da za'a iya maida maka"

Wani shegen kallo ya wurgama mandood din tare da cewa.

"Niba rago bane da zan zauna a gaban idona naga ana aibanta jinina na kyale haka! Taurin kaine dani! Ni mutum ne da ako da yaushe yake cin nama da nama karya kasuwan nake nabi ta kansu na mitsitstsikesu domin na gama amfana da tsokar jikinsa"

Luuuuuu Ak yaja idonsa dayabi zaid dashi kamad zai kulle su gaba daya sai kuma ya budesu war akan twins dinsa gudan jininsa zaid.

Wani irin fashewa da kuka Moh tayi tana mikewa tsaye tare da fadin.

"Tabbas jinin Maryam masifa ce a garemu, ni dama tun farko banso hassan ya aurita ba wllh! Har iyaka na ketara masa akan auren wannan me bakin jinin, na rantse ba zata shigo cikin gidan a matsayin matar aure amma saida ta shigo tazo ta haifa mana jaraba da masifa a masarauta"

"Ashe kinga kenan baki da matsayi da iko akan dan da kike ikirarin naki ne, duk da kin yankamar iyaka amma saida ta ketara, kince ba zata shigo ta shigo! Ko wanne mutum yana da gari kana yana da iki a inda yake. Ba tare da kin tare ta daga shigowarma kuma ta shigo harta haifa miki magadan masarautar EMAAR's kina ji kina gani wannan masarautar ta zama tata. Wannan garin ya zama nata bayan wannan mene bakyason ta sake tsallaka miki, wannan masarautar tamu ce garin ma namu ne a gaban idonki zamu mulki masarautar dama kasar da kike ikirarin Oum bazara shigo ba. Saidai masu hadiyar zuciya su hadiya in yaso ta buga su mutu"

Ak ya yaboma Moh maganfanun da tunda uwarta ta haifeta ba'a yaba mata koda kwatancinsu ba.

"ABDOUL-MALEEK"

Muryan Oum ya katse shi daga wata maganar da yake shirin sake yanko mata.

Hatsaniyace sosai ta kaure a cikin dakin kowa yaki ya rusuna kowa ji yake da nasa zafin kan. Abinda ya rusunar da rigimar nasu faduwar da Oum tayi. Wannan shine dalilin lafawar komi haka Ak yama Oum dinsa daukar jarirai ya fice da abarsa zuwa clinic din masarautar, Shine da kansa ya duba Oum nashi kasancewarsa dactor, kana pilot ne idan yaso babu inda baya ketawa a kasashen duniya. Kana gashi Babban soldiers wanda matakin farko ma da Marshal ya soma.....

Washe gari

A nutse yake Sakkowa daga matakalar benen zuwa entrance din da zai sada shi da bangaren oum dinsa. yana sanye cikin wasu fitinannun lallausan farin yadi. yayin da kuma ƙkafarsa ke sanye cikin wani black combat toms mai kyau irin na yayan sarakunan nan, Sai wata mini jacket din daya dora saman kayan yar filic da ita.

babu abinda ke tashi ajikinsa sai wannan fitinannen kamshin turaren nan nasa me azabar tsada da bama wanda yake shakarsa cikakkiyar nutsuwa ta musamman.

Tamkar wanda akema wanka da madara haka farar fatar jikinsa ke daukar idon me kallonsa. Cikin cikakkiyar takun da kallo daya zakayi masa ka gane cewar kakkarfa ne sabo da motsa jikin da yake aduk kwanan duniya ta hanyar machine gams.

Blue eyes din nan rufe cikin wani luxury sun glasses wanda ya sake bayyana taswirar karan hancinsa da yake mike ziyat tamkar da biro aka zama masa shi daram. pink lips din nan nashi sai wani kalan glowing yake tsananin taushin na bayyanuwa wa me kallonsa, kallo daya zakama Ak ka gane shi din me kyau ne kana na musamman masha Allah,domin allah ya wadatashi da komi najin dadin rayuwa. cike da kwanciyar hankali da nutsuwa yake takawa irin takun dake nuna shidin kakkarfan namiji ne kana tsayayye. Marar daukan wargi da in Manners din nan.

Kai tsaye babban katafaren parlourn Oum dinsa yama tsinke wanda girmansa yake dauke da wasu tsadaddun furnitures, parlour ne mara tarkace amma yana da kyau na fita daga hayyaci. Kayatattun royal cushion din dake zagaye da parlourn sunyi may kawanya, daga tsakiya kuma akwai wani shimfiɗaɗdiyar red carpet da throw pillows akai, sai wani ƙkaramin round table daga gaban wani kebantaccen rug, sai babban plat screen plasma din da ya kusa cinye bango guda na parloirn don girman shi. iskan A/cn dake kasawa kai tsaye yake fidda wani irin daddan yanayi a cikin parlourn, dubansa ya kai ga ƙkaton agogon dake manne a bango wanda yake ƙkawace da zanen pop, tare da pisc na Oum shi tare dame martaba.

10:25am agogon ya buga cire pcarp din kansa yayi yana kallon ƙyakkyawar fuskan Oummey'nshi dake zaune kan caution mug ne a hannunta me dauke da zazzafan ruwan bunu marar madara.

Kallo daya zaka mata kagane ita din mahaifiyarsa ce saboda kamar dake tsakaninsu, lumshe idanunsa yayi hadi da dan sauke numfashin ganin zaune cikin koshin lafiya da yayi.

Cikin amon muryansa mai dadi da nutsuwa yace

"Takabbalallahu minna wamin kum alaina wa'alaiki ya Oummey! ". Shafa tulin sumar kansa tayi wanda yasha gyara mai kyau da sheki yayin da yake durkushe agabanta ya dafa hannayensa duka biyu a ƙkafarta, cike da kulawa tace

"Amin barkan mu da wayewar garin Alhamis lafiya habeebty"

Jesra dake tsaye hannuwanta sarke akan kirjintane ta dan turo baki gaba tare da fadin.

"Aifa shikenan nikam tawa ta kare tun da nakan gaban goshin ya dawo"

Cikin yanayinsa na rashin son magana yayi dan murmushi yana faɗin

"Kina kishi da hakan ne jes?”

ya fadi hakan yana maida kallonsa ga mahaifiyar tasa yana faɗin

"Ya Oummey nah ya saukin jikin ki?".

" Alhamdulillah naji sauki tun da ka dubani HABEEBT?,kaje ga Me martaba ya kamata ka sake auna yanayinsa Garga"

Kansa yayi noding yana mikewa tare sa barin shahin.....

BY AMMEY LAYLERH

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~□ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... □~*

Page 47&48

ROMANCE

BLACK MONEY

DEEP

Hope

courage

Survival

Humanity

Inspiration

□□□□✔

□ NIGERIA □

A kullum duniya canjama bawa ajin karatu take yau din kace kawai zata tabbatar maka da hakan, musamman idan kaga ta banbanta da ƙkaddarar jiyanka!. Rayuwa mataki biyu ce Acikin kowacce duniya duk wacce kaddararka ta zabar maka zata kaika ne zuwa makomarta, sabanin shine kawai dace wajen banbance nagartacciya ko gurbatacciya.

A yau dai ga merrah wacce take dab da amsa sunan mrs Salma isa manu, wanda komi da komai ya gama kammala kansa daya danganci bikin aurensu wanda ya rage kwanaki biyu takkk.

Kamar kullum yanzu ma zaune take a palon Annenta tana danna wayarta wajen karfe biyar da rabi na yammacin ranan alhamis.

A zahiri danna wayar take amma a badinin ta ita kanta bazatace ga abinda take aikatawa a cikin wayar ba. Abinda kawai ta sani shine tana lallatsa wayar ne.

Sallamar da aka yine ya sanyata dagota da kanga. Hajiya ummace ta shigo da sallama rataye da jaka a hannunta.

Mikewa tayi ta nufeta tana murmushi ta amshi jakar tana fadin "Hajiya sannu da zuwa"

Zama tayi akan kujerar palon kana ta amsa da cewar "Yauwa Merrah na biyo sahun kine dama kwana biyu shiru bakya zuwa. Ni na rasa wacce iriyar amaryace wannan ace gyaran jikinka ma gudunsa kake?' Kyaje gidan ne mijin ya koroki astagfiroullah

Allah na tuba. Wllh tsaya kiji wannan bikin da naje Ikaja. Bayan kai amaryar da kwana biyu mijin nan ga daho kaza a dafe rigijff tasha kayan miyarta sharr. Ai wllh nake baki labari yakai gidan su amaryar nan bayan uwarta taci taji salam babu komi tace wannnan ai kunyi mantuwa babu komi a ciki na kayan hadi. Kinsan me yace ce musu yayi yanda sukaji kazar nan haka yaji yar su, to yanzu dan Allah me amfanin hakan? Wllh babban gata nake miki yar nan"

Wani murmushin da baikai zuci ba meerah ta saki tana sunkuyar da kanta kasa. Acen kasar zuciyarta tana furta

(Ni wllh da yamin daidai kuwa amma fa ni bama yarda zanyi wannan me kama da birin ya taba niba, bare ya hada jiki dani nevermine wllh)

Fitowar Anne shine ya katse meerah daga duniyar tunanin data fada. Kallo daya Anne ta mata ta dauke kai tana karasawa inda hajiya umma ke zaune. Gaisawa sukai nan suka fada wata maganar daban ba wacce hajiya umman keta kokarin ganin ta kawota ba.

Jakar kayan Anne ta turama meerah tana fadin taje tayi amfani dasu kafin ta shigo dakin itama. Hayaniyar data kaure a cikin gidan ne ya sanya su umma fita.

Wata matashiyar mata ce wacce taci wani ubansun ado jikin farin leshin daya sha doguwar riga half bubu, sai farar siririyar yarinyar dake gefenta cin mutumci take zuwaba a cikin gidan tana fadin sai an nuna mata uwar data haifi amaryar da ake shirin likama dansu, dan son zuciya da bakar zalama anga gidan arziki shine za'a likema dansu...

Kallo daya Anne ta watsama matar ta dauke kanta tana komawa inda ta fito, shunenta maman affan ta mata ai kuwa ta tafi zata fusgo Anne.

Wani irin juyowa Anne tayi tare da watsa mata wani mugun kallon daya sanya maman sury jan burki daga shirin fusgar da taso yima Annen.

Tsananin kwarjinin da idanuwan annen suka mata ne ya sanya ta hadiye sauran maganganunta, tana kama kanta cikin muryan da baya daukar wargi ko wanne ta furta.

"Idan har kun isa da danku kuje gida ki hana a daure aurensa da DIDI!, jinina yafi karfin a wulakanta shi haka jinin Ayshatul humaira ba daskararren jini bane jinin dake gudana a jikinta tafarfasa yake ya tafashensa yake. Tafi karfin ta hada zuriya da gurbat.....

Maganar ce ta yanke mata sakamakon rufe bakinta da hajiya umna tayi. Ita kuwa sury tuni ta makale jikin mummynta haka nan ta tsinci kanta da shakkun matar ba karamin kwarji ta mata ba.

Daya bayan daya matan gidan suka fara zamewa domin su kansu ba karamin gwarjini Annen ke musu ba barin ma idan halinta najin kai ya tashi.

Su kansu yayanta wani bin sai su wuni ba tare da kalma daya ta shiga tsakaninsu ba, wannan halin nata kuma ba karamin tayarma da malam abdullahi hankali yake ba.

Jan hannunta umma tayi suna komawa parlournta. Nan ta shiga bata baki amma samm taki tanka mata ita kanta tasan wannan gwamutsen hadin auren ba son shi take ba, to amma ya ta iya.

Ta kasance matar da bata jayayya da hukincin ubanhiji in banda haka ko ita da tuni ta farke wannan auren da take ganinsa kamar ba tabbatacce ba har waye war garin yau din. Har yamma hajiya umma na gidan....

Bangaren meerah kuwa haka tayi wunin sukuku gashi ba damar fita bare ta dan fita ko ta samu full energy nata ya dawo. Ta hanyar shakar iskar wage, abincin da tun dazu Anne ta tura mata take ta faman jagwalgwalawa, ita bata ci ita bata dena jujjuya shiba. Har saida hajiya umma ta fasu ta furta.

"ya abincin gabanki tun dazun kinki ci sai famar jagwalgwalashi kike?. Meye haka kike yi da abincin nan meerah?" dago kanta tayi ta kalleta Itama Anne sai ta maida attention dinta kan meerah din. Wani dan murmushi ta saki irin me ciwon nan kafin a hankali tace.

"Umma kinsan dazu da yamma na ci

Wannan abin sam bana wani jin cin abincinne kawai na ji yanzu bana jin yunwar ma"

"Toh idan baza ki ci ba ki rufe anjima kyaci" tashi tayi sai kuma jiri ya dibeta ba tare da kowa ya lura da hakan ba Kawai sai faduwarta suka ji. Da sauri Anne ta nufeta tana jijjigata, dakatawa tayi sai kuma ta juyoo da kallonta zuwa ga hajiya umma tare da furta "Bata numfashi"

"Subhallah dama ba jiri bane ya dibeta?". Hajiya umma ta fadi tana yin kan meerah din " Maza kira malam ki sanar dashi Ayshatu" hajiya umma ta fadi cikin kidima domin ba karamin tashi hankalita yayi ba.

Cikin kankanin lokaci saiga malam tare da Ibrahim babban dansa. Fito da ita sukai suka sanya a mota suna nufar hospital drektly....

A hankali take bude idanunta da sukaimara masifar nauyi, dan motsa idanunta tai tare da dan cije leɓe kadan.

kafin ta samu nasarar bude ido da ƙkyau. "Asibiti kuma?" Ta ambata a hankali tana dan waige-waige da kallon dakin data bude ido ta ganta cikin bazata.

Nan komai ya shiga dawo mata sai kawai ta koma tana jingina da jikin gadon, lokacin wajen goman dare.

"Meerah ashe kin tashi ma?"

Hajiya umma ta fadi tana komawa don yin magana da dactor. Tunda Anne tana gida babu jimawa hajiya umman tace taje. Ba don taso ba ta tafi tana tunanin damuwar da ake taima didinya yawa da kuma yawan tunani.

Sai gasu ita da nurse ta dawo sake aunata nurse din tayi nan tace ma da umman babu wata damuwa insha allah zuwa safe ma zasu basu sallama. "Zanyi sallah ummah"

Meerah ta fadi cikin muryan da yayi low sosae.

Da taimakon Umma ta sakko a gadon sai yanzune ta kuma fahimtar a daki na musamman take, kuma ita kadaice a ciki hakan ya sanyata kallon umman da alamun tambaha.

"Bamusan wanda ya sanar masa ba muma kawai ganinsa mukayi yazo ya sanya an sanja miki daki" dan lumshe ido tayi tana jin ma sam.. Bata son ci gaba da zaman hospital din. Sallan magrib da isha'i ta kawo tana koma ta jin gina kanta da karfen gadon.

Sallamar salman din itane ta katse mata rufe idon da take niyar yi. Hannuwansa rike da manyan ledojin shopping ya shigo. Gaida umma yayi ts amsa tana tsokanarsa da angon kwana biyu. Dan murmushi yayi yana shafar sumar kansa yana jin wani irin madararn dadi na lullebeshi. Don ji yake tamkar ya jawo wannan kwanan biyun su dawo yau, kamar ya janwo nesa kusa haka yake ji da yana da damar hakan da tuni ya dawo da nesansa kusan sa. Kodan muradin wannan lafiyayyan jikin da yake ya kwadaitu sosae da sosae da tsarin halitta da kuma surar jikinta.

Kallo daya ta masa ta dauke kanta shine ya gaida ta tare da mata ya jiki ciki² ta amsa. Nan ya shiga yar firarsa da umma domin gwanar tamu taki ko saurarensa.

Kiran wayar sa friend's nashi suka yine akan sun sauka lafiya suna airport yazo ya dauke su, shine ya san yashi masu sallama yana cema umman abokanan sane suka zo domin tun gobe juma'a zasu fara shagwalgulan bikin. Yama so ace tun laraba suka fara amma malam da kanshi ya dakatar da hakan. Domin ya kawoma meerah katunan shagulgulan ne d nufin ta rabama friendies nata, wannan shine dalilin dakile maganar da malam abdullahi yay, ba tare daya sani ba kuwa haka salman da manyan abokanansa suka kama manya manyan hotels dake garin lagos dim suke abinda suka ga dama.

Ta hilton hotel yabi ya taho da wasu domin debo manyan friends dinsa. Ajeborters na waje sa sauran garuruwa, a lokacin dayay ido biyu da dolly ba karamin baci ransa yayi ba domin idan ya tsani abu ya tsane shi kenan. Haka idan yaso tofa ya so shi kenan da dukkan zuciya da ruhinsa. Cikin kaushin murya ya kalli moussa yana fadin.

"Kaine kazo da wannan abin ko?"

Ya fadi yana masa nuni da dolly wani kafurin murmushi dolly ta saki tana " hey beb baka happy da zowa na ba kenan?"

Tana shirin rungume shi ya ture ta a jikinsa yana fadawa motarsa yana fadin.

"Le's go guys ku muje ko?"

Sauran motocin suka shishshiga suna barin airport din tare da kama hanyar hilton hotel dasu..

Tun da suka shigo harabar hotel din suka soma jiyo tashin sautin Wakar da aka sanya din. Irinta shegen nan wanda suka rike a harkar tantiranci.

Tab katon harabar inda suke yake da wayayyun matasa da yan mata 'yan bana bakwai,wadanda rayuwa da kuma duniya ke musu dadi suke cashewarsu cikin kwarewa, wasu babu kayan arziki a jikinsu mafi yawan mazan kuma gajerun wanduna ne a jikinsu.

Hannuwansu dauke da manyan kwalaben giya wasu cigarette's ce a hannunsu suna busa hayaki. Wasu kuwa pep na shisha ne a ganansu suna zuka su fesar da hayakin cikin wani dan iskan salo.

Tun kamin motarsu ta gama parking dolly dake sanye cikin wasu shegun outfit riga da wanda na baxon ta balle murfin motar fa fito. Akan inda giya, shisha, cigarette's coc suke ta fara nufa kai tsaye. Shishar ta dauka ta mata wata kafurar zuka tana baza hayakinta daya hada hoton love. Zaune takai akan almurun kujera. Tana zare wawakeken shade din daya kusan cinye rabin fuskarta.

Mafi hankalunan yayan ajebor din dake zagaye da wurin ne ya dawo kanta, Nanfa suka mata caaa aka har wasun su na kakarin kama hannuta donsu shakata tare da ita. Kai tsaye club dancing din ta shige ya soma wata kalar rawar daya sanya manyan yaran daukar ihuuuuuuu suna sowa.

Nan fa kowa ga fara kokarin isa ga dolly saidai taki ba kowa damar hakan. Har suka karaci shedancinsu suka tashi wajajen karfe biyun dare.

★★KANO★★

Idan muka koma kano kuwa sosae rayuwar kamal da mariya ke gudana cikin kanciyar hankali, akwai girmama juna a tsakanunsu sosae suna zamansu lafiya yau kimanin kwanakj tara kenan da aurensu. Amma babu abinda ya taba shiga tsakaninsu. Hasalima kowa daki daban yake kwana abinsa. Sammm daga shi har ita babu abinda ya dame su kowa ya harkan gabansa. A kullum zata shiga dakinsa ta gyaro masa ta kuma wanke masa ƙananan kayansa a washing machine. Kamar kullum yanzu ma aikin gyaran ɗakin take hankalinta kwance, ɗomin dama sauya fita take shigowa ta gama masa Aiyukansa ta tafiyarta. Riga da wando ne a jikinta na palazzo ride vizzon ruwan kasa inda rigar ta kasance baka irin me kamar robar nan. Kanta babu ɗan kwali sai fakin gashinta da tayi a ƙasan ƙeyarta. Bluetooth ne a kunne ya tanaji latest waƙar Hamisu Breaker me taken mu daina TSORO. Wanda wakar yake ratsa zuciyanta kai tsaye, domin tabbas talakan kasa shine a wahale babu tsoron Allah a zuciyoyin shuagabannin mu. Kana babu tsoron Allah a wajen wasu jami'an kasar.

Tun ɗazu yake tsaye yana kallonta a ƙalla ya mata sallama sama da sau uku amma shiru bama ta jishi ba. Wani kakan shagaltar yayi a kallonta yadda take motsa ƙananun laɓɓanta shi yafi komai tafiya da imaninsa, aikinta take cikin nishadi da nutsuwa harta kammala ta juyo da biyar tafiya, Nan sukayi hudu dashi saurin ja baya tayi tana sunkuyar da kanta kasa tare da faɗin.

"Kayi mantuwa ne yaya?"

Ta tambaye shi,shiru ya mata yana sake kureta da mayen kallonsa. Jikinta ne ya ɗan soma rawa kaɗan Idanunta na cikowa da kwalla. Gudun ko ganinta a dakin sane ya ɓata ransa, "Don Allah kayi hakuri!" Ta fadi muryanta na karyewar sansomin kuka. Komai baice mata ba haka ta raba gefensa ta wuce....

Taku ɗaya tayi a na biyu taji lallausan hannunsa cikin tafin hannunta, cak ta tsaya zuciyanta na bugawa domin duk tsawon zamansu ko yatsarta be taɓa kwatankwacin kamawaba.

Juyowa tayi Idanunta na zube da hawayen da take ta kokarin ganin boyewa. Ta buɗe baki kenan da biyar sake bashi hakuri ya taryi nata numfashin ta faɗin.

★I LOVE YOU★

Wani irin yankar kirjinta taji yayi numfashin na kokarin barin gangar jikinta. Dagowa tayi a tsorace hakan ne ya bashi daman tallafar fuskanta yana jefa idanunsa cikin tsakiyar nata idanun. Wani kalan mamular baki tayi Idanunta na far far. ★And I really love you 2 appreciate my love★

Kalamansa suka dade mata dirar MIKIYA a tsakar kanta. "I lOBE YHU MARRIYERTOU" ya sake faɗi yana janyo ta zuwa cikin jikinsa. Xuwa lokacin kuwa ƙafafun kariya sun soma rawa tana dab da kaiwa kasa ya rigata yana dorata a kan ƙafafunsa.

Ji da ganinta ne suka dauke na wuccin gadi, {KAMAAL?} Ta tambayi zuciyarta ta hanyar furta sunan sa a cikin zuciyar. Hannuwansa dake cikin nata har loƙacin ta damke da karfin daya sanya kamal ɗago kansa yana me sake dubanta kaɗan. (KAMAAL!) ba tare data sake fargaba zuciyanta ya ƙara ambatar sunan. "Yeah KAMAAL SURAJ RANO na tsananin ƙaunar MARRIYERTOU fiye da duk yadda zaki zata"

"Kasan kuwa da wace kake tare?. Tare kake da Mariya Mariyan da sau uku anasa bikinta ana fasawa, wannan mara sa'ar! Wannan wacce ba kowa bace ita fa ce wacce ta tashi cikin tsananin rayuwa? Sammm Ni banyi zubi da kalan matar auren kaba yaya KAMAAL, A nawa tunanin ka aure nine domin cire mahaifina daga cikin damuwa. Ka aure ni domin kana tausayinmu wacce zaka iya sak.....

Bata karasa ba ya rufe bakinta da nashi tsawon minti uku. Sai kuma ya ɗago idanunsa na tara ruwa.

"Na aurekine don ina sonki MARRIYERTOU! Na aureki bisa jagorancin zuciyata domin tun baki kai haka ba nake jinki har cikin raina!, Yanayin nutsuwarki, kamalarki haɗi da kyawawan halayenki ban bayyana miki bane gudun kada na ɓata alaƙarki da tsofaffin samarinki. Amma sai gashi Allah ya bani ke ta inda banyi zata ko tsammata ba!. Sai da nayi azumin kwana uku na nuna godiyata ga Allah daya bani ke a matsayin matar aure na, Alfarmar dazan nema daga gareki shine kawai ki SONI!, Ki SONI kada kwatankwacin yadda nake muku ne inason mu rayu cikin aminci bisa jagorancin tsabtatacciyar soyayyar da zamu gudanar a cikin rayuwar zaman aurenmu!"

Sosae ta sake ƙanƙameshi tare da sake shigewa cikin jikinsa tana sakin wani irin kukan da batasan dana me zata ƙirashi ba, kukan farin ciki ko akasin haka?....

"Nasha tazarar dake tsakanin mu irin tazarar sama da kasa ne yaya KAMAAL! Na zata SO be yimin adalci bane dana kamu da son wanda nasan bazan taɓa samu ba har gaban abada a matsayin mijin aurena. Nima INASON KA YAYA KAMAAL! Inaga tun kamin ka kamu da soyayya nina kamu da taka soyayyar yaya KAMAAL. A zatona kamin zarra kafi karfina tako ina Shi yasa na bisne hakan a cikin cannn karshen zuciyata! I LOVE YOU FOR EVERYTHING my Ayh"

Kanta ya dora akan kirjinsa tana jin yadda zuciyarsa ke bugu fat fat. "Da gaske kike? Da gaske kina sona Mrs Ayh?"

Ya fadi kuma yana jefa idonsa cikin tsakiyar idonta, kanta ta gyada mishi tana sake lafewa a jikinsa.....

Bakinsa ya haɗe da nata daga zaunen yana mata wani irin lafiyayyan Romance. Daukarta yayi cilak yana shigewa bedroom nashi, a ƙalla sun ɗauki good 30 minutes kana suka fito hannunsa riƙe da files ɗin daya dawo ɗauka.....

Wurin aikinsa ya koma kai tsaye domin kota halin yayane so yake saiya cafke me lefin nan, haka zai ci gaba da zakulo manyan masu laifukan da suke ɓuya ta karkashin kasa. Kai tsaye Lafiyayyen office nashi ya wuce Saida yayi wasu yan rubuce rubuce akan file ɗin kafin ya janyo laptop dinsa copying komai yayi ta ciki.

Wayansa da yay ƙara ne ya fidda woyace me muhimmanci dole ya amsa, bayan sun gama ya kunna data da niyar turo sako ta Whatsapp sai abubuwa suka yi ta faɗowa saman screen ɗin woyan musamman ta peonies.

Da niyar share sakonnin Ni yaje amma saiya dakata ganin hoton kamilallar fuskan da bazai taɓa mantawa da ita bane akayi wasu rubutuka akai. Kai tsaye ya gane pisc ɗin na ranar dazai bar kasar ne.

★WANTED?★

Ya sake maimaitawa wani guntun murmushi na kufce masa kaɗan.

"Ya baku baya kuyi duk iya yinku har zuwa makura maza kuyi ta Aman wutarku, don shi idan ya tashi wanka da wutar yake bi ma'ana wankan wuta fire □□□"

Manna woyar yayi da fuskansa yana sakin ijiyan zuciya bayan yayi wani short rubutu akan fuskan AK ɗin daya juya.

BY AMMEY LAYLERH

□ MIKIYA □

~We want an end to oppression□~

https://chat.whatsapp.com/GiLzmY90dz17bRbw5yMYBg

_____

MARYAM NASEER

~AMMEY LAYLERH ✍~

✯ *~ JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... ~*

Page 49&50

ROMANCE

BLACK MONEY

DEEP

Hope

courage

Survival

Humanity

Inspiration

The Beginning of the Beginning

✔

Akace salati baya hana ɗaukar rai kowani rayuwar ɗan Adam akwai salon ƙaddarori masu tarin yawa, akowacce duniya akuma koda yaushe kaddara tana tafiya ne daidai da rayuwa, haka kuma tana rayuwa da mune cikin farinciki ko akasin haka.

Sannan kuma babu wani bawa wanda ka iya gujema tarin ƙaddarorinsa lallai ƙaddararmu tana gudana ajikinmu ne kamar jini, akowace rana abubuwa mabanbanta suna faruwa to haka itama ƙaddara takan iya sanjama bawa ako da yaushe, haka kuma babu bawan da yake iya sanja tarin ƙalubalen yadda ƙaddararsa tazo mai ayau gani a daren juma'a wanda wayewar garin azabar itace zata zamo ranar da ALƘALAMIN ✍ ƘADDARATA zai ci gaba daga ranar daurin aurena. Ko wacce ƙaddara tana zuwarma ko wanne Muminine feji bayan feji haka ko wanne feji yana dauke ne da nashi salon rubutun.

♡☆❤♡♡ ☆

♡NIGHT IN THE MORNING♡

Du inda ka gimla ta cikin shilton hotel ɗin sautin Night music ne ke tashi. Wata iriyar badakalar rawa ake gudanarwa a cikin hotel ɗin. Duk wasu yayan manya kuwa wanda basu samu halartar sauran shagulan dasu Salman suka shirya ba to ayau kammm sun sami isowa, domin na daren yau din shine shakundum.

Wadan da manyan yara suka shirya ma Salman ɗin ♡BACHELOR's NIGHT☆ duk wasu yan gang bang nasu masu ji da fatu da tsantsar wayewa suna cike a wurin. Kallo ɗaya zaka ma wurin ka gane Are not my kind of people domin bana kowa da kowa bane.

Kowa ka kallo yana tare ne da Ben ɗinsa suna kwalɓewa a tare wasu kuma Romance na junansu suke. Kamar yadda uban gayyar da yake tare da dolly ɗinsa da suka shirya tun daren jiya, yanzu ma rungume suke da juna daga shi se wata shegiyar fit out ɗin riga da wani guntun wando, gaba ɗaya gaban rigar a bude yake sai sake shigar da kanta da babu ko wula take. Kwalbar wine ce a hannunta idan tasha saita bashi.

Daga nan surar ta yayi suka faɗa wani bedroom wa'iya zubillah, babu ruwandu da jama'ar dake dakin wanda suke aikata masha'arsu. Suma wani wurin daban suka faɗa.....

★RANA BATA ƘARYA

Masu iya magana suka ce wai Rana bata ƙarya sedai uwar ɗiya taji kunya.

Ni Meerah Ayau nafi kowa yarda da batun domin kuwa nima da kaina na yarda wannan rana tawace kam. Domin A yau gidanmu cike yake taff Yan uwa na kusa dana nesa duk sun gama hallara kansu. Ta ko ta ina hayaniyar yan bikice kawai ke tashi masu farin ciki nayi haka basu baƙin cikin ma duk nayi. Ga tarin abinci kala-kala da ake ta hidimar yi saidai kash! Babu dangin Anne'nmu ko ɗaya. Sai Hajiya umma kawai wanda za'a ƙira da dangin Anne'n sai kuma mutanen da ake mutunci dasu.

Zai wasu yan ƙananun gulmace gulmacen dake tashi wai babu abinda Anne tayi tanadi na biki. Tanaji tayi shiru ta share su domin ita sammm wannan ba matsalar ta bace, Ni kuwa Ina cannn kuryar ɗakin Anne'n zaune cikin shigar wani mayen leshi maroon color's.

Wanda yay masifar fitowa dani sai na tashi tamkar wata irin jinin larabawan nan ko kasashen ketare, ga gyaran da aka min ya sake tsatstsafo da zallar kyawuna na asali sosae dan ba ƙarya Anne tayi ƙoƙari ba lefi ita da Hajj umma. Acan ƙasan zuciyata kuwa jina nake duk wata iri kamar yanda aka san duk wata amarya da shiga irin wannan yanayin a irin ranar Ranan. gefe.Shigowar Disha da wasu kawayena suna rangada min guda aka shine ya sake sanyaya jikina sai kace ba wannan meerah'ɗinba yar zafin kai. "Allah yayi an daura amarya a gidan Salman, Ni zaki fara Bama wannnan kwallelen farin goran albishir ɗin"

Ban sake tsinkewa da lamarin ba Saida naji shigowar babban yayanmu yaya Ibrahim. hakan shiya sake tabbatar min cewar shikenan an ɗauro auren. gabana sai ya shiga wani irin luguden daka da sauri-sauri wani irin tsoro da fargaba na ratsa min cikin ɓargo da duk wata magudanar jini ta jikina. Shikiyancin da su disha sukaci gaba da min tare da guɗa a saman kai shine ya sake tattare duk wata nutsuwa data saura wa jikina. Sai na samu kaina da sakin hawaye masu zafin gaske da ban san dalilin yinsu ba, domin na gagara banbance komai a yanda ya dace na fahimcesa wanda kai tsaye Ni zan iya kiransa dana baƙin cikin zama mallakin Salman da nayi a wannan rana. Bugun da zuciyata taci gaba yine ya sanya ni lumshe idona a take wasu hawayen suka sake sakkomin. Shewa da dariya suka shiga min suna cewa duk hawayen farin cikin mallakar Salman ne ai hawayen. Ni kuwa ni kaɗai nasan kalan yanayin da nake ciki. Ya tabbata kenan ƙaddarar wani sabon fejin ta sake buɗe min? Ganin kuma yanayin sanyin nawa yayi yawane ya sanya su disha kyaleni, batare da sun fahimci kamar akwai abinda ke damuna ba don sun dauka yan izzar ne a kusa.

Daga can tsakar gida kuwa taro yay taro gida ya sake kacamewa da hayaniya irin ta biki, Wasu na hotuna wasu na kwalliya wasu na hirarsu haka ma masu aikin abinci nayi. Bayan daura Aure da kamar mintina ashirin baffanmu ya ƙira Anne, bata ɓata loƙaci sosae ba ta dawo fuskanta da ɗan sassauci ba kamar kwanakin bikin ba. Nan abokan zamanta suka shiga kus kus a tsakanin su bayan sun gama

gulmar wanne irin sulun bikine da babu dangin mahaifiyar amarya, a loƙacin ma Saida Aunty labiba babbar yʼar Hajiya umma ta taka musu birki kana suka shiga nutsensu. Domin kowa ya san labiba bata da mutunci kona miskana zarra.

Nan akaci gaba da shagalin biki kowa be tsinke da lamarin ba Saida Anne ta fito cikin wata rantsatstsiyar shigar farin less. Howowo zanso ku hango yadda Anne ke walainiya cikin danyen leshin data dautsa.

Mu kuwa muna can uwar ɗakan Anne wajajen lassar la'asr Aunty labiba ta shiga tare da aunty adawiyya da baby autar Hajiya umma suka shiga niki niki hannuwansu dauke da wasu shegun bags har guda uku. Badan kar ace na fiya kyauyanci ba dana rantse ban taba ganin kome kala da bags ɗin ba. Zama suka yi fuskar ko wannensu dauke da murmushi a fuskarsa.

"Amarya ya kamata ki sanjà shiga ga sabbin kayanki da Anne'nki ta sai miki na fitar biki su zaki sanya"

Ijiyar zuciya na ɗan sauke inajin yanayin bugun zuciyana ya sanjawa tare da cinkushewar yanayin dana tsinci kaina a ciki.

"Amma aunty adawiyya wannan shigan na jikina ma ai babu laifi nake ga, nifa bana gayyar kayan zafin nan!"

Meerah ta fadi tana miƙewa tsaye banɗakin cikin dakin ta shiga alwula ta dauro kamar yadda aunty labiba ta faɗa. Nan kowa ya shiga yin alwular muka gabatar da sallar la'asr. Bayan mun idar aunty baby ta shiga tsara min kwalliya a fuskana duk da banso hakan ba. Gashin kaina da shi kansa nasa gyaran na daban ne aunty baby tama wani irin style. Ta raba shi biyu ta kai har karshen ƙeyata wanda ya sauka har gadon bayana wasu shegun style ta shiga yi da gashin. Saida ta kammala kana ta sake nado shi da ribom's. Wata fitinanniyar riga da sket half bubu na wani shegen luxury catton less, irin me haɗe da jakar nan ta tamarmi sai mayafinsa. Wasu shegun barima me kama da diamond ta sanya min tare da zobenta da agogon hannu. Ya subhanallah a take wani irin kyalkyali ya shiga tashi a jikina. Ga wasu Mayun turarukan da ban taɓa jin koda irin ƙamshin su ta shige ɓarinsu a jikina. A take dakin ya ɗauki sowar kawayena jan hannuna aunty labiba tayi tana faɗin ALHAMDULILLAH sai gaban Anne da baffa har dama wanda basu so ganin wannan babban rana ba, namu ba irin nasu bane.

Ina sanyo kafata tun bai kai ga fitowa ba duk wata jama'a dake tsakar gidan suka zubo idanuwansu a kan bakin kunshin daya wani irin sake fidda kyawun kaɗana. Kwallace take kokarin zubo min ganin tabbas waɗan nan mutanen sun taru ne a yau domin ni, hannuna aunty labiba ta janyo tana karasa fiddo ni zuwa tsakar gidan. Wani irin tsitt duk hayaniyar data kacame gidan a ɗazun sukayi. Ko wanne idonsa na kaina, harda masu sake mitsirtsike idanuwansu.

Wata babbar guda Hajiya umma ta saki tana cira hannuwana sama tare da sake ranbada gudarta tana faɗin.

"ALHAMDULILLAHI! ALHAMDULILLAH!! ALHAMDULILLAH!!! Yarinya tayi goshi Ubangiji ya baki zaman lafiya tabbatacciya a gidan aurenki MEERAH, Allah ya kare ki daga dukkan sharrin masu sharri. Allah ya tsoka ne idon makiya akan wannan auren da Allah ne ya hada shi, bawai mutum ba saidai Allah Wllh kuwa mutum din zaija da ikon Allah to bismilla!"

Duk wannan abin ciki daga murya Hajj umma tayi nan fa wasu suka sha jinin jikinsu domin kaff ya'yan baffa mata babu wanda yaba Anne ko gudun mawar nera biyar. A cewarsu a gudun mawa karin ƙarfin biki.

Nan marasa kunyar cikin su suka shiga amshe Hajj umma suna shiga tare da jeruwa da meerah ɗin aka fara buga photuna na garari. Babu kunya Anne ta rungume DIDIꞌƉINTA aka musu photos da yawa. Nan manyan yayye maza ma suka shigo akaci gaba da hotunan Raiha ce nanuke da meerah duk inda ta yi cikin tata shigar na cotton less.

Nan fa gida ya sake ɗaukar hayaniyar data fi ta ko yaushe kawayena kuwa sunyi cannn ta bayan kewayen gidan sun kafa party tare da shan disko harda mardiyya da bama shiri, dake dama rashin shirin akan hayatuddeen ne saita sauke ta shigo ake shan shagalin da ita. Wajajen sallar magariba kawaye suka fara mitar basu ga ango yazo ba bare ayi zancen photo dake baby na tare dasu sai tace musu ai suma suna da party'n da suke yine da an daura auren shi yasa bai zoba.

OHO nidai bansan abinda ake ba domin ina cennn ɓangaren baffa wani zazzafan zazzabi ya rufe ni tun ina dauriya har Saida ya kaini ga kwanciya. Nan baffa kuwa ya sameni da nasiharsa na komai naga ni a lamarin aurena tabbacecce ne tun daga rabbi izzati, karna yadda nayi jayayya da hukuncin da Allah yay min. Kana karna taɓa butulcema zabinsa na zama mace mai tsananin haƙuri da biyayya a gidan aure na Insha Allah zanga sakamakon auren nan ko bayan babu ransa. Abinda ya sake sanyaya jikina kenan sai kaina ma ya soma sara min.

Ana idar da sallar magariba yꞌan daukar amarya suka zo, tun kamin suzo nake wani irin kukan daya sanyaya jikin kowa dake gidan, kira nake Ni Wllh nama fasa wannan Auren dama ai banaso don karnama baffa musu ne ya sanya ni amincewa toni Wllh na fasa. Nan na tayar da hankalin Anne'na da baffa dama duk wani masoyina, wata irin nasihar dahar nabar duniya bazan taɓa mancewa ba Anne na tamin haka ma baga Hajiya umma ba, domin nasihace irin me ragargaza zuciya harma da ratsa gangar jiki. Nidai kuka na nake a haka har dangin ango suka zo tafiya dani.

Nan fa na ce bansan zance ba na rike hannun Anne na kakam ina risgar kuka.

"Ki sani wannan tafiyar itace mabuɗin bude abubuwa da yawa meerah! Bawai kuka nace kimin ba jarum taka yaka mata ki nuna, yanxu an dena kuka dan anyi aure. Bare ma ki sani naki auren yasha banban da saura, Ki nuna musu ke kibiyar ajali ce wacce sulke baya iya ratsata! Ki nuna musu kedin jinin da.....

Wata farar dattijuwoce tayi saurin damkar hannuna da nata lallausan hannun, wanda ya hanani karasa jin me Anne na take nufi a gaban da ɗin nan?, Motocin da baka ganin iyakarsu wanda tsadarsu kaɗai kan iya juyarma dame ƙaramar ƙwaƙwalwa kai. Cikin kuka nake don haka ban tantace ya kamanni da kalansu yake ba nadai san ban iya hangar iyakarsu. Kar kuce wai bana lura a ah ina lura da komai domin idan naji ana magana har wani sake leƙo da kaina nake. Da bismilla wannan matar ta sanya na shiga cikin wata narkakkiyar Toyota Highlander 2024/2025 bugun American.

Ido a rufe yake amma sanda kamshi da sanyin daya ratsa ko ina na jikina ne ya tilas tamin buɗe jajayen idona da sukaci kuka.kallo ɗaya nama motar na furta.

"Allah ya isanmu" na faɗa kasa kasa ɗan nasan da kukaden mu talakawan kasa aka siya wadan nan shegun motocin.

★SALMAN POV★

Sabo da tsabar farin cikin da yake a ciki jinsa yake tamkar an yimay bishara da gidan aljanna, wai yau shine ya mallaki meerah a matsayin matar sa shi kuwa me yafi wannan daɗi a duka cikin tarihin rayuwar sa.

"BABU!"

Ya fadi a fili lokacin da jerin abokan sa suka yo masa rajiyar angwaye. Haka ya kemashe idanunsa yace babu me shigar masa gida wai shi a matse yake don haka kowa ya kama gabansa. Nan fa suka shiga masa tsiya suna cewa zasu rama ne. Shi dai bai damu ba kansa ya mayar da get ɗin gidan ya rufe dan yasan zuwa yanzun kowa ya kama gabansa.

Har wani sassarfa yake haɗawa da ita wajen isa ga muradinsa meerah wacce kullum sai yayi mafarkinta suna sheka soyayyar su...

Jiki har mazari yake sanda ya ƙarasa shigowa palon gidan da yaji wasu shegen kujeru na alfarma. Da dai yaga saurin kamar bazai masa ba sai kawai ya kwasa da gudu sama kai bedroom ɗin daya tabbar da anan aka ajje masa amaryarsa ya tura.

Tana zaune cikin lullubinta har yanzun kuwa ga wani kamshi dake tashi daga jikinta, wata kakkaurar ijiyar zuciya ya saki yana jingina da jikin kofa domin gani yake kamar bazai zo yagan taba. Amma yanzu ALHAMDULILLAH hankalin sa ya kwanta. Ajje ledar da abokanan sa suka bashi yayi saman stool.

Zama yayi kusa da ita ba tare dako sallama ya mata ba, kai tsaye ya sanya hannunsa yana janye lullufin fuskarta zuwa kan shoulder nata.

Wani irin zabura yayi yanaja baya idanunsa na firfitowa wanda suka bayyanar da tsoronsu a fili muraran.

"Sury miya kawoki nan? Ina Meerah? Ina aka kai min Matana!?"

Sune tambayoyi uku a jere daya jefa mata lokaci daya bakinsa na rawa.

Wani irin murmushi sury ta saki tana gyara zamanta tare da duban shi kaɗan, sai kuma tadan shiga jujjuya idonta tana faɗin. "Uyummm wacce mata kuma kake da ita bayin Ni! SURAYYERH MOUSSA CANJI?"

A matuƙar tsawace Salman yace.

"Malama ina magana kina maida min amsa zaki buɗe baki ki bani ina matana? Ina meerah ɗina take?"

Wata shegiyar dariya sury ta sake saki irin ta rainin hankalin nan sai kuma ta mike tsaye tana ɗan juyi a gaban sa. "Yanzu dame wannan kodaddiyar yarinyar ta fini?, Kyau?, Dirin jiki?, Ko kuma wayewa eyeeee Salman?, Ka faɗamin ka bude baki kamin magana"

Wani irin kwafka yakai mata yana damkar wuyanta cikin tsantsan ɓacin rai ya furta .

"Tambaya ta karshe ina meerah ɗina take? Wllh³ sau uku kenan idan har baki bani amsana na rantse saina rabaki da numfashin ki sury"

Tari ta shiga da kakari da hannu ta masa alamar ya sauke ta zata yimay bayani. Sakinta yayi sai gata dagwash a kasan tiles ɗin dakin tari ta shiga yi tana rike wuyanta har saida numfashin ta ya ɗan dawo daidai. Cikin muryan daya jigata ta soma d fadin.

"Wllh ³ Dani aka daura maka aure ta hanyar sanja sunan meerah da Mommah tasa akayi a masallacin! Babu wanda yasan yanda akayi sai a wurin fadar sunan amarya kowa yaji bada meerah aka daura maba tunda Mommah ta rantse dama tace Wllh wannan auren naka da meerah ba a isa anyi saba sai idan bata numfashi, shine ta rufe bakin kowa har aka daura auren babu wand ya lura daba daidai aka daura ba Ata danginmu sai daga dangin amaryar ne suka farga, dama daurin auren biyune a lokaci guda Shine shine shineeeee.....

Kasa ƙara sawa tayi sakamakon uwar shaƙar da Salman ya mata, cikin huci da tafarfasar zuciya ya ke faɗin.

"Wllh yau saina kashe ki a wurin nan kafin naje ka uwar taki dama duk wani shegen daya wuce gaba wajen tarwatsa min farin ciki na, Wllh saina nuna muku kalar zallar haukar dana iya. Saina nuna muku Ni rikakken Mahaukacine inda akan meerah ne, saina tada hankalin kowa kafin naga shegen madaurin auren da idonsa baya gani na karasa lalata masa shi ta hanyar kwakule sa tunda baya da wani amfani"

Numfashin tane ya fara seezing amma duk da haka cikin karfin hali take faɗin ya tsaya ta karasa faɗa mar komai amma ina Salman yayi riga da yayi nisan da baya jin kira, domin baya cikin duniyar mutane ya tafiyar sa irin tasu duniyar ta zararru.

"Zaki faɗamin ina meerah take ne kai tsaye ko sai na karasa kashe ki na bisne gawarki a cikin wannan ɗakin?"

Cikin muryan da ko fita bayayi sosae ta shiga faɗin

"Tana wata duniyar ta daban! Ta maka nisan dako hange daga nesa ba zaka iya mata dan an riga an daura mata aure d dh daaaaa.....

sai kuma ta tafi gaba daya luuuuuuu tana zubewa a jikinsa yarabbbbb..

★_ALHAMDULILLAH ALHAMDULILLAH ALHAMDULILLAH □ □!!! Anan zamu dakata a book One na wannan littafi mai suna MIKIYA sai kuma Allah ya haɗamu da masu rabo a book two_

★Tofa masu karatu yaya take ne?.

★Mike shirin faruwa?.

★Ina Meerah amarya?.

★Mi kalaman sury suke nufi?

★Shin da waye aka ɗaura wa meerah aure?

★Waye AK?

★Miye haɗin Nigeria da kuma KUWAIT ?

★Tofa wata daban su waye KAMAAL da kuwa MARRIYERTOU?

★Magana fa ake ta an kawo amarya meerah ta rikiɗe ta koma sury. Taya taya ya hakan ta faru?

★ANNE ZATA SAN ASALINTA?

★SHIN MIYA KAWO MADINAH?

★Hhhhh masu karatu akwaifa gurmi. Gurmi gagarumi ma kuwa na musamman. Dan littafin nan ɗauke yake da nasa salon shima. Hargitsi da cakwakiyar dake cikinsa kuwa. Hhhhumm ba'a magana, dan bama mu fara komai ba sai a book 2 bamu ko tsoma kafa ba a cikin masarautar Kuwait ko nace EMAAR's

★Kai kar dai na cikaku da surutu ku shirya kawai tsaff domin warware muku zare da abawar dake cakude cikin wannan littafin

Duk zamu samu amsoshin wad'annan tambaya idan mun shiga book 2 da yardar Allah. Nan muka kawo k'arshen BOOK 1 NA MIKIYA Wanda basu biya ba su hanzarta don kar ayi tafiyar babu su littafin MIKIYA Naira 500 ne kacal babu yawa

Ga duk mai son biya zai tuntub'eni a wannan number

08104493215

Wanda suke sun biya zasu turo kuɗin su cikin wannan asusun bankin

3206656358

Maryam Nasiru

First Bank

A turo shedar biya ta wannan number

08104493215

*_Kardai ku manta this one ma is not for free zaku Antayo darinku biyar ta Asusun banki na 3206656358 Maryam Nasiru first Bank ko katin mtn ta wannan number 08104493215 vip suma is 700 kamar yanda kuka sani masoya I no kuna bani goyon baya fiye da yanda nake tunani don haka ina ma kowa fatan Alkhairi don haka kar ku tsaya jiran ayi posting a sato muku na BABA NA BATI ku Antayo kuɗin ku karanta Cikin farin ciki da salama yanda kuke so sai najiku masoya karku sake ayi tafiyar PART 2 na MIKIYA BA TARE DAKE BA HAJIYATA by AMMEY'N LAYLERH'NKU me ƙAUNAR KU FAKA FAKA_*

*Byeeeeeeeee my Re@l f@ns sai mun sake haduwa a cikin PART 2 gamai Rabo. Dan koda kuɗinka Saida rabonka littafin MIKIYA ba hhhhhhhhhhh To ai shikenan sai a gimtse koooo? Ko zamu dana rihazal ne na littafin SANYI YA HAIFI WUTA _PRINCE SAPWAN_ kenan ba hhhhhhhhh

A gimtse kawai baaaaa.